[2/5, 8:11 AM] MOM MASHKUR & AFRAH: *BONONO*

(RUFIN ƘOFA DA ƁARAWO)

NA

MAMAN AFRAH

First Class Writer's Asso.📝

*SADAUKAR*

Daga farko har ƙarshe sadaukarwa ne ga MARYAM HAFIZ (Merry tah) Alkairin Allah ya kai gare ki Allah lulluɓe rayuwar ki da tarin ni,imomi da albarkatu Allah raya mana Abdallah fatan alkairi.

Daga marubuciyar:

Ruɓaɓɓiyar igiya
Ƴan adaidaita sahu
Ungozoma
Ƴar zaman wanka
Da sauran su.

PAGE 1

Da tsananin murna da farin ciki nake hango shi jingine da motar da ya zo ɗaukana saboda a yau ne muka kammala karatun mu na secondry school da yake boarding school nake yi. Sai dai ina jin mummunar faɗuwar gaban da take neman ta kawo mini cikas, a gabaɗaya tarin kalaman da na yi ta shiryawa zan yi amfani da su wajen tona masa asirin zuciyata, ina tunkarar sa bugun zuciyata yana tsanan ta. Duk da ina jin tsoro da fargaba a kan hakan amma dai na shirya tunkarar komai don na mallakawa zuciyata wanda take da buri, kuma shi ne dai wanda ta daɗe tana dakon soyayyar sa haka kuma tun zuciyata tana jaririya na raine ta da soyayyar Yaya ABDULHAKEEM sai dai kash!. Ban taɓa furta masa ba.

Yau kwana na yi ina tufka da warwara ina saƙar jaki a kan irin yadda zan furta kalaman tun jiya

da Abba ya faɗa mini a waya cewa Ya ABDUL ɗin ne zai zo ɗauka ta .

"Oyoyo Ya ABDUL" Na ce ina ƙanƙame shi ta baya da yake ya bani baya ne,  ina sakin jakar da na riƙo a hannuna don shi bai ma san na zo wajen ba hankalin sa yana ga waya.

"Oyoyo HEEDAYA" Ya ce yana raba ni da jikin sa idanun sa kafe a kaina.

"Ya ABDUL" Na ce ina jin wani yanayi na yadda ya kira sunan nawa sai in ke ji kamar duk duniya babu wanda yake kiran sunana in ji ya iya faɗa, tare da ba kowane harafi haƙƙin sa sama da Ya ABDUL.

"HEEDAYA an girma an kammala school" Ya faɗa yana riƙo hannuna tare da lakato hancina, idanuna na lumshe kafin na buɗe su tarrr na sauke a kan kyakkyawar fuskarsa da kullum take mini gizo tamkar ranar na fara ganin ta. Hannu na miƙa na ɗauki jakar sakin hannun nawa ya yi

Sai da muka gama saka kayan nawa gabaɗaya a but ina ta masa mitar bai zo ɗaukana da wuri ba, duk yawanci ƙawayena sun tafi, haka dai muka yi sallama da sauran da suka rage wanda ba a zo ɗaukan su ba, na shiga motar muna ɗagawa juna hannu cike da kewa.

Hanya ya nausa motar muka kama tafiya domin zuwa garin namu mai suna Dutse, dama a garin Gumel nake karatu. Tun da ya fara tafiya motar ta yi tsit baka jin komai sai ƙaran A.C tafiya muke yana tuƙi cike da nutsuwa. A hankali na waiga na saci kallon fuskarsa gabana ya yanke ya faɗi ganin tamkar duk shaƙuwata da shi ina jin nauyin furta masa kalmar so. Kasancewar Ya ABDUL ɗan gidan ƙanin mahaifina sannan gidanjen mu sun kasance maƙotan juna. Tun ina ƙarama ta na taso cikin kulawar sa saboda ya kasance mai son yara, zan iya cewa bayan iyayena a duniya babu wanda ya kai Ya ABDUL da Aunty RABEEYA sona da nuna mini kulawa Aunty RABEEYA uban mu ɗaya da ita sai dai kowa da mahaifiyar sa.

"Bakin surutu dai yau ya mutu mus, ko duk kewar rabuwa da ƙawayen ne?" Ya ce yana ɗan waiwayo ni tare da sakar mini murmushi. Ni ma kaina na samu da sakin murmushin amma na yaƙe wanda iyakar sa fatar baki, saboda yadda zuciyata take cike da son furta kalaman da suke nuƙurƙusar ta.

"Ya ABDUL, ina so na yi maka magana" Na faɗa gabana yana faɗuwa. Rage gudun ya yi, tare da ɗan kallona kafin ya mayar da kallon nasa bisa hanya ya ce

"Ina jin ki" Shiru ya biyo baya kalaman sun yi tsauri wajen furtawa, nauyi da kunyar sa nake amma ina gani  wannan ce damar da nake da ita in furta masa daga ni sai shi a yau ba sai gobe ba, saboda na san ƙa'idar Abban mu daga ka gama secondry school yake maka aure gwara in tanadi mijina a hannu kar in je in zauna a gida irin na Aunty RABEEYA.

"Baka mini kayan candy ba" Na samu kaina da furta hakan ba don haka na yi niyyar faɗa ba

sai don na rasa ta inda zan fara ina son gane bakin zaren amma kuma na kasa, nauyi da kunyar sa nake ji.

"HEEDAYA yanzu kayan candyn ne kike faɗa dakyar ai kin san ke ta hannun damana ce, na shirya miki abin da zai faranta miki, kin san na je india lokacin da ya kamata na yi miki abubuwan da za ki rabawa ƙawaye,  jiya na dawo amma na ce ni zan ɗakko HEEDAYANA" Ya faɗa yana sakin murmushin nan da yake narkar da zuciyata. Wani daɗi ya baibaiye mini ruhi a rayuwa ina son ya ce mini HEEDAYAR sa duk da ba da manufar soyayya irin ta aure yake faɗar hakan ba amma hakan yana daɗaɗa raina fiye da tunanin mai tunani. Na sani cewa yana ji da ni kowa ya san hakan a family namu, tun ina mitsitsiya ta wajen sa ne wurin share kuka na shi ne mai lallashi da lallaɓa ni idan ina kuka, wani lokacin ya saɓani a kafaɗar sa har sai na yi bacci sai dai bai san cewa tun wannan ƙaunar da shaƙuwar da na yi da shi daga lokacin da na yi wayo komai ya canja na yi nutso a kogin son sa tamkar dai a rijiya mai gaba dubu da za ta yi wuyar fitowa.

Ta nuna masa farin ciki da jin daɗin furucin sa, amma ba haka aka so ba ƙanin miji ya fi miji kyau!. Har suka shigo garin Dutse tana jin takaicin rashin sanar da shi ƙudurin ta.  Suna shiga get ɗin tangameman gidan nasu  tun kafin ya gama parking ta hango Aunty RABEEYA ta taho da murnar ta, sai dai HEEDAYA tana fitowa ta juya mata baya tare da zunɓuro baki alamar ta yi fushi.

"HEEDAYATA!" Aunty RABEEYA ta furta lokacin da ta ƙaraso ta rungume HEEDAYA amma ta ƙi cewa komai.

"Ya ABDUL wa ya taɓa mini ƴar lele"

"Ba ruwana kun fi kusa" Ya ce yana dariya tare da buɗe but ɗin lokacin har Na'eema, Mubashshar, da Ihsan sun fito domin taryarta.

"Bake ba ce kika ƙi bin Yaya ɗakko ni"

"Ayya sorry kin ji na tashi da ciwon kai ne sannan Ya ABDUL ɗin ne ya sa mu zauna don shirya abubuwan da za a tarɓe ki amma a yi wa Aunty afwa" Ta faɗa tana rausayar da kai gefe. Murmushi ta saki tana rungume Aunty RABEEYA tana jin ƙaunar ƴar uwar tata duk da iyayen su mata basa jituwa kuma basa son ƙaunar nan da take tsakanin ƴaƴan.

Kayan nata suka ɗauka aka nufi cikin gidan kowa yana murna Ya ABDUL bai shiga gidan ba sai ya juya ya tafi gidan su domin zuwa ya watsa ruwa.

Suna shigowa har lokacin hannun ta sarƙe da na Aunty RABEEYA, da Hajiya Baturiya mahaifiyar su Aunty RABEEYA suka fara cin karo ta fito daga part ɗin ta riƙe da plate za ta nufi part ɗin Abba. Tun daga nesa ta fara aikawa da HEEDAYA mummunan kallo na tsantsar tsana. Ita ma ramawa ta yi a fakaice ba tare da ta bari Aunty RABEEYAR ta gani ba don sauran

ƙannen nasu tuni sun riga su yin part ɗin Hajiya Zainab mahaifiyar su HEEDAYA. Amma a fili ganin sun zo dab da juna cikin kissa da nunawa Aunty RABEEYA girmama mahaifiyar ta sai ta ce.

"Momma ina yini" Ko kallo bata ishe ta ba don dama tana zuwa dab da su ta ɗauke kai bayan ta jefawa Aunty RABEEYA tata harara na ganin ta da HEEDAYA.Ɗan jim HEEDAYA ta yi na alhinin abin da Momma ta mata.

"To mene ne na damuwar? Ai in da sabo kin saba da halin gidan mu, ba za su taɓa canjawa ba suna nan a yadda suke sai dai mu tun da Allah ya haɗa kanmu ai ba za su raba mu ba, HEEDAYA babu abin da zai raba ni da ke babu abin da zai kankare ƴan uwantaka ta jini da nake miki ina ƙaunar ki zan iya sadaukar da komai a rayuwa ko mene ne in har zai saka ki farin ciki" Aunty RABEEYA ta faɗa tana sakar mata murmushi kasancewar ta fi ƙaunar HEEDAYA sosai a kan ƙanwar ta Na'eema wacce suke ciki ɗaya.

Sai da ta raka ta har ƙofar falon Hajiya Zainab wacce suke kira da Umma, sannan ta dakata ba don ta so ba za ta juya, riƙe mata hannu ta yi ta ce

"Haba Aunty ya za ki dakata daga nan mu je ki raka ni mana har ɗakina" Ta ce tana zumɓura baki.

"Zan je mu ƙarasa haɗa miki kayan tarɓar da muka shirya miki ni da Yayan ki" Ta faɗa tana kallon ta, ba don ta gamsu ba ta saki hannun ta suna yi wa juna murmushi, Aunty RABEEYA tana juyawa HEEDAYA ta shige falon da gudu cike da murna da farin cikin dawowa gida gabaɗaya, ba da sunan hutu ba don ta tsani boarding school ɗin nan kawai don ba yadda za ta yi ne ta san halin Abban su idan ya ce kulle dole ne mutum ya ce casss ko ba ya so. Su ma su Umma abubuwan da suke yi tsakanin su da na yaran sai a bayan idanun sa ne suke yi a gaban sa sai su dinga kissa da kisisina sai dai ɗan abin da ba a rasa ba.

Da murna suka rungume juna ita da Umma, bayan nan ta zauna suna ta hira ita da Mubashshar da Ihsan. Ɗakin ta ta nufa ta shiga don ta watsa ruwa har ta cire kayan, ta ɗauki towel ta ɗaura za ta shiga banɗakin sai ta nufi jakarta da aka shigo mata da su, ɗaukan jakar ta yi ta fito da hoton Ya ABDUL ta tsaya kallo tana rayawa a ranta.

'Da sannu ba da gajiyawa ba zan sanar da kai sirrin da yake raina, ina son ka ina mugu-mugun kishin ka, zan iya komai a kan ka zan iya fafatawa da kowa a kan ka, babu wata da zan bari ta raɓe ka idan kuwa wata ta yi gigin yin hakan sai na koyar da ita darasin da har ƙarshen rayuwar ta ba za ta manta ba' Ta faɗa tana sakin murmushi tare da shafo hoton ta mayar da shi cikin jakar ta ajiye ta shiga wankan tare da ɗauro alwala ta fito. Shiryawa ta yi ta saka doguwar riga sanna ta yi sallah. Wajen ƙarfe biyar Aunty RABEEYA ta zo part ɗin su riƙe da wata ƙatuwar leda, ko da ta samu Umma a babban falo ta gaishe da ita ko kallon arziƙi bata samu ba bare ta saka ran za ta amsa sai ma nuna mata hanyar waje da ta yi tana cewa

"To baƙar munafuka annamimiya wato ƴata ta dawo za ki fara mini diddibtun munafurci kina nan zaune a gida ke ba karatu ba ke ba auren ba, kin rasa mashinshini ga shi nan har ƙanwar bayanki ta gama karatu ta dawo gida za ku jera har ma ta samu miji ta tashi, to kar ki kuskura ki zo ki goga mata baƙin jini irin naki ta rasa mijin aure ko ki hure mata kunne" Umma ta faɗa cike da bala'i. Ihsan da fitowar ta kenan ta samu wuri ta zauna tana taɓe baki ta ce.

"Umma ni ma da nake zuwa day school yanzu saura shekara biyu na kammala"

"Yo ai sai ku duka ku  tashi kun barta sai dai ko Alhaji ya bada sadakarta don bana jin za ta auru" Kai Aunty RABEEYA ta sunkuyar tana jin ƙunci da raɗaɗin maganganun da take ji tamkar ana watsa mata ruwan dalma a zuciya, duka shekarun nata ashirin da ɗaya ne fa, kawai don dai Abba ba ya bari a cigaba da karatu sai dai mutum ya yi a gidan miji shi ya sa ake ganin hakan amma da karatu take zaman gidan ma ba zai gundure ta ba bare har ake ganin ta kasa samun miji duk da samarin suna ziryar zuwa amma dai daga ta musu maganar aure sai su daina zuwa ita ma bata san mene ne dalili ba sai dai ta san Allah ba ya bacci kuma yana sane da ita. HEEDAYA da take ɗakin ta tana gyara kayanta take jin tashin maganganu a falo hakan ya sa ta fito tana fitowa ta ga Aunty RABEEYA ta juya za ta fita, da sauri ta ƙarasa tana kiran sunan ta tare da riƙo hannun ta, cak ta tsaya sai dai bata juyo ba kuma bata ɗago fuskarta ba sai hawaye da yake tsiyaya.

"Haba Umma kin san dai ai wurina ta zo ko? Ko don ƙaunar da take mini ta cancaci ta samu rangwamen wasu abubuwan daga gare ki" HEEDAYA ta faɗa tana kallon Ummar, tare da juyawa ta shiga aikawa Ihsan saƙon harara.

"To uwata faɗa mini abin da ban sani ba, ke ai wawiya ce don ana nuna miki farin haƙori shi ya sa kike ganin soyayya ce, bayan ta ciki na ciki so take ta gama shiga jikin ki sai ta ida nufinta, in kin manta in tuna miki ƴar kishiyata ce fa, an faɗa miki kishi wasa ne? Ko an faɗa miki ƙiyayyar kishi wasa ce, za su iya duk yadda za su yi su shiga jikin mu kafiin cim ma burin su"

"Haba Umma bai kamata ba wanna abin da kike tun ban kai haka ba take nuna ƙaunarta da kulawar ta gare ni, da a ce tana da wani nufin a ganina da ta daɗe da bayyanawa...

"Ga shi in ji Ya ABDUL sarƙa da ɗankunne da agogon ni na baki, ki shirya ki same mu a gidan Ammie" Aunty RABEEYA ta faɗa cikin muryar kukan da ta kasa dannewa.

"Aikin banza shi ma ABDULHAKEEM ɗin ai munafuki ne, ai wallahi tun da uwar sa ta munafurce ni to babu yarda tsakanina da shi gabaɗayan ku lumbu-lumbu ne wutar ƙaiƙayi bata kama ba ta haɗe wuri da hayaƙi" Umma ta faɗa tana jin zafi da raɗaɗi a zuciyarta kasancewar ta uwar gida, sannan kafin a auro Momma mahaifiyar su RABEEYA wacce ita ce amarya, to Umma bata da ƙawa kuma abokiyar shawara sama da Hajiya Fati wato mahaifiyar ABDUL kamar ba facaloli ba haka kan su yake a haɗe, amma daga bisani da aka auro Momma suka yi

wani rikici da Ammien da Umma shikenan sai alaƙa ta ɗinke tsakanin Ammie da Momma aka dawo ana zaman doya da manja da Umma da Ammien wannan dalilin ne ya sa Umma ta tsani ABDUL gabaɗaya bare kuma RABEEYA da dama kishin da yake tsakanin iyayen yake tasiri har kan ƴaƴan su.

Kowa ya tsani ɗan kowa, basa duba zama ya haɗa, ƴaƴa sun girma babu wacce za ta fitar da kowacce amma kullum kishi yana nuƙurƙusar su sun kasa ba zuciyar su haƙuri su yi zama cikin salama da aminci.

Aunty RABEEYA bata jira cewar HEEDAYA ba ta damƙa mata ledar ta juya da sauri jin kuka mai sauti yana neman ƙwace mata. HEEDAYA rasa bakin magana ta yi ta juya fuuuu fa tafi ɗakin ta. Duk da tana jin abin da aka yi wa Aunty RABEEYA har ƙasan ranta amma jin wani sassanyan daddaɗan turare mai narkar da zuciya ya ziyarci hancin ta gabaɗaya sai ta shagala da son ganin turaren tun da dai in aka ɗauke sarƙa da ɗankunne da agogo sauran duk Ya ABDUL ne ya bata kenan turaren nan daga gare shi ne.

Wasu turaruka ne guda uku masu bala'in ƙamshi sannan daga ganin su masu tsada ne, sai wani leshi da aka yi wa riga da skirt ɗinkin ya tsaru daidai jikin ta da mayafin su, sai takalmi sai kwalin waya iphone 16 sai kuma sarƙa da ɗankunnen da agogon wanda Aunty RABEEYA ta bata. Daɗi ya cika mata zuciya a duniya in akwai kyautar da ta fi so ita ce ta Ya ABDUL sai kuma ta masoyiyar ta Aunty RABEEYA.

A gaggauce ta shirya, kayan sun yi matuƙar karɓar ta, wayar ta jona a caji bayan ta mayar da sim ɗin ta na cikin wayarta da take amfani da ita idan ta zo hutu. Fitowa ta yi tana buɗaɗa ƙamshi, lokacin da ta fito babu kowa a falon sai TV tana aikin ta. Duk can ta samu sauran ƴan uwan nata har da Ya ABDUL da ya shirya shi ma ya yi matuƙar kyan da ya sa ta shagala da kallon sa, bata ba kanta wahala wajen shiga gaishe da Ammie ba don ta san ko ta je ma dakyar ta amsa. Ƙwarya-ƙwaryar fatin da aka shirya mata na kammala karatun wanda ya faranta ranta matuƙa, har da ƙaton cake aka mata mai ɗauke da sunan ta a jiki wannan duk aikin Ya ABDUL da Aunty RABEEYA ne .

Sai da aka kira magriba suka tashi, an ci an sha an yi hotuna, gida suka dawo ɗakin ta ta shige bayan ta gabatar da sallaha ta kwanta tare da kunna wayar. Ta fara danne-danne sai ta jiyo muryar Umma tana ƙwala mata kira. Fitowa ta yi ta same ta a falo ita kaɗai ce.

"HEEDAYA" Umma ta kira sunan ta amsawa ta yi tana mayar da hankali kan Ummar.

"Ina fata kin fitar wanda kike so, kin san dai halin Abban ku ni bana son duk abin da zai zama matsala kuma bana son ki bar mini abin gori daga kishiya da facala. Ina so cikin wanda suke neman ki, ki tabbatar kin samu wanda za ki faɗawa Abban ku a matsayin abokin rayuwar ki idan an tambaye ki, bana so a ce kin zauna a gida na fi so kamar yadda dokar sa take daga an gama secondry a yi aure ina fatan ba za ki bani kunya ba" Murmushi HEEDAYA ta yi tana jin

daɗin hirar nan dama ta daɗe tana son faɗawa Umma muradin ta amma sanin tsakanin ta da Ammie ya sa take ta dakon son a ranta amma dai yanzu za ta yi ƙarfin hali ta tari aradu da ka, ta faɗa mata zaɓin ta in ya so ko mai za faru ta shiryawa hakan in ya so sai ta tunkari Ya ABDUL ɗin da hujja tun da dai ta san ba zai taɓa maido mata da ƙoƙon barar tayin soyayyar ta ba, kuma duk runtsi ta shiryawa kowane ƙalubale domin cikar burin ta na auren sa.

"Umma ina da wanda nake so, na daɗe da zaɓar sa a matsayin abokin rayuwata kuma uban ƴaƴana" Wani murmushi Umma ta saki tare da dafa kafaɗar HEEDAYA ta ce.

"Dama ni na san ba a rasa nono a ruga,  tabbas! Na san da cewa ba za ki taɓa rasa mai auren ki ba, ai ke ta daban ce babu mu babu barin abin gori a dangi na yin kwantai, shin wane ne shi? Ɗan gidan waye?"

"Umma ba shi ya ce yana sona ba, bai taɓa sanin ina son sa ba sai dai na san ba zai guje ni ba duk runtsi" Galala Umma take kallon ta jin kalaman  da suka raunata ƙarfin gwiwar da take ji na samun mijin da ƴarta ta yi sai dai shin wace irin mgana ce wannan.

"Kina da hankali HEEDAYA wanda bai san da matsayin son da kike masa bane za ki fitar a matsayin mijin aure!? Yanzu a ɗan lokacin nan soyayyar sa za ki nema ko fitar da shi ga Abban ku a matsayin miji? Kin san Abban ku dai ba zai saurara miki ba ko? Wai waye ma?" Ta faɗa cikin hargowa.

"Umma neman soyayyar sa ba zai mini wahala ba ni na sani"

"Saboda zuciyar sa a hannun ki take ko?"

"Ba haka bane, amma ina da yaƙinin hakan, sannan ba ɓoyayye bane makusanci ne makusanci na a alaƙa makusanci a zuciyata"

"Tambayar ki nake waye so nake in san waye?"

"Ya ABDULHAKEEM" Ta furta muryarta tana rawa don ta san ta taro aradu da ka, ta ɗakko dala ba gammu tabbas akwai sarƙaƙiya, cakwakiya da babban ƙalubale a wannan muradin nata. Wani irin hangaza kafaɗar ta Umma ta yi kafin cikin sauri ta miƙe tsaye har zanin ta yana neman faɗuwa saboda yadda maganar ta duke ta a ƙirji, yadda ta ji sunan a bazata bata taɓa zaton HEEDAYA mahaukaciya ce ta ajin ƙarshe ba sai yau! Ɗan gidan facalar ta? Wanda a yanzu bata da maƙiyar da take da ita sama da ita, wacce suke zama tamkar wuta da ruwa da basa haɗuwa wuri guda, bayan sun zama abokan gaba, wanda take jin daga ABDUL har mahaifiyar sa tamkar ta kawar da su daga doron duniya amma shi ƴarta za ta zaɓa a matsayin miji?.

Ya kuka ji labarin? Kun karɓe shi? Mai kuka hasaso zai faru a gaba? Kun gane ruguntsumin da muka kawo kanmu? Ba wannan ne ainihin makamar zaren ba, wannan shi ne wasa farin girki a cikin labarin shi ne somin taɓi sai dai a gaba za mu gano mene ne dalilin ambaton labarin da suna *BONONO RUFIN ƘOFA DA ƁARAWO* waye ɓarawon? Waye bononon? Wa aka rufe? Waye ya rufe amsoshin suna gaba sai dai ba zan baku kunya ba in sha Allah.

MAMAN AFRAH
09013181851
[2/6, 2:08 PM] MOM MASHKUR & AFRAH:
https://chat.whatsapp.com/F7TUZezpOWLKYnyTNFuy2Y

BONONO

(RUFIN ƘOFA DA ƁARAWO)

NA

MAMAN AFRAH

First Class Writer's Asso.📝

*SADAUKAR*

Daga farko har ƙarshe sadaukarwa ne ga MARYAM SANI HAFIZ (Merry tah) Alkairin Allah ya kai gare ki Allah lulluɓe rayuwar ki da tarin ni,imomi da albarkatu Allah raya mana Abdallah fatan alkairi.

Daga marubuciyar:

Ruɓaɓɓiyar igiya
Ƴan adaidaita sahu
Ungozoma
Ƴar zaman wanka
Ƙara'in inna delu
Beelal
Jalli joga
Da sauran su.

*09013181851*

PAGE 2

"HEEDAYA ashe mahauciya ce ke?Ashe ƙwaƙwalwar ki bata aiki? Shin notinan kan ki ne suka sunce ko yaya? ABDULHAKEEM ne kike so har kike muradin aure? Kin manta irin murɗaɗɗiyar gabar da take wanzuwa a tsakanin mu da uwar sa yanzu? Hatta maganar fatar baki bata haɗa mu da ita, ko hanya muka haɗa kin sani tamkar bamu taɓa sanin juna ba ko da gidan nan ta zo iskar da ta bi hanyar part ɗina ma bata kallo sai dai ta je wajen Hajiya Baturiya, shi ne kike so ki ja mini abin kunya da gori ki sa suke yada mini magana suke mini bita da ƙulli dukan kabarin kishiya, to ahir ɗin ki na yarda ki so ko wane namiji a doron duniya kuma zan tsaye miki tsayin daka in ga kin mallake shi amma ban da ABDULHAKEEM ko soyayyar ƴan uwantakar da kike masa na tsane ta bare soyayya ta aure da haɗa zuri'a har abada!" Umma ta kai ƙarshen maganar tana haki tamkar wacce ta yi tseren gudu.

"Ba zan iya ba Umma na riga na afka sai dai auren sa ne kaɗai mafit... Tun kan ta ƙarashe maganar da ta fara Umma ta ɗauke fuskarta da wani gigitaccen marin da sai da kunnuwan ta suka yi dummm.

"Idan kika ƙara furta kalmar soyayyar ABDULHAKEEM a wurin nan sai na tsine miki HEEDAYA" Ta faɗa tana huci tare da nuna ta da yatsa.

Ƙasa ta zamo daga kan kujerar har lokacin hannunta dafe da kuncin ta da ya sha marin, hawaye suna kwaranyo mata wanda bata jin za ta samu salamar zubar su matuƙar ba Umma ta amince da zaɓin ranta ba. A kan gwiwoyinta ta dira tare da sunkuyar da kanta ta ce

"Ki yi haƙuri Umma, ki mini afuwa please amma ba zan gushe ba ina furta kalmar so ga Ya ABDUL ba har sai ranar da na bar lumfashi a doron duniya" Tana kai wa nan ta miƙe cikin kuka da ɗan gudu za ta tafi ɗakin ta. Taku ɗaya biyu Umma ta yi ta damƙo wuyan rigarta ƙiiii ta janyo ta bata mata masauki a ko ina ba sai a gabanta.

"Baki ji lokacin da na ce miki zan tsine miki ba?" Ta tambaya tana aika mata harara cikin zare idanu.

" Ai na ce ki mini afuwa!, saboda numfashina sarƙe yake da linzamin ƙaunar sa ba zan iya ba Umma, ba zan iya daina son sa ba in kika raba ni da shi zan kasance cikin ƙunci da mummunan tashin hankali har abada!" Ta faɗa tana rushewa da kuka.

"To ko za kike mutuwa kina falkowa ba za ki taɓa auren ABDULHAKEEM ba!." Umma ta faɗa tana sakin wuyar rigar HEEDAYA tare da kama hanyar ɗakin ta fuuuu tamkar za ta tashi sama

domin yau HEEDAYA ta caje mata kai ta ɓata mata rai sai dai ba za ta taɓa raunata a kan wannan maganar ba tabbas ba za ta kasance cikin mutanen da ake ce musu ɗan kuka shi yake jawa uwar sa jifa ba!.

Bata samu zarafin tafiya ɗakin ta ba a wajen ta durƙushe tare da sakin wani marayan kuka zuciyar ta tana raya mata ta tashi ta tafi gidan su Ya ABDUL ɗin ta furta masa abin da yake ranta, ko shi zai iya yin wani ƙoƙari wajen ganin ba a daƙushe wannan maganar ba. Har ta karɓi shawarar zuciyar ta tana shirin tashi sai ta ji muryar Na'eema tana sallama a ƙofar falon. Da sauri ta share hawayen ta, amsa mata ta yi.

"Abba ya ce yana kiran kowa da kowa" Tana faɗar haka ta juya ta fice. Cikin sanyin jiki ta shiga ɗakin Umma da sallama tsaye ta same ta a ɗakin tana gewaya ɗakin tamkar wacce take wurin dutsen safa da marwa da alama dai maganar da ta faɗa mata ce take ci mata tuwo a ƙwarya.

"Abba ya aiko yana kiran kowa da kowa" Ta faɗa cikin sanyin murya tare da juyawa za ta fita ganin ba amsa mata Umma za ta yi ba.

"Idan har ya kasance taron da ya kira ya shafe ki ma'ana domin ki aka yi, wallahi idan kika yi gigin buɗe wannan bakin naki kika furta cewa ABDULHAKEEM kike so sai dai ki nemi wata uwar ba ni ba" Bata furta ko ƙala ba ta juya ya fito daga ɗakin amma a ranta tana raya muddin Abba ya tambaye ta wa take so to sai dai Umma ta yi haƙuri, amma bata da wanda za ta furta sama da Ya ABDUL. Ihsan ta kira da Mubashshar ta shige ɗakin ta a maimakon ta tafi part ɗin Abba. Wayar ta ta ɗakko ta kamo sunan Ya ABDUL ta shiga doka masa kira da zummar ta fara sanar masa a waya kar ta je sai ta faɗawa Abba ya kira shi ya tamabaye shi kuma a samu akasin lissafi, ya ce bai san da maganar ba. Amma ta san muddin ta faɗa masa to ba zai yi ƙasa a gwiwa ba daga an tambaye shi zai aminta da hakan saboda ta san ba zai taɓa ƙin ta ba. Tana kara wayar a kunne ta ji ana sanar da ita wayar a kashe, wata nannauyar ajiyar zuciya ta sauke tare da ajiye wayar ta taso ta fito tana rayawa a ranta muddin Abba ya nemi sanin wa take so wa ta zaɓa a matsayin miji to za ta faɗa masa gaskiyar abin da yake ranta sai dai ko a mutu ko a yi rai.

Tun da ta nufi part ɗin Abba bata ci karo da kowa ba, da alama duk an hallara ita kaɗai ake jira. Ita dama Abban ma tun lokacin da za ta tafi gidan su Ya ABDUL wajen partyn da aka shirya mata, kafin ta tafi ta shiga ta gaishe shi bata ƙara sanya shi a idanun ta ba. Tsit kake ji falon baka jin maganar kowa tamkar babu kowa a ciki sai ƙaran A.C kawai don ko TVn tana yi amma an cire volume gabaɗaya. Da sallama ta shiga falon, baki ta ji an haɗa wajen amsa mata, gaban Abba ta je ta durƙusa ta gaishe da shi, kanta a sunkuye har ta samu waje ta zauna a ƙasan cafet kusa da Aunty RABEEYA, da yake gabaɗaya yara a ƙasa suke zama manya ne kawai a kujera. Aunty Hafsa ita ce babba a gidan, daga ita sai Aunty RABEEYA sannan HEEDAYA sai Na'eema sannan Ihsan sai Mubashshar. Aunty Hafsa, HEEDAYA, Ihsan, Mubashshar su ne ƴaƴan Umma Aunty RABEEYA da Na'eema su ne ƴaƴan Momma.

Tun da ta zauna kanta a sunkuye yake tun shigowar ta da ta haɗa ido da Umma ta aika mata wani kallo mai alamar gargaɗi, sai kuma bayan ta zauna Aunty RABEEYA ta jefa mata murmushi sai dai bata samu damar mayar da martani ba, saboda fargabar da take ciki.

Gyaran muryar da Abba ya yi tare yake ya tafi da bugun zuciyar ta sai dai tana ta addu'a a zuciyar ta.

"Ba komai bane ya sa na tara ku a nan sai don magana mai muhimmanci, amma kafin wannan maganar ina so in fara ba RABEEYA dama domin jin daga bakin ta, saboda sanin kan kowa ne maganata tamkar yankan wuƙa take sannan bata da bambanci da rubutu a kan dutse wanda ba ya goguwa!" Ya ce yana ɗago kai ya sauke a kan Aunty RABEEYA da gaban ta ya yi mummunar faɗuwa, don dama ta riga da ta sanya a ranta cewa taron nan don ita aka yi shi. Babu wanda ya ce uffan sai Abba ya ɗora da cewa.

"RABEEYA kin samu wanda za ki bayyana a wajen nan matsayin mijin aure?"

Wani miskilin murmushi Umma ta saki a ɓoye wanda Momma ce kaɗai ta gani kuma dama ta yi domin ta ne, saboda ta san dai maganar samun mijin RABEEYA akwai ya babu ne kakar wajen uba. Wani tuƙuƙin baƙin ciki ne ya tokare a maƙoshin Momma jin furucin Abba da kuma murmushin da Umma ta mata wanda ta san baya rasa nasaba da murmushin ƙeta. Da sauri Momma ta ɗauke idanun ta tana kallon cafet ɗin da yake malale a tsakiyar falon.

"Abba ban samu ba, wanda suke zuwa kowa na tunkara da maganar aure sai ya daina zuwa" Ta ce muryar ta tana rawa don idan akwai abin da ta tsana a duniya a zo tambayar ta mijin aure sai take ganin kamar ita ta fi kowa baƙin jini.

"To shikenan RABEEYA dama na baki damar hakan ne kar in zartar da hukunci sanin kan kowa ne bana yin auren dole, amma tun da dai baki fitar ba ni zan zaɓa miki ko ma in ce na zaɓa miki don shi ne maƙasudin zaman mu a nan yanzu" Kai ta sunkuyar hawaye yana malala mata a kumatu tana kallon yadda suke ɗisa a kan cafet. Umma kuwa tamkar ta tashi ta taka rawa haka ta ji tsabar murna da farin ciki jin za a yi wa ƴar kishiyar ta auren dole.

"Abokin ka ne Alhaji?" Umma da ta so ƙara ƙonawa Momma rai ta faɗa.

"Na baki damar magana ne? " Ɗif ta yi tun da burinta ya cika dama so take ta yi tambar domin ta sosa ran Hajiya Baturiya.

'Na shige su wannan yarinya za ta bar mini abin faɗa wato yanzu wataƙila ma tsoho ne ya zaɓa mata' Momma ta faɗa a zuciyar ta. HEEDAYA duk da halin da take ciki amma sai ta ji tausayin Aunty RABEEYA duk da cewa ta ji daɗin jin cewa taron ba don ita aka shirya ba wataƙila sai

nan gaba za a kira nata taron.

"RABEEYA na zaɓa miki Yayan ki ABDULHAKEEM a matsayin mijin da za ki aura ki rayu da shi!." In ka ɗauke Na'eema, Abba, Ihsan , Mubashshar sai da kowa ƙirjin sa ya buga da ƙarfi musamman HEEDAYA da ji da ganinta suka mata ƙaura na wasu daƙiƙai. Ita kanta bata san lokacin da ta tashi tsaye ba amma cikin ƙarfin hali ta koma ta zauna tana jin zuciyarta tana zillo tamkar za ta hudo ƙarjin ta ta fito waje. Momma wani sanyi ne ta ratsa zuciyarta ko ba komai ƴarta ba tsoho za ta aura ba, sannan kuma ɗan gidan aminiyarta Hajiya Fati bugu da ƙari kyakyawan matashi mai cikar haiba da kamala ya haɗa komai da wuya a samu macen da za ta ƙi shi. Umma kuwa ranta ne ya sosu tare da mugun ɓaci tana ganin ma kamar da gangan aka mata haka ko dai ana son mata bita da ƙulli dukan kabarin kishiya ne tabbas!. Ta san ruwa ba ya tsami banza wato haɗa baki aka yi don zumuncin Hajiya Fati da Hajiya Baturiya ya ƙara ƙarfafa su ƙara jin daɗin nuna mata wariyar launin fata.

Aunty RABEEYA kuwa sai ta rasa a wane yanayi take farin ciki ko saɓanin haka? Ta tabbata idan har ta ce ba za ta ƙaunaci ɗan uwanta da aure ba tabbas ƙarya take!. Ya ABDUL ba za ta taɓa ƙin sa ba nagartaccen namiji ne da ya haɗa komai na nagartar miji na gari, sai dai shi ɗin zai karɓe ta a matsayin mata? Zai yarda ya aure ta? Zai kyautata mata har ta samu farin ciki a cikin gidan sa? Shin ba zai goranta mata ba cewa ta rasa miji taimakon ta ya yi ya aure ta?. Waɗannan cukurkuɗaɗɗun kalmomin su ne suke kai kawo a birnin zuciyarta. A hankali ta ɗago idanun ta, ɓangaren da mahaifiyar ta take zaune don gano yadda ta ɗauki maganar ai sai ta ga fuskar Momma ganin ta sakar mata wani murmushin farin ciki da jin daɗi sai ta ji wani sanyi a ranta tare da jin ƙwarin gwiwa. Ganin Umma ta doka mata wata harara da kallon tsana da sauri ta ɗauke fuskar ta ƴar uwar ta Na'eema ta kalla ta ga tana wani rausaya kai alamar jin daɗin furucin Abba.

"Na amince Abba!." Ta furta muryar ta tana rawa gabanta yana tsananta bugu. Duk da ta san amincewa da rashin amince wa abu guda ne a wajen Abba domin ta san yadda ya faɗa ba zai sauya ba, amma ta faɗa masa ne don bai kamata ta yi shiru ba shirun tamkar wofantar da maganar ne a ganin ta.

Kallon fuskar tauraruwar ta masoyiyar ta HEEDAYA ta yi a nan ta ga abin da bata yi zato ba abin da ya saka ta a ruɗani wato ganin hawaye suna ƴar tseren fitowa daga idanun HEEDAYA. Mamaki da al'ajabi ne suka dirar mata a lokaci guda.

'Mai ya sa HEEDAYA kuka? Ko zaton ta ba zan amince da Ya ABDUL ɗin ba shi ya sa take zubar da hawayen tausayin za a mini aure da wanda ba na so?' Ta tambayi kanta a zuciyar ta tana miƙa hannu a hankali ta kamo hannun HEEDAYA saboda yadda take jin zubar hawayen HEEDAYA har ƙasan ranta, amma wanda ya ga kama hannun HEEDAYA da ta yi shi ya ga janyewar HEEDAYA sosai abin ya taɓa mata zuciya har bata san yadda za ta fasalta abun ba.

Sai dai hasashen ta bai taɓa bata cewa HEEDAYA son Ya ABDUL ɗin take ba, da son shi take ta tabbatar da ita wacce za ta fara sani ita dai kokwanton da ta shiga ya yi yawa har ta fara tunanin ko dai Umma ta zaunar da HEEDAYA ne ta mata kuɗuba a kan ta daina kulata.

"Allah ya miki albarka Allah kuma ya sa abokin rayuwa na arziƙi ne wanda sai mutuwa ce za ta raba ku, mun yanke hukunci ni da mahaifin sa a kan cewa nan da sati huɗu masu zuwa za a ɗaura aure!" Cewar Abba.

"Allah ya tabbatar da alkairi Allah sa abokan junan arziƙi ne" Momma ta faɗa kai kana jin muryarta ka san tana cike da shauƙi da farin ciki. Ido Abba ya tsare Umma da shi dakyar ta daure ta ce

"Allah sa alheri" Ta faɗa tana jin ɗaci a zuciyar ta. Yanzu kam ta san shikenan ruwa ya ƙarewa ɗan kada, gutsiri tsoma sai inda mai ya ƙare shiga motar mahaukaci, yanzu ne za su ƙara haɗe mata kai, ita ba ta ƴar ta take yi ba ma da ta soyayyar ABDUL ɗin a zuciyarta ta tunanin yadda zumunci zai cigaba tsakanin kishiyarta da facalar ta, tabbas ta yi da na sani a kan yadda ta ɗauki Hajiya Fati a baya amma yanzu ta koya mata hankali da yi mata karatun ta nutsu.

Dining aka koma aka fara cin abincin dare, HEEDAYA ta zauna ne kawai tana wasa da cokali a plate ɗin ta saboda ko loma ba za ta iya kai wa bakin ta ba. Aunty RABEEYA yanayin da ta shiga na hukuncin da aka yanke a kanta ya sa ta kasa cin komai musamman ma da ta ga HEEDAYA cikin wata iriyar damuwa, bare dama dukan su ba yunwa suke ji ba saboda ɗan ciye-ciyen da suka yi wajen partyn HEEDAYA. Hajiya Baturiya har wani ƙwasƙwas take da cokali in za ta ɗauki abincin duk don ta ƙonawa Umma rai.

Abba ne ya yi wa Mubashshar umarnin ya je ya ɗauro alwala su tafi masallaci, don shekarar sa goma Mubashshar ɗin. Sauran kuma suka taso suka fito Momma ce riƙe da hannun Aunty RABEEYA tana wani nuna murna a fili.

"Ka ga amaryar ɗana ABDULHAKEEM abin mu tuwona maina ni da aminiyata Hajiya Fati" Ta ce tana yi wa Umma wani kallo ta wutsiyar ido Umma kuwa fuuuu ta fice su har tana neman faɗuwa. HEEDAYA da ta fito tana haɗa hanya tsabar ɓacin rai ta zo ta wuce ta gaban su tana jin Aunty RABEEYA tana kiran ta amma ko kallo bata ishe ta ba bare ta saka ran za ta amsa mata.

Ko da ta zo falon bata ga Umma ba hakan ya sa ta shige ɗakin ta tana zuwa ta kwanta rubda ciki tare da fashewa da wani matsanancin kuka. Kukan take ko za ta ji sasaauci da salama, amma tamkar ana ingiza son Ya ABDUL a zuciyarta sannan a yau ɗaya tak ta ji ta tsani Aunty RABEEYA .Karan wayar ta ne ya katsr mata kukan da take yi amma bata kawo wayar a ka ba, don yanzu ba ta wayar ba take, amma jin kiran daga ya katse yake ƙara shigowa sai ta

tashi fuskar sharɓar da hawaye ta ɗakko wayar sunan Ya ABDUL da yake reto a kan screen ɗin wayar ne ya sa zuciyarta mummunar bugawa.

Ya ABDUL kuwa bai san wainar da ake toyawa ba, bai san Abba sun yi magana da Daddyn sa ba bare ya san har sun yanke hukunci uwa uba kuma har ya san Abba ya sanar da Aunty RABEEYA za a haɗa su aure. Yau kawai ya ji a ransa ya dace ya je wa Aunty RABEEYA da maganar soyayya a raɗin kansa don bai ga wata makusa ko naƙasu da aibu ba da za ta kasa auruwa har ake matsa mata ta fitar da miji. Tun da ga shi ya gama karatun sa har yana aiki a asibitin sa ya kamata kawai kowa ya ji bazata cewa shi ne zai auri Aunty RABEEYA sai dai yana fatan ta karɓe shi da hannu biyu shi ne ya yanke shawarar kiran HEEDAYA domin ta raka shi ya miƙa ƙoƙon barar sa duk da kasancewar Yaya a wurin ta amma babu raini a tsakani. Ya san HEEDAYA za ta fi kowa farin ciki. Sai da ya shirya tsaf yana buɗaɗa ƙamshi shi ne ya shiga kiran wayar HEEDAYAR ganin shiru bata ɗauka ba shi kuma ya ƙudurta a ransa cewa ba zai wuce yau ba sai ya sanar mata, hakan ya sa ya kira Aunty RABEEYA da take kwance a doguwar kujera a falo gabaɗaya hankalin ta yana kan HEEDAYA da ta yi fushi kuma babbar damuwar ta bata san mene ne dalilin fushin ba, ga Momma ta dame ta da maganar shirye-shiryen biki. Kiran da ya shigo wayarta ne ya dawo da ita hayyacin ta daga nutson da ta yi a kogin tunani. Ganin sunan Ya ABDUL har sai da numfashin ta ya yi barazanar kufce mata saboda yadda ta tsorata kiran ya zo mata a bazata, tunani barkatai suka cushe mata ƙwaƙwalwa a kan ko ya kira ta ne ya kora mata gargaɗi.

Kasa ɗagawa ta yi har sai da ta tsinke wani kiran ya shigo, Ya ABDUL kuwa har ya fitar da ran za ta ɗauka sai kuma ya ga ta ɗauka. Aunty RABEEYA wayar ta kai kunnen ta hannunta yana karkarwa tana jiran jin abin da zai faɗa mata. Wata nannauyar ajiyar zuciya ya sauke wanda har sai da ita kanta ta ji ƙaran saukar ajiyar zuciyar.

"Ganin nan zuwa in same ki a falon baƙi" Haka kawai ya ce cikin bada umarni ya kashe wayar. Duk da bata gama tantance dalilin zuwan nasa ba amma a ƙalla ta ji sanyi da rangwame don ta ɗauka da faɗa zai balbale ta.

"Ina za ki je?" Momma ta jefa mata tambayar.

"Ya ABDUL ne yake kirana" Ta faɗa cikin sanyin murya. Wani murmushi Momma ta yi bata ce komai ba. Jikin ta sanyi ƙalau ta nufi falon, ko da ta je shiga kawai ta yi ta zauna da yake ma falon hanyar get yake zamanta ke da wuya ko minti uku ƙwarara bata yi ba ya shigo da sallama. Kanta a sunkuye har ya shigo ya yi wa kansa masauki a kujerar da take dab da tata.

HEEDAYA kuwa tana ta ƙoƙarin haɗa kalmomin da za ta yi amfani da su wajen sanar masa damuwarta har kiran ya yanke wayar ta ajiye zuwa can ta ƙara ɗakkowa ta bi kiran lokacin yana falon baƙin tare da Aunty RABEEYA kiran nata ya shigo.

"Hlo Ya ABDUL"

" Gani a gidan ki zo ina falon baƙi akwai magana mai muhimmanci" Haka kawai ya ce ya kashe wayar. Bata san ta aka yi ta tashi ba amma dai ta ganta a tsaye ƙiƙam ko wayar bata ɗauka ba ta fito gabanta yana faɗuwa ta nufi falon baƙin tana rayawa a ranta wataƙila ya zo ya ce yana son ta ne, ya zo ya furta mata kalmar so ne...

MAMAN AFRAH

09013181851

[2/6, 10:12 PM] MOM MASHKUR & AFRAH: BONONO

(RUFIN ƘOFA DA ƁARAWO)

NA

MAMAN AFRAH

First Class Writer's Asso.📝

*SADAUKARWA*

Daga farko har ƙarshe sadaukarwa ne ga MARYAM SANI HAFIZ (Merry tah) Alkairin Allah ya kai gare ki Allah lulluɓe rayuwar ki da tarin ni,imomi da albarkatu Allah raya mana Abdallah fatan alkairi.

Daga marubuciyar:

Ruɓaɓɓiyar igiya
Ƴan adaidaita sahu
Ungozoma
Ƴar zaman wanka
Ƙara'in inna delu
Beelal
Jalli joga
Da sauran su.

*09013181851*

PAGE 3

Gabaɗaya zuciyar ta ta kwaɗaitu ne da son jin furucin sa a gare ta, ba furucin komai ba face na so da ƙauna tana fatan hakan, idan kuwa har ya furta to ai shi ba mace ba ne da za a ce za a masa dole, kin ga ita Aunty RABEEYA sai ta haƙura wannan ne abubuwan da take rayawa a ranta har ta ƙaraso falon. Ɗaga labulen ta yi tsabar hankalin ta ma ba ya tare da ita saboda zumuɗi da fargaba ta manta da yin sallama. Sai dai abin da ta gani wanda idanunta suka yi tozali da shi, ya so zautar da ita domin kuwa ta kiɗima. Ganin Ya ABDUL zaune a kujerar dab da Aunty RABEEYA da ta sunkuyar da kai tana wasa da hannun ta shi kuma ya ƙura mata idanu yana jifan fuskarta da wani irin kallo mai ƙunshe da ma'anoni da dama, ko wanda ba shi ake yi wa kallon ba idan ya gani ya san so ne mai zallar cike da ƙauna bare kuma wanda ake yi wa kallon.

"Ina son ki RABEEYA ina ƙaunar ki ina son na aure ki a kwana kusa, domin ki dawo kusa da ni mu rayu a inuwa ɗaya... Wannan furucin da yake faɗa yana wani murmushi su ne suka daki kunnuwan HEEDAYA ta ji tamkar wanda aka watsa mata tafashashshen ruwa a jiki, karkarwa ta shiga yi jin jikinta ya ɗauka tamkar mazari, lokaci guda wani abu ya zo ya tokare a zuciyar ta ƙwaƙwalwar ta ta toshe ta ma rasa wane abu ya kamata ta yi, a hankali ta saki labule ba tare da sun san da zuwanta ba bare har su ganta juyawa ta yi da gudu ta nufi part ɗin su.

Ɗakin ta ta shiga ko rufewa bata yi ba ta kwanta tare da sakin kuka mai cin rai, tana jin wayar ta tana ta ruri bayan jimawa kaɗan amma ko ɗagowa bata yi ba ta san ba zai wuce Ya ABDUL ba, wanda a yanzu take jin haushin sa don ya mata gagarumin laifi, laifin kuwa bai wuce na furtawa wata ƴa mace kalmar so ba kalmar da ta yi ta dakon ranar da zai furta a gare ta amma hakan ya gagara ta ci burin furta masa ita ko da ba zai amince ba, amma yau ya furtawa Auntyn ta RABEEYA wannan wace irin baƙar rana ce? Sai dai abin mamaki sai ta ji duk duniya babu wanda take jin tsanar sa sama da Aunty RABEEYA ba don komai ba sai don wanda take so wato Ya ABDUL ta furta kalmar so a gare ta.

Ya ABDUL kuwa bayan ya gama kiran HEEDAYA ganin bata zo ba sai ya yanke shawarar isar da saƙon nasa tun da ji yake ya ƙagu ya furta mata. Shirun Aunty RABEEYA da yadda take sakin wani sassanyan murmushi ya tabbatar masa da maganar sa ta samu matsugunni a wajen ta, hakan ya sa bayan ya isar da saƙon ya ƙara kiran HEEDAYA jin bata ɗauka ba sai suka shiga tattaunawa tana faɗa masa abin da Abba ya faɗa mata ɗazu sosai ya ji daɗin jin wannan batu sai ya shiga godewa Allah.

A can su Ya ABDUL bayan Daddy ya faɗawa Ammie abin da suka yanke shi da Abba na

haɗa Ya ABDUL da Aunty RABEEYA sosai ta ji daɗi tamkar ta zuba ruwa a ƙasa ta sha.

Umma kuwa abin duniya ne ya haɗe mata goma da ashirin, sosai take jin baƙin cikin wannan auren da za a haɗa saboda ta san sai sun ƙara haɗe mata kai. Wani irin takaici take jin don yanzu in akwai abin da yake ci mata tuwo a ƙwarya bai wuce haɗin kan Hajiya Fati da Hajiya Baturiya ba. Jin ta kasa jurewa da sauri ta shanye damuwar ta ɗakko wayarta ta shiga dokawa Hajiya Aisha ƙawarta kira, bugu ɗaya biyu ta ɗauka tamkar wanda take jiran kiran dama.

"Barka da dare ƙawata kin wuni lafiya?"

"Ba lokacin gaisuwa bane babu lafiya"

"Subhanallahi! Mai yake faruwa ne ƙawata?"

"Wani bala'i ne ya tunkaroni" Nan ta kwashe abin da yake faruwa ta faɗa mata, har furucin HEEDAYA a kan soyayyar ABDUL ɗin. Wani uban ashar mai maiƙo Hajiya Aisha ta narka kafin ta ce.

"Amma ke dai wallahi ban san ranar da ƙwaƙwalwarki za ta fara aiki babu gargada ba, yanzu a ce HEEDAYA ta miki wannan furucin maimakon tun kafin shi Alhaji Bashir ɗin ya tara ku ki je ki tunkare shi da maganar, da a ce kin kirani a lokacin kin faɗa mini da na baki shawarar yadda za ki yi, ai shi ya sa a rayuwa ba a so mutum ɗaya ya yanke hukunci da kin ga idan ya ji wannan furucin dole ya dakatar da maganar shegiyar kwantan yarinyar can RABEEYA amma yanzu kin bari komai ya caɓe"

"Haba Hajiya Aisha ya ana nuna miki annabi kina runtse idanu? Ina nuna miki gabas amma kina kallon kudu? Maganar yaron can ɗan gidan Hajiya Fati fa nake miki amma kina batun in amince da batun HEEDAYA. Shin har kin manta butulcin da Hajiya Fati ta yi wa ƙawance na da ita? Kin manta yadda kishi ya rufe mata idanu ta turbuɗawa idanun ta toka ta shuka mini rashin mutunci a kan abin da bani da masaniya tun daga nan sai baƙar gaba ta koma suka jone da kishiyata, amma yanzu kike batun amincewa da auren su in ce na aurawa ƴata wa? Ɗan maƙiyata k...

"Don Allah dakata Hajiya  Zainab, duk kin harzuƙa sai zuba kike ba comma ba fulstop mai ya sa wani lokacin tunanin ki irin na yara ne? " Ɗif Hajiya Zainab ta yi ranta yana ƙuna wai ita ce mai tunani irin na yara Hajiya Aisha bata jira ta amsa mata ba don bata ma bata damar ba ta cigaba da faɗin.

"Ita Hajiya Fati ba saboda mijin ta Alhaji Mukhtar ya ga ƙawarki  Hajiya Bilkisu ya ce yana so ba ne asalin rigimar, duk da ke baki san ma sun haɗu sun ƙulla soyayya ba amma da batun aure ya tashi ta ɗora laifi a wuyanki tana ganin da haɗin bakin ki za a ci amanarta a mata kishiya, duk irin amincin da yake tsakanin ku amma ta sa ƙafa ta yi fatali da su, ta shuka miki rashin mutuncin da kika biye mata kuka kwashi ƴan kallo, kuma daga ƙarshe auren bai yiwu ba saboda masifar faɗan da aka sha yi ba sai ta koma ta jone da kishiyar ki ba?..

"Sai wani maimaicin abin da ya wuce kike na fi so kawai ki faɗa mini abin da zai rage mini zugin da nake ji a zuciyata amma kina mini lissafin abin da na sani" Hajiya Zainab ta katse ta.
"Ki cigaba da saurare na za ki ji bakin zaren, to idan yanzu HEEDAYA ta auri ABDUL kin ga mun jefi tsuntsu ɗaya da dutse biyu. Na farko ɗan ta ya dawo hannun mu tun da yana auren HEEDAYA a nan ne za a yi amfani da shi a ƙuntata mata, ɗanta ya zama mijin ta ce ya manta da ita yake bautawa sirikar sa wato ke kenan da matar sa wato ƴarki kenan, takaici baƙin ciki duk za su taru su mata rubdugu, sannan na biyu kin aurawa ƴarki muradin ta" Tun da ta fara faɗar maganganun Umma ta yi tsai tana jin yadda take zaro magana tamkar wata computer sosai take jinjinawa ƙwaƙwalwar ƙawar tata saboda kaifin basira tana kuma mamakin ya aka yi ita bata yi wannan tunanin ba ya aka yi tun da HEEDAYA ta faɗa mata tana son ABDUL sai kawai ta hau dokin zuciya take ta sukuwa?.

"Kai ƙawata gaskiya ƙwaƙwalwar ki tana ja" Umma ta ce tana jinjinawa lamarin.

"To ai shi ya sa nake faɗa miki mugu shi ya san makwatar mugu, ai in ita sakarai ce bata amfani da tunani wajen yanke hukunci to wallahi da sannu sai mun nuna mata shayi ruwa ne, sai mun zame mata ciwon ido sai ta yi da na sanin ci miki mutunci a rayuwa. Ban san mai ya sa mata wasun su basu da tunani ba wai duk lokacin da za su samu labarin mijin su yana da budurwa ko zai ƙara aure, ko kaɗan basa duba cewa shi fa mijin nan nasu shi ne ya je ya ce yana son macen ba wai macen ce ta ce tana son shi ba, amma sai su hau dokin zuciya su ringa kiran budurwar a waya suna mata barazana da cewa ta rabu da mijin su ko su mata wani mummunan abu, wasu ma har gidan su budurwa ko bazawar suke zuwa su yi cin mutunci. Shin mai ya sa ba za su gane cewa mazan ne masu laifi ba? Su ne suke cewa suna son matan, sannan mai ya sa ba za su hana mazan nasu zuwa wajen matan ba sai dai su ringa tadawa macen hankali bayan ita ma zuwa aka yi aka ce ana son, shin sai yaushe mata za su gane cewa ƙarfe ɗaya ba ya amo?, Kawai don mijin ta zai auri ƙawar ki sai ta ce da haɗin bakin ki wato shi ba shi da laifi sai ke da ita ne masu laifi bayan baki san hawa ba baki san sauka ba"

"Ai in kika ji abubuwan da mata suke yi a kan maza sai kin kama baki, kullum mata suna ƙarar da gishirin su a dahuwar ƙaho ne, yawanci mace ce ta fi damuwa da namiji a kan shi mijin ya damu da ita. Kullum mata ne suke shan magungunan mata don su farantawa mazan su, wasu ma basa duba da rashin ingancin maganin ko illar da zai yi wa lafiyar su, sai dai su yi ta bankawa cikin su da ƙasan su abubuwan don kawai su birge namijin a ƙarshe kuma ya shuka musu rashin mutunci, ko su haɗu da wata cutar sanadin amfani da maganin a ƙasan su, ke hatta planing da mata suke na haihuwa kin taɓa jin namiji ya saka abin planing? Ko ya sha wata ƙwaya ta hana haihuwa, sai dai mata su sha, sai dai mata su saka a dantsen hannun su kai wasu har da wanda ake saka musu a bakin mahaifa komai dai mata ne suke yi don su birge maza amma kuma kullum matan ne a cikin damuwa da taskun rayuwa da tunane tunane da saka kishi a rai da hana zuciya sakat mazan kuma ko a kwalar rigar su sai shegen wulaƙanci"

"Wallahi" Hajiya Aisha ta faɗa.

"Yanzu dai wani hanzari ba gudu ba kin san dai Alhaji idan ya shata layi babu mai ƙetarawa, yanzu tun da har ya yi wannan maganar to babu makawa sai an yi kin ga kenan mun bar kashi tun ran kwasa" Umma ta faɗa tana jiran jin abin da Hajiya Aisha za ta ce.

"Hahahaha, shi Alhaji Bashir ɗin shi ya yi kansa? Ko dole ne aka ce miki sai mutum ya zauna jiran dama, ai mutum shi yake samarwa kansa dama"

"Kamar ya?" Umma ta tambaya cike da son jin bakin zaren.

"Wurin malami za mu je a gobe mu sa ya hargitsa komai ta ɓata komai ya mayar da komai kan HEEDAYA a yi auren da ita kin ga za ta yi farin ciki sannan za mu nuna wa Hajiya Fati a tafin hannun mu take"

Wata dariya Umma ta ƙyalƙyale da ita kafin ta ce.

"Kai wallahi kin biyani Hajiya Aisha gabaɗaya na ji damuwata ta wanke, amma da baki ji yadda nake cikin ƙunci da ɓacin rai ba, ke kin ga da muka fito daga part ɗin Alhaji yadda Hajiya Baturiya take wani ɗaga kai tana fankama ita ala dole za su yi tuwona maina da aminiyar zancen ta"

"Rabu da ƴan iska, za su ga yadda ido zai juye da mujiya" Haka suka sha tsare-tsaren su kafin su yi sallama a kan cewa gobe Umma za ta je ta ɗauki Hajiya Aisha su wuce wajen malamin.

HEEDAYA sai da ta sha kuka tamkar ranta zai fita kafin ta tashi da luhu-luhun idanun ta, ta shiga dokawa Aunty Hafsa waya.

"Hllo ƴar gatan ƙanwata"

"Aunty" HEEDAYA ta faɗa tana fashewa da kuka.

"Subhanallahi mai yake faruwa ne?" Ta tambaya hankali a tashe.

"Aunty ina cikin damuwa" Ta faɗa tare da kwashe komai ta faɗa mata cikin kuka.

"HEEDAYA dama ABDUL ne kike so? "

"Wallahi Aunty ji nake zan iya mutuwa in ban same shi ba"

"Haba HEEDAYA yanzu ai sai ki haƙura tun da dai Auntyn ki RABEEYA za ta aure shi...

"Ni ba Aunty ta ba ce kuma wallahi na tsane ta zan iya yin komai don ganin na mallaki Ya ABDUL ciki kuwa har da kisan kai...

"Kina da hankali HEEDAYA kina cikin hayyacin ki kuwa?"

"Aunty na mutu a kan son shi wallahi, da ƙaunar sa nake rayuwa komai nake zuciyata tana haɗe da tunanin sa, komai na rayuwata da na tsara da shi nake tsarawa sai yanzu a rana ɗaya a dare ɗaya a ce zan rasa shi ba zan iya ba Aunty"

"Ki nutsu ki dawo hayyacin ki, maganar RABEEYA fa ake ko ƙwaƙwalwar ki ta samu taɓuwa ne kin manta cewa ƴar uwar ki ce ta jini uban mu ɗaya da ita babu yadda za a yi ku auri miji ɗaya kuma Abba ba zai taɓa janye maganar sa ki auri ABDUL ɗin ba...

"Aunty ki bar ambata Ya ABDUL zai auri wata, ni kaɗai ce matar sa bana son ya auri kowace mace sai ni kuma ita ma Aunty RABEEYA na tsane ta yanzu saboda ina kishin sa kishi irin wanda ban san wane iri ba ne"

"Bari kawai zan yi magana da Umma" Aunty Hafsa ta ce tana yanke kiran jin tana ta mata magana tamkar ba a hayyacin ta take ba. HEEDAYA kuwa Aunty tana kashe wayar ta jefar da ita a kan gadon ta cigaba da kuka.

Umma zaune take bakin gado tana ta doka murmushin jin daɗin shawarar da suka yanke ita da Hajiya Aisha, har ta fara hango irin mulkin mallakar da za su yi wa Ya ABDUL. Kiran Aunty Hafsa ne ya shigo wayar ta.

"Hafsa"

"Umma barka da dare ya gida"

"Lafiya lau  yau duk bamu gaisa ba ma ina kishiyar tawa Ikram"

"Ta yi bacci" Shiru ya ɗan biyo baya kafin Aunty Hafsa ta ce.

"Umma wai mai yake faruwa ne HEEDAYA ta kira ni tana kuka?"

"Wayyo HEEDAYA da ta yi haƙuri ma burin ta yana dab da cika"

"Ta ina Umma?" Kwashe komai ta yi ta faɗa mata.

"Haba Umma wannan ba daidai ba ne...

"To uwar ƴan wa'azi da nasiha kin fimu sanin ya kamata ne, ke mai ya sa bakya kishin uwar ki

sai ta wasu? Bakya kishin ƴar uwar ki sai wata"

"Ba haka ba ne Umma kin ga HEEDAYA yanzu ta yi candy kafin ta ɗan huta ai mijin ta zai fito kuma duk furucin nan da take yi zafin so ne daga ta ga ya auri RABEEYA za ta haƙura"

"Hafsa babu ruwanki a cikin maganar nan sai inda ƙarfina ya ƙare dama ban hango kyan wuri a kunnen jaka ba sai yanzu da aka buɗe mini komai na gani tangararai" Aunty Hafsa jin Umma ba fahimtar ta za ta yi ba ta mata sallama ta kashe wayar tana fatan Allah ya ktauta ya ganar da su.

Suna yin sallama ɗakin HEEDAYA ta tafi a falo ta samu Mubashshar da Ihsan suna kallo, tana shiga ta mayar da ƙofar ɗakin ta rufe, zaunawa ta yi a bakin gadon ta ɗago HEEDAYA tana lallaɓa ta.

"Kar ki kuskura ko a mafarki ki cire son ABDUL a ranki ko ki saka dangana, ai kawai ki ƙarawa wuta fetur na tsaye miki sai mun ga abin da ya turewa buzu naɗi" Sosai HEEDAYA ta ji daɗin wannan albishir.

Washe gari Umma ta tambayi Abba a kan cewa za ta je gidan Hajiya Aisha ta duba ta ba lafiya, amma idan direba ya kaita a can zai baro ta" Nan ya amince tare da cewa ta mata sannu, lokacin da ta fito rataye da jakar ta da ta lodowa kuɗaɗe za ta tafi sai ga Hajiya Baturiya ta fito daga part ɗin ta ganin Umma sai Momma ta ɗaga murya ta ƙwalawa RABEEYA kira fitowa ta yi Momma ta ce.

"Na tafi gidan aminiyata kuma surukar ki Hajiya Fati" Ta faɗa tana dariya da gayya don ta ƙonawa Umma rai. Umma ko kallon ƙurar da ta ɗakko ta bata yi ba, don ta ga ko mayafi babu a jikin ta ba ma fita za ta yi ba kawai neman magana ne ita ma RABEEYA da ta fito ta gane mai Momma ɗin ta yi juyawa kawai ta yi ta koma ciki.

Direba yana sauke ta ya koma tana shiga ta ga Hajiya Aisha har ta shirya a motar ta suka fito suka tafi Hajiya Aishar ce take tuƙa su saboda zuwa wajen sirri ba a ɗaukan direba. Tafiya mai nisa suka yi har sai da suka fita daga garin na Dutse, sun yi tafiya sosai kafin su bi wata siririyar hanya. Babu komai a dokar dajin sai wani ɗakin ƙasa guda ɗaya jal. Dab da ɗakin ta yi parkin suka fito baka jin komai sai kukan tsuntsaye. A bakin ƙofar suka tsaya maimakon yin sallama sai ihu suka shiga kwaɗawa su duka.

"Ihu-ihuuuuu"

"Ihuuuuu" Aka amsa da ihun daga can cikin ɗakin alama ce da aka musu da cewa su shiga.

"Hajiya Aisha amma wannan malami ne kuwa kodai boka ne?"

"In uban boka ne ma mu dai ba biyan buƙata muke nema ba, kuma da wa ya ce miki akwai malamai yanzu ai ƙalilan ne malamai na Allah da annabi sauran duk buge ne duk sahun bokaye suke.

"Da baya-baya ake shigowa" A hakan suka shiga ɗakin wani tsoho ne tukuf zaune a gaban wata ƙwarya ɗakin duk tarkace ne da  wani gadon kara a ajiye. Sai da suka zauna sannan Hajiya Aisha ta buɗe baki za ta fara magana.

"An sanar da ni komai bana buƙatar ƙarin bayani" Bai buƙaci maganar su ba ya ɗora da cewa.

"HEEDAYA za ta auri ABDULHAKEEM babu makawa amma sai idan an bi sharuɗan da zan gindaya, matsawar aka kuskure to ki sani ba zan iya dakatar da komai ba na fasawar auren da ƴar uwar ta RABEEYA" Kallon kallo aka shiga yi tsakanin Umma da Hajiya Aisha.

"Kun amince?" Kai kawai Umma take gyaɗawa kamar wata ƙadangaruwa ko jin sharaɗin bata yi ba.

"Wannan ganyen guda ashirin da bakwai ne, adadin ranar da aka sanya wato sati huɗu, idan kika irga bakwai sau huɗu ya kama kwana ashirin da takwas kenan wato wata guda, ban da yau kullum za ta ɗauki ganye ɗaya ta yi fitsari a kansa tana mai ambaton sunan ABDULHAKEEM ɗin sai ta saka a shadda sai ta zuba ruwa ya tafi. Tsawon kwanakin nan kar ta masa maganar soyayya kar ta tunkari kowa da maganar a rana ta karshe kuma za ta riƙe wannan layar a hannun hagu sai ta samu wani abu na ci ta tunkari RABEEYA ta miƙa mata kar ta kuskura ta yi magana duk runtsi ko uhum kar ta ce, tana ba RABEEYA abin ita kuma RABEEYA za ta ci abin daga RABEEYAR ta ci sai ta yi sauri ta je ta binne layar to babu makawa da ita za a ɗaura auren!" Ya kai ƙarshe yana ƙara jaddada kar a ƙetara sharuɗan...

MAMAN AFRAH

09013181851
[2/9, 9:57 AM] MOM MASHKUR & AFRAH:
https://chat.whatsapp.com/H8hTgWtMZ3s7uhyedcPR17

BONONO

(RUFIN ƘOFA DA ƁARAWO)

NA

MAMAN AFRAH

First Class Writer's Asso.📝

*SADAUKARWA*

Daga farko har ƙarshe sadaukarwa ne ga MARYAM SANI HAFIZ (Merry tah) Alkairin Allah ya kai gare ki Allah lulluɓe rayuwar ki da tarin ni,imomi da albarkatu Allah raya mana Abdallah fatan alkairi.

Daga marubuciyar:

Ruɓaɓɓiyar igiya
Ƴan adaidaita sahu
Ungozoma
Ƴar zaman wanka
Ƙara'in inna delu
Beelal
Jalli joga
Da sauran su.
*09013181851*

PAGE 4

Duk da Umma ta ji daɗi amma kuma tana ta taraddadi a kan sharuɗɗan. Tafiya suke amma ta kifa uban tagumi, rage gudun Hajiya Aisha ta yi ta ɗan juya ta kalle ta.

"Wai ya haka ne ƙawata ko hankalin ki bai kwanta da aikin ba ne? Ko kuwa dubu ɗari biyar ɗin da ya ce a bashi ne kike ganin ya yi yawa?"

"Haba ke kuwa ai ko wani ne ya ce miki zan yi mita a kan kuɗi kya shede ni kin fi kowa sanin kuɗi ba matsalata bane kuma a kan aikin nan ko miliyan nawa yake buƙata zan bashi don burina da kuma mafarkin HEEDAYA ya cika amma hanzari ba gudu ba ni kar fa a je a samu matsala kin san dai yadda na miki bayani na fuskanci yarinyar nan ta mutu a kan son sa anya za ta bi sharuɗan da aka gindaya kuwa na ganin bata furta masa so ba ko ta faɗawa wani magana dangane da soyayyar?"

"Ana ga yaƙi kina ga ƙura, kar fa ki manta ita ma burinta a bai wuce samun ABDUL ɗin ba ai indai ta ji sharuɗan dole za ta kiyaye ko don ganin muradin ta ya cika" Shiru Umma ta yi tana nazari kafin ta saki wani murmushi ta ce

"Ai shi ya sa bana nadamar samun ki a rayuwata tabbas kaifin ƙwaƙwalwa da basirar ki kaɗai ya ci a jinjina miki, lallai na ƙara yarda cewa tuwon girma miyar sa nama!" Suna ta tattaunawa har suka iso cikin gari gida ta so ta biya ta ajiye ta sai ta wuce amma sai Umma ta sanar da ita abin da ta cewa Abba na duba ta za ta yi bata da lafiya. Sai da ta huta sannan ta kira direba ya zo ya ɗauke ta bayan sun tsara abubuwan yadda za su kasance don Hajiya Aisha ta ce shiri za su fara na bikin tun da suna da dahir da tabbas na cin maganin nan don aikin sa tamkar yankan adda ne ma ba na wuƙa ba.

Cike da annashuwa ta shigo gidan ko da ta haɗu da Hajiya Baturiya a maimakon ta aika mata saƙon harara sai ta sakar mata wani shu'umin murmushi, tare da sanya idanun ta cikin nata ta ce.

"Ka ga Hajiya Baturiya aminiyar Hajiya Fati, iyayan amarya kuma iyayen ango!" Tana gama faɗar hakan ta cigaba da tafiya tana wani murmushin da ita kaɗai ta san manufar sa. Hajiya Baturiya kuwa mamaki ne ya kashe mata jiki don ta san ruwa ba ya tsami banza ko kaɗan bata yarda cewa akwai alkairi ga murmushin Umma ba, ta san akwai wata a ƙasa amma sai dai mene ne a ƙasan? Waye zai bata amsar tambayar wannan cike da kallon tuhuma ta bi bayan Umma har ta ɓacewa ganin ta kafin cikin ƙarfin hali ta ɗaga sagaggun ƙafafun ta ta cigaba da tafiya tana ta faman saƙe-saƙe. Ko da ta shiga falo ganin Na'eema tana zaune tana cin pizza sai ta ɗauki wayar ta ta nufi bedroom ɗin ta don wannan wayar sirri ce bata son kowa ya ji. Hajiya Fati ta dokawa kira.

"Hajiya Baturiya uwar amarya da angon sati huɗu... Maimakon ta bata amsa sai ta ce

"Akwai matsala fa"

"Wace iri?"

"Mutuniyar ki tauraruwa mai wutsiya ce na ganta ta dawo gidan nan cike da annashuwa bayan ba haka ta fita ba anya babu wata maƙarƙashiya kuwa? Gaskiya daga ganin yanayin ta akwai wata a ƙasa"

"Wace irin maƙarƙashiya?"

"Ke kin san Hajiya Zainab ba kanwar lasa ba ce bata barin ta kwana yanayin yadda ta mini ɗazu ya nuna mini kamar tana da wani shiri" Ta kwashe yadda suka yi ta faɗa mata, shiru ya biyo baya tana ɗan nazari da tunani sai kuma ta ce.

"Anya kuwa bana jin akwai wani shiri da za ta yi a kan mu, na fi alaƙanta hakan da borin kunya, amma dai ke kin san in har a kan auren ABDUL da RABEEYA ne kissa da kisisinar ta ko wani shirin ta na ɓoye ba zai sa a fasa ba kin san dai yadda Daddyn ABDULHAKEEN DA Abban su RABEEYA suke da kafiya da jajircewa babu wani abu da zai sauke su daga aƙidar da suka sanya gaba" Ta ce tana ƙara tabbatar mata don a tunanin ta ko kissa za ta yi a fasa auren bata taɓa kawowa ai za ta je wurin boka ko malam ba, sannan kawainiya abu na fili suka sani wato tana kishin alaƙar su ne shi ya sa bata son auren amma basu san cewa akwai wani boyayyan burin ba na son da HEEDAYA take yi wa ABDUL ɗin.

"To shikenan Allah nuna mana wannan rana dai da rai da lafiya a ɗaura auren yaran su tare hankalin mu ya kwanta"

"Amin ya rabb" Da haka suka cigaba da tattaunawa a kan shirye-shiryen tun da suna gani lokacin babu wani yawa sannan suna so su yi komai na kece raini.

Umma tana shiga falo ta samu Aunty Hafsa ta zo, suna zaune ita da Ihsan da Mubashshar sai Ikram tana ta wasa HEEDAYA kuma tana kwance kan doguwar kujera.

"Oyoyo Umma" Ikram ƴar shekara biyar ta faɗa tana ƙanƙame Umma.

"Inyeee kishiyar ke ce a gidan nawa kika zo aure mini miji" Umma ta faɗa tana dariya tare da shafa kanta.

Zaunawa ta yi tana cewa

"Wash na gaji wallahi"

"Sannu da dawowa suka shiga mata inda Aunty Hafsa ta gaishe da ita.

"Umma sai na zo na ga bakya nan duk zuwan da na yi da wuri" Aunty Hafsa ta faɗa bayan sub keɓe.

"Eh na tafi uzurin gabana, ke da na faɗa miki yadda abubuwa suke tafiya kika shiga faɗin Allah ya ce annabi ya ce kike mini nasiha da wa'azi haba Hafsa kamar dai kin fini son Allah ko tsoron sa ne, kar ki manta fa ubangijin nan na kowa ne " Umma ta ce tana faɗa mata inda suka je da Hajiya Aisha a kan aure ya dawo kan HEEDAYA"

"Umma babu macen da za ta auri mijin da ba nata ba, duk runtsi idan har mijin ta ne sai Allah ya juya al'amarin ba wai sai an je neman taimakon wani ba, yana da kyau bawa ya nemi taimakon a wajen Allah, amma yarda da wanin Allah shirka ne da Umma kuma duk wanda ya je

wajen boka sallar sa ta kwana arba'in bata karɓuwa ni a ganina da HEEDAYA da RABEEYA duk ɗaya ne!."

"Au Allah Hafsa? Ni kuma sai na ce duk ban san waɗannan abubuwan ba to tun kan ki diro duniya na san su"

"To amma mai ya sa ba za ki yi amfani da sanin ba Umma, ai amfanin ilimi aiki da shi"

"Wai nema kike ki kafirta ni Hafsa ce miki na yi ban yarda da Allah yake komai ba amma dai an kin san an ce malamai magada annabawa ne, kuma da kike batun rashin karɓuwar sallah mai bakin ki ya ce? Ta kwana arba'in kika ce sallar ba wai an daina karɓa kwata-kwata ba, amma kin san Allah gafurur rahim ne ko, kuma ki sani akwai bambanci tsakanin HEEDAYA da RABEEYA kwatankwacin tazarar sama da ƙasa ni ba ɗaya bane a wajena HEEDAYA ce ƴata! In baki sani ba ki sani mutane da dama sun bar yin sallah domin cikar burin su na duniya sau nawa ƴan siyasa suke cin karen su babu babbaka, saboda neman mulki malamai da bokayen da suke musu aiki su hana su sallah ta tsawon kwanaki ko watanni ma, sau nawa ake zuwa maƙabarta a haƙo gawa a yi asiri da wani sashe na jikin ta, mutane da dama ni fa zan yi sallar amma karɓa ne ba za a yi ba yo wasu umarni da barin sallar ake musu kuma su barta".

"Umma da wanda Allah ya ƙi karɓar sallar sa da wanda boka ko malam ya dakatar da shi yin sallah ni a ganina duk abu ɗaya ne basu da bambanci tun da shi ma wanda ba a karɓa ai ba za a saka masa ladan yin sallar a mizanin littafin aikin sa, shin idan wa'adin ɗayan su ya cika a wannan lokacin wato Allah ya karɓi rayuwar sa ya mutu mai?"

"Kafiri" Umma ta faɗa a harzuƙe don ta gaji da jin i Hafsa iiiii jgudun kar su yi tasiri a kan ta ta sanya ta fasa aiwatar da shirin ta.

"To bambancin musulmi da kafiri sallah ce da sauran ibadu amma sallah ita ce kan gaba da komai a cikin ayyukan bayi, ita ce farkon abin da ake duba wa a cikin aiyukan bayi idan sallah ta yi to sanna saura su biyo baya idan bata yi ba komai ya ɓaci mai ya sa ba za mu kiyaye ta ba? Duk fa wata cim-ma manufa ko buri idan aka je nema wajen boka ko malam to ana hana yin wata ibadah ne saboda shaiɗanu ne ake aikin da su b...

"Ya ishe ki haka Hafsa!" Umma ta faɗa a ƙufule tana ɗaga mata hannu alamar dakatarwa. Ƙwallah ce ta ciko idanun Aunty Hafsa ganin mahaifiyar tata ta yi nisa bata jin kira.

"Nan gidan ubanki ne ba zan hana ki zuwa ba amma in kin san za kike shigar mini hanci da ƙudundune ki tashi ki fita mini a ɗaki" Ta faɗa cikin ɓacin rai tana nuna mata hanyar ƙofa. Da sanyin jiki ta tashi tana ta faman bata haƙuri ta fita daga ɗakin tare da rufo mata ƙofar.

Haka Hafsa ta yi wunin gidan rai babu daɗi domin haka Umma ta ƙi sakar mata fuska babu yabo babu fallasa ta san cewa kawai saboda bata so ta faɗa mata gaskiya ne.

Sai da ƙafa ta ɗauke Umma ta kira HEEDAYA ɗakin ta sai da ta rufe ƙofa har da saka mukulli sannan ta ɗakko jakar da ta saka maganin a ciki. Bayani ta shiga yi mata dalla-dalla tare da faɗa mata sharuɗɗan da aka gindaya.

"HEEDAYA ki tabbatar kin aiwatar da komai kamar yadda aka tsara kar ki kuskura ki ƙetare komai"

"Umma kenan!. Ai babu tangarɗar da za a samu in dai daga gare ni ne saboda wannan abu ne dama da na saka a cikin kaina cewa ko ta halin ƙaƙa sai na mallaki Ya ABDUL ciki kuwa har da bin malaman da bokaye bare kuma na samu mai shige mini gaba? Ai wallahi sai na jajirce na tsaya tsayin daka don ganin burin mu da ni da ke ya cika kuma Ammie sai ta kwashi kashin ta a hannu matsawar na shiga gidan ɗanta sai ya dawo mijin ta ce...

"Kuma mijin mace ɗaya" Umma ta faɗa tana ɗan kai mata duka tana dariya.

"Wannan ma ai faɗa ma ɓata baki ne Umma don bai isa ya zauna da wata mace ba bayan ni kisshin bala'in da yake nuƙurƙusata a zuciya wallahi bana jin zai iya barin Ya ABDUL ya san wata mace bayan ni ni fa ina ganin ƙoƙarin ki Umma, da kika zauna da kishiya ni ba zan ma iya ba gani nake kawai sunana gawa idan za a mini kishiya, shi ya sa na ci alwashi daga ranar da aka ɗaura mini aure zan ajiye zugar ƙawayena wanda basu kai ga samun shafawar fatihar aure ba don wallahi matsawar yarinya bata da aure in dai ƙawata ce babu ni babu ita wala a zahiri ko online na daina kula ƴan mata sai matan aure"

"Inyeee lallai abin naki azimun ne HEEDAYA ban ga laifin ki ba ai kishi kumollon mata ne kuma duk wacce ta tsaya kallon ruwa kwaɗo zai mata ƙafa, ai in dai aka ɗaura auren nan da ke dole na tashi haiƙan na neman miki wurin zama na dindindin daga ke ba ƙari" Umma ta ce tana bata hannu suka tafa, rungume ta HEEDAYA ta yi cikin farin ciki tana jin haƙiƙa mahaifiyar ta ta share mata kukan ta a cikin ɗan ƙanƙanin lokaci. Gabaɗaya maganin ta bata tare da mata nannago a kan ta kula sosai.

HEEDAYA ko da ta kai maganin nan ɗakin ta a drower ta saka tana ji a zuciyar ta matsalar ta ta zo ƙarshe. Kayan bacci ta ɗauka ta saka a jikin ta ta kwanta. Nocking ƙofar ɗakin ta ake bugawa a hankali kamar ba a so tasowa ta yi ta buɗe ganin Aunty RABEEYA sai ta ji wata irin tsanar ta a ranta, shi ya sa ma a yau ta ƙi kwata-kwata su haɗa hanya saboda abin da take ji a ranta. Amma tuno da sharuɗɗan da Umma ta faɗa mata sai ta washe baki.

i"HEEDAYA tah" Aunty RABEEYA ta faɗa tana jin daɗin ganin walwala a fuskar HEEDAYA ƙarfin halin rungume ta HEEDAYA ta yi ɗakin suka shigo suka zauna a bakin gadon tana ta tambayar ta dalilin da ta sa jiya ta sauya mata da kuma dalilin kukan ta nan ta sanar da ita cewa kawai ta rasa mai yake damunta shi ne dalilin kukan nata. Ba don ta yarda da hakan ba sai don ta san cewa HEEDAYA ba za ta mata ƙaryar wani abu da ban ba bata san cewa yanzu wannan

ba HEEDAYAR da ta sani ba ce a baya. Hira suka shiga yi a nan har take bata labarin Ya ABDUL ya zo ya ce yana son ta da bakin sa sannan ta faɗa mata yau ma wuni suka yi suna waya, sosai HEEDAYA ta ji wani abu ya tokare mata sai dai ta yi saurin wayincewa ta ce mata bari ta shiga banɗaki ta fito da to ta amsa ita kuma da ta shiga bayin ta shiga share hawaye sai da ta ɗan taɓa kuka ta wanke fuskar ta sannan ne ta ji sauƙin tuƙuƙin da ranta yake mata goge fuskar ta yi ta fito.

"Amma dai ba fitsari kaɗai kika yi ba har da kashi ko?" Aunty RABEEYA ta faɗa da wasa tana dariya.

"Kai Aunty HEEDAYA ta ce tana dariya, nan dai suka yi sallama ta tafi. Sauƙin da HEEDAYA ta samu a ranta shi ne mafitar da Umma ta samo mata da tunanin fara aikin gobe don cim ma manufarta.

Washe gari HEEDAYA ta buɗe drower cike da murna tana son ɗauko ganye ɗaya ta yi amfani da shi kamar yadda Umma ta sanar mata cewa ta masa fitsari ta saka a shadda ta kora ruwa. Sai dai mai abin al'ajabi sai bata ga ledar mai ɗauke da magungunan ba, hankali tashe ta shiga bincike kayan drower amma ledar magani ta ce ɗaukeni in da kika ajiye ni. Tamkar sabuwar mahaukaciya haka ta shiga watso gabaɗaya kayan drowar a rikice amma bata ga ledar ba wani irin zaro idanu ta yi gabanta yana faɗuwa duk ta hautsi ne ɗakin har ma drower da bata saka ledar a ciki ba sai da ta shiga bincikawa amma bata ganta ba...

A kiɗime ta fito daga ɗakin ta ɗakin Umma ta nufa. Umma wacce yau take jin ta cike nishaɗi da shauƙin samun mafita tana zaune a gaban madubi tana ɗaura ɗankwali baram ta ji ƙaran hankaɗowar ƙofa ta ji tana waiwaya wa ta ga HEEDAYA ta shigo tamkar wacce aka biyo duk ta birkice ga hawaye suna sintiri a kumatun ta . Gaban Umma ne da doka da mugun ƙarfi har bata san lokacin da ta yi wurgi da ɗankwalin hannun ta ba ta taso ta tunkaro HEEDAYA wacce ita ma ita ɗin ta tunkaro.

"Mene ne HEEDAYA?" Umma ta tambaya hankalin ta ita ma a tashe tana fatan dai ba wata matsala ba ce ta kunno kai ma'ana ba amfani ta yi da maganin ba a adaidai ba da kwa sun shiga ɗari uku ma ba uku ba, don sam bata taɓa kawowa ma cewa shi kansa maganin ne ba a gani ba.

"Umma na rasa magani... Tun kafin ta ƙarasa maganar Umma ta zaro idanu tare da saka hannu ta finciko HEEDAYA ta ce

"Kina da hankali kuwa HEEDAYA gidan uban wa kika kai maganin? Kin san ina ne makomar hakan?"

"Umma wallahi na rasa shi a drower ta na ajiye... Tun kafin Umma ta ji ƙarshen maganar ta juya

har da gudun ta HEEDAYA ta take mata baya suka doshi ɗakin HEEDAYAR. Bincike ta shiga yi bayan HEEDAYAR ta nuna mata in da ta ajiye maganin amma ba ya nan. Na shiga uku ni Zainab" Umma ta ce tana ɗora hannu biyu a kai ta saki wani kuka mai cike da ihun takaici saboda ta san komai ya kwaɓe tun da ba a ga magani ba, murna ta koma ciki tun da komai ya ruguje tun da dai magani ya ɓata tun ba a fara aiki da shi ba haƙiƙa da alama murna ta koma ciki. Ita ma HEEDAYA kukan ta saki.

"Bayan kin dawo ɗakin nan da maganin babu wanda ya shigo?" Umma ta faɗa lokacin da wani tunani ya faɗo mata.

HEEDAYA da ta rikice gabaɗaya sai sannan ta yi tunanin cewa ko wani ne ya shigo ya ɗauka tunda ta san dai da hannun ta ta ajiye kuma ma waye zai ɗauka bayan babu wanda ya san ta ajiye.

"Tambayar ki nake?"

"Umma Aunty RABEEYA ce kaɗai ta shigo"

"Ta yi mai?" Umma ta tambaya hankali tashe.

"Kawai hira muka yi take tamyata dalilin da ya sa na mata fushi da kuma faɗa mini...

"Faɗa miki mai"

"Umma bana son furtawa da bakina"

"Ba za ki faɗa mini ba sai na saɓa miki"

"Cewa ta yi wai Ya ABDUL ya ce yana son ta" Ta faɗa kamar ta rushe da kuka saboda ɗacin faɗar cewa ya ce yana son Aunty RABEEYAR .

"Dallah rufe mini baki an faɗa miki da ana sakewa da mutane ne ai ga shi nan ta zo har ɗaki ta ɗauke ledar maganin" HEEDAYA jin furucin Umma a take ta zaro idanu tunowa da ta yi cewa ta shiga banɗaki ta bar Aunty RABEEYA a ɗakin. Gaban ta ne ya shiga bugawa da ƙarfi zuciyar ta ta shiga hautsinawa tana ta ƙoƙarin son tuno wani abun amma ruɗanin da ta shiga ya hana ta tuna komai.

"Shikenan ta rusa komai" Muryar Umma ta katse ta.

*ƘAUYEN KANYA*

Inna Tasallah ce zaune a gaban wuta tana fifitawa ruwan sai tafasa yake tana son yin tuwon amma shiru har yanzu Maryama bata dawo daga niƙan ba. Maimunatu ce ta fito daga ɗaki tana wani yatsina ta ce

"Inna ina wannan marar galihun za ta kai mini ruwa in yi wanka"

"Tana can yawon gantalin ta mana kin ganni ina zaune zaman jiran ta kawo mini niƙa amma shiru kake ji maye ya ci shirwa" Ta faɗa cike da faɗa. Sallamar Maryama ɗauke da roba a kanta shi ya hana Maimunatu maganar da ta yi niyyar yi. Babu wanda ya amsa mata a cikin su sai saƙon harara da suke aika mata su duka tamkar idanun nasu zai faɗo ƙasa. Idan da dabo ta saba da wannan abubuwan amma sai dai ita damo ce sarkin haƙuri.

Wurin Inna ta ƙarasa sai da ta durƙusa da hannu biyu ta miƙa mata robar tana mai cewa

"Inna ga niƙan" Hannu Inna ta miƙa kamar za ta karɓa aikuwa ta ɗaga hannun ta saukewa Maryama yatsun ta biyar a fuskarta.

"Shegiya mai baƙar zuciya in ban da baƙin ciki da takaici a ce tun daɗewa in aike ki amma sai yanzu kika ga damar dawowa?"

"Wallahi Inna injin cike yake da layi ɗaya injin ya lalace kowa nan yake kaiwa shi ya sa layi ya yi yawa"

"Ƙarya kike baƙar munfuka uwar shegiyar ƙarya" Maimunatu ta katse mata magana.

"Yo sai kin faɗa ma waye bai san munafurcin ta ba, tana can dai yawon bin maza" Inna ta ce tana mata wani kallon tsana. Kai ta sunkuyar tana tuna cewa tun da Goggo Shafa ta rasu shikenan ta cigaba da fuskantar tsangwama duk da tana rayen ma tana samun hakan amma ba kamar yanzu da ƙasa ta rufe idanun ta ba.

"Wuce ki kai mata ruwan wanka ki zo ki yi tuwon don babu bawanki a gidan nan da zai miki tuwo dama ganin baki dawo ba ne ya sa na ɗora tukunya" Da to ta amsa kafin ta tafi ta kwalfi ruwa wanda gama jidar ruwan ta yi kenan aka aike ta niƙan kullum haka take ƙarewa a tsaye abinci ma babu mai bata. Ruwan ta kai mata ta dawo ta yi talgen ta bar shi yana dahuwa ta daka daddawa da sauran kayan miyar ta haɗa wata wutar ta ɗora tukunyar miyar ta koma gefe ta doka tagumi tana kallon Inna da Maimunatu suna cin alala wanda wannan ta san abincin la'asar ne suke ci bayan sun ci na rana ita kuma ko na rana bata ci ba rabon da abincin tun ɗumamen safe da Baffa ya ci ya rage mata ta ci.

"Ungo kar in ƙware kin zauna kin kafe mutane da wanna ƙwala-ƙwalan idanun" Maimunatu ta faɗa, Maryama kuwa jin ƴaƴan hanjinta kamar za su tsinke saboda yunwa ta tashi ta je na miƙa hannu gutsiren alalar ta dangwara mata a hannu. Tasowa ta yi ta dawo mazaunin ta tana kallon gutsiren alalar tana tuno maraicin da ta yi na rashin Goggo Shafa duk da ba ita ta haife ta ba amma  dai tana nuna mata gata haka ta ɗaga alalar ta saka a bakin ta wacce gutsira biyu ta yi ta cinye ta suɗe hannun ta je ta wanke hannun ta dawo ta cigaba da aikin.

Baffa ne ya shigo da sallama hannun sa riƙe da buhu da yake daga cin kasuwa yake. Wani daɗi da sanyi ta ji a zuciyar ta ta tabbatar ko ba komai yanzu zai bata wani abu ta saka a cikin ta.

Durƙusawa ta yi ta gaishe shi ds masa sannu da zuwa ya amsa cikin sakin fuska, buhun ya buɗe ya fito da rogo ya fiddo da rake ya bata tana murmushi ta saka hannu biyu ta karɓa tana murna samun abin da za ta saka wa cikin ta. Inna kuwa sai harara take aika mata a fakaice tana wani taɓe baki.

Zaunawa ta yi ta fara tura rogon tamkar za ta haɗa da hannun ta saboda yunwa, Baffa kuwa sai da ya bata sannan ya miƙawa Inna buhun don dama ya san idan ya bata ba lallai ta ba Maryamar ba. Sai da ta cinye rogon tas sannan ta je ta ɗauki ruwa ka sha, lokacin Baffa ya shiga wanka.

Tana dawowa ta zauna kawai sai ta ji cikin ta ya ƙulle ya murɗa mata sai kuma ta ki zuciyar ta tana tashi kafin ta tashi har amai ya ƙwace mata. Da gudu ta yi wajen dabobi ta shiga kelaya amai. Baffa da fitowar sa kenan ya hango ta tana ta amai tamkar za ta amayo kayan cikin ta. Da sauri ya yi wajen ta yana kiran suna ta yana cewa ko lafiya, Inna kuwa wani murmushi ta saki. Ruwa ya bata a buta ta wanke bakin ta ya kamo hannun ta, sai da suka kusa zuwa ya zaunar da ita wani aman ya taho. Da sauri Inna ta tashi ta je wajen tana ƙarewa Maryama kallo.

"Maryama ko ciwon ciki kike, ko dai yunwar ce ta ci ta cinye ki shi ya sa rogon ya ƙi zama a cikin?" Ya tambaya yana kallon ta da tausayawa.

"Haba Malam wannan ai ya fi ƙarfin ciwon ciki " Inna ta faɗa lokacin da ta gwala idanun Maryama.

"To mene ne?"

"Juna biyu gare ta" Ta faɗa hankali kwance cikin halin ko in kula.

"Ci me?" Ya tambaya hankali tashe duk da ba wai ya yarda da shaci faɗin nata ba ne. Maryama kuwa jin furucin Inna babu shiri sai ga ta a tsaye ta miƙe daga sunkuyon da ta yi tana aman jikin

ta sai karkarwa yake.

"Ciki mana ko bata isa ba? Ai dama tsintacciyar mage bata mage, shi ya sa tun a farko da aka tsinci yarinyar nan tun tana jaririya na ce maka kar ka ɗauke ta amma ka murɗe kunne ka ƙi yanzu ga shi nan dama duk wanda ya ƙi ji ba zai ƙi gani ba. Gefen ƙirjin sa ya dafe na hagun saitin zuciyar sa yana mai nuna Maryama da yatsa tare da yanke jiki ya faɗi...

MAMAN AFRAH
09013181851
[2/9, 9:57 AM] MOM MASHKUR & AFRAH: BONONO

(RUFIN ƘOFA DA ƁARAWO)

NA

MAMAN AFRAH

First Class Writer's Asso.📝

*SADAUKAR*

Daga farko har ƙarshe sadaukarwa ne ga MARYAM SANI HAFIZ (Merry tah) Alkairin Allah ya kai gare ki Allah lulluɓe rayuwar ki da tarin ni,imomi da albarkatu Allah raya mana Abdallah fatan alkairi.

Daga marubuciyar:

Ruɓaɓɓiyar igiya
Ƴan adaidaita sahu
Ungozoma
Ƴar zaman wanka
Ƙara'in inna delu
Beelal
Jalli joga
Da sauran su.
*09013181851*

Da sauri HEEDAYA ta juya za ta fita daga ɗakin Umm ta riƙo ta tana jefa mata wani kallo ta ce

"Gidan uban wa kuma za ki je?"

"Zuwa zan yi in tambaye ta ina ta kai mini ledar da ta ɗauka"

"Ashe baki da hankali to in bakaniya kama ɓarawo ba shi kama ka yake yi, sannan ki ce mata magani  mene ne?"

"Haba Umma kin san fa maganin nan yana damfare da kowane cikar burina kawai zan ce mata maganin basir ne na ƙawata na taho da shi daga school a cikin jakata"

"Ita kuma layar fa?" Shiru ta yi ita sai a lokacin ma ta tuna cewa har da laya a ciki gabaɗaya kan su ya ɗaure sun rasa wane kalar tunani za su yi.

"Ni fa Umma sai in ke ganin kamar Aunty RABEEYA ba za ta ɗauki maganin nan ba"

"To ƙafa maganin ya yi ya fita?" Shiru ta yi tana ɗan tunani.

"Ko dai mu ƙara bincikewa a nutse ko za mu gani"

"Hmm! Bincike na nawa kenan ban da wanda aka yi amma ba a ƙin ta mutane wai an ce ɓarawo ya gudu" Umma ta ce tana nufar drower HEEDAYA ma ta bu bayan ta suka cigaba da dubawa amma babu shi babu dalilin sa.

Shiru HEEDAYA ta ɗan yi tamkar wacce take tuna wani abu.

"Kin gani dai da idanun ki ba ya nan in dai ba wani bane ya ɗauka sai dai ko aljannu" Ta katsewa HEEDAYA tunani.

"Tabbas! Jiya da zan ɗauki sleepin dress ɗina na ji faɗowar leda" HEEDAYA ta faɗa tana janye kayan da suke ƙasa ta shiga dubawa.

"Kin ji faɗowar ledar amma baki ɗauka ba wace irin mutum ce ke kuwa ga shi kin rusa komai to ina maganin yake. Ita dai HEEDAYA bata ce komai ba tana ta nazari.

"Ɓera!" HEEDAYA ta faɗa da ɗan ƙarfi jin ƙwaƙwalwar ta ta mata wani tunani ta san tabbas akwai ɓera a ɗakin.

"Ɓera?" Umma ta tambaya da mamaki.

HEEDAYA bata bata amsa ba ta tafi ta fara duba kusurwar ɗakin da bayan gado Umma ma sai ta bi ta suke ta dubawa duk da bata jin wani ɓera ne zai ɗauka ta fi ɗora zargin ta a kan Aunty RABEEYA.

"Lah Umma kin ga ledar can a drower " HEEDAYA da ta hango ledar a batan drower ta faɗa cike da murna. Da sauri Umma ta zo ta leƙa ai kuwa ta hango ledar baki washe ta shiga faɗin.

"Shegen ɓera ashe shi ya ja ledar ɗan banza ya ruɗa mana ciki"

"Umma mu yi addu'a dai Allah sa bai cira ledar ba ko kuma ya taune ledar ya gutsitstsira ganyen" Da haka suka shiga ƙoƙarin janye drower cikin sa'a kuwa suka babu abin da ya yi wa ledar cike da murna suka rungume juna. Umma bata bar ɗakin ba sai da HEEDAYA ta ɗauki ganyen ta shiga bayi ta yi yadda aka ce ta yi.

"Kin tabbatar dai fitsarin ya taɓa ganyen?"

"Ai Umma sai da na jiƙa shi jigif" Ta faɗa tana wata murna ganin ta fara taka tsanin da zai kai ta ga cim ma burin ta.

Tun daga wannan rana kullum sai HEEDAYA ta ɗauki ganye ɗaya ta yi yadda aka ce sannan ta iya takun ta tana nuna wa Aunty RABEEYA farin haƙori har ma da Ya ABDUL bata bari ta furta masa ko nuna masa wani abu da ya danganci soyayya ba.

Kwanci tashi asarar mai rai biki har ya rage saura sati guda a inda ɓangarori da dama kowanne yake ta shirye-shirye. Hajiya Fati uwar ango tana nata shirin don ita ma biki ta shirya yi na kece raini gidan ango ya sha fenti komai saboda kayan Aunty RABEEYA wanda Hajiya Fatin ce ta yi wa Momma rakiya suka zaɓo don koman su tare suke yi sai dai suna mamakin yadda Umma bata nuna musu komai na auren ya dame ta hasali ma sai take nuna wa Momma faran-faran a fuska wanda a zuciyar ta so take kawai tarkon da suka ɗana ya kama tsuntsu, babu abin da ya rage illa kawai jiran ranar ɗaurin auren don daga Umma har ƙawarta Hajiya Aisha tare da HEEDAYA sun saka wa ransu cewar auren da za a ɗaura babu makawa da HEEDAYA za a ɗaura bisa lura da maganin da suka ci alwashin kyansa kamar yankan wuƙa. A zahiri HEEDAYA tana nuna shirin auren Aunty RABEEYA take yi amma a baɗini shirin nata auren take don tana da tabbacin ita ce za ta tare a ɗakin Ya ABDUL ba Aunty RABEEYA ba.

Umma da Hajiya Aisha da HEEDAYA su suka je wajen siyar da kujeru da kayan gado na kece raini HEEDAYA ta zaɓa suka biya kuɗin a kan cewa za  su zo su ɗauka daga baya don kamfanin da suka siya katan sanannan kamfani ne. Kayan kicin ma haka suka loda kamar babu gobe a nasu nufin idan ɗaurin auren ya juye zuwa kan HEEDAYA sai a kwashe kayan Aunty RABEEYA a jera na HEEDAYA.

"Umma wannan lafayar fa?" HEEDAYA ta tambaya tana ɗaga kayayyakin da Umma ta kira ta ɗakin ta ta gani.

"Wannan ita ce za ki saka ranar ɗaurin auren idan za a kai ki ɗakin mijin ki ita za ki naɗa" Umma ta ce tana washe baki tare da ƙara kallon laffayar mai manyan fulawoyi  irin kuɗin da ta narka don fito da amarya HEEDAYA fess a idon masoya da ma maƙiyan baki ɗaya. Sosai HEEDAYA ta ji dadɗin ganin laffayar har ta fara hango irin kyawun da za ta mata a ranar da ta naɗa don zuwa ɗakin mijin ta a matsayin amaryar sa lallai wannan rana za ta zame mata ɗaya tamkar da dubu rana ce mai tsananin tarin tarihi a rayuwar ta.

"Ummana Allah ya bar mini ke ina ƙaunarki ina alfahri da samun ki matsayin uwa, wacce take faɗi tashi don farin cikin iyalin ta" Ta ce tana kara laffayar a jikin ta lokacin da take tsaye gaban mudubu tana ganin irin kyan da ta mata.

"Ni ma ina ƙaunar ku HEEDAYA burin kowace uwa ta sanya ɗiyanta farin ciki marar yankewa"

"Haka ne Umma amma ke kam kin sha bamban da wasu uwayen duba da yadda kike amfani da aljihun ki da lafiyar ki don cikar burina haƙiƙa ba zan taɓa mantawa da wannan abin da kika mini na jajircewa don ganin na samu zaɓin raina kuma muradin rayuwata, ba zan gushe ina miki addu'a ba har ranar da numfashi na zai tsaya domin Allah ne kaɗai ya san irin tarin ƙaunar da nake yi wa Ya ABDUL ga shi zan mallake shi a ɓagas cikin sauƙi cikin ruwan sanyi" Ta faɗa lokacin da take rungumo kafaɗar Umma.

"Wannan dole ne ma HEEDAYA cikar burin ki da kuma ambulawa maƙiya ƙasa a ido dole ranar ɗaurin auren nan daga akala ta sauya an ɗaura da ke to har sai na zubar da ruwa a ƙasa na sha" Ta faɗa tana dafa bayan HEEDAYA haka suka cigaba da tsare -tsare.

Yau laraba ya rage saura kwana uku ƙwarara ɗaurin auren Ya ABDUL da Aunty RABEEYA a zahiri kenan amma a badɗini ta ɓangaren su Umma saura kwana uku ɗaurin auren HEEDAYA da Ya ABDUL. Shiri ya kankama ta kowane ɓangare Aunty RABEEYA da ta ce HEEDAYA ta zo za su tafi gidan ƙunshi da ƙwayaye ta.

"Haba Aunty RABEEYA ina ƙanwar amarya fa ango zan zauna in ke bin ku ah lallai ai ni ma gashin kaina zan ci ni da ƙawaye na ku tafi naku ƙunshin mu ma mu tafi" Ta faɗa cike da zolaya tana dariya, don ita ma ƙunshin amarya za ta je a yi mata tun da tana ganin ma ai ita ce amarya ba Aunty RABEEYA ba a ganin ta Aunty RABEEYA wahalar da kanta kawai za ta yi tun da ba aure za a ɗaura mata ba.

"Allah sarki my HEEDAYA na gode! Shi ya sa nake ƙaunar ki wallahi" Ta faɗa cike da jin dadɗi tun da tana tunanin HEEDAYAR duk shirin nan da take domin ita take yi bata san ita ma wani

nufin ne a ranta ba na ganin an ɗaura auren da ita.

Sosai HEEDAYA ta gayyaci ƙawayen ta ƙwan su da ƙwarƙwatar su, tana faɗin bikin yayar ta za a yi don ta fi so sai sun zo su ji ita ce amaryar MEEMA babbar ƙawar ta kawai ta faɗawa cewa tana sa ran a ɗaura auren ta da Ya ABDUL ɗin tun da ta san ya take son shi. Don ita MEEMAR ma da ranar auren ta a kai suka kammala karatu.

Umma da Hajiya Aisha ma gayyata suka yi sosai suka gayyato ƙawayen su da abokan arziƙi a cewar Ummar mijin ta ne yake aurar da ƴa amma ƙudurin zuciyar ta tafi so sai sun zo in aka sanar da ɗaurin auren sai su taya ta murna da gayya.

Amarya HEEDAYA da amarya RABEEYA duk sun sha gyara ciki da waje an sha ƙunshi baƙi da ja an sha saloon don HEEDAYA wani ƙananan kitso aka mata na ibra. Magungunan mata kuwa da tsumi babu wanda Umma ta manta wajen gyaran har da su kazar amarya. Fatar nan da ta sha gyara sai sheƙe take abin sai sam barka kowa sai yake zolayar HEEDAYA wai ƙanwar amarya ta zaƙe da yawa sai dai ta yi dariya a fili ta ce

"Yo ba dole ba ana yi wa Aunty RABEEYA tah aure" A zuciyar ta kuma ta ce

"Hmmm! Iska tana yawo da mai kayan kara da sannu za ku gane ainihin dalilin gyaran nan da na yi wallahi ko tausayin Aunty RABEEYA ba zan ji ba idan ta ji da ni aka ɗaura idanuna zan shafawa toka i  cigaba da hidimata don har ƙwarya-ƙwaryar party zan shirya a ranar.

'Hajiya Momma uwar amarya, ya aka yi kuma ido ya juye da mujiya? Yanzu dai kin gane lokaci yana sauyawa a koyaushe ƙaddarar mutum kuma tana iya sauyawa daga mummhna zuwa kyakktawa ko ta canja daga kyakkyawa zuwa mummuna' Wannan su ne kalaman da HEEDAYA take ayyanawa a zuciyar ta za ta faɗawa Momma idan aka ɗaura auren ta.

"Yanzu kun yarda ruwa ya ƙarewa ɗan kada? Ko kun san cewa idan taƙamar mutum wuni ya yi a zaune wani kwanan hanya ya yi, duk runtsi kar ka raina shirin wani don shirin ka ka sani shi wancan baka san shirin sa ba amma Allah shi ya san karatun kurma!"Waɗannan su ne kalaman da Umma ta tanada za ta yi wa Momma da Ammie martani da su idan aka ɗaura auren HEEDAYA da Ya ABDUL.

Yau za a yi kamu tun la'asar ɗin fara HEEDAYA ta shirya cikin rantsatstsen leshin ta dark blue mai  fulawa ja da light blue ɗin mai make up ɗin da Umma ta ɗakko musu ta musamman ita ce ta tsantsare HEEDAYA da kwalliya mai ɗaukan hankali aka mata ɗauri sosai ta yi kyau ta fito a amaryar ta sak don ta ɗau aniyar yau sai dai su saka angon a tsakiya don ita ce amarya ba za

ta taɓa yarda ta zauna a inda babu ango. Umma da Hajiya Aisha ma make up ɗin su aka musu suna sanye da atamfa iri ɗaya an musu ɗinki sai zabga ƙamshi suke ita dai Aunty Hafsa tana ta jin babu daɗi tub da ta san shirin na su Umma kuma tana fatan Allah kar ya basu nasara duk da tana fargabar ranar ɗaurin auren, tun da dai ta san asiri gaskiya ne sannan hausawa suna cewa camfi gaskiyar mai shi. Kowa ya fito cass Ammie ma uwar amarya da Momma uwar ango su ma ankon su suka yi. Aunty RABEEYA ma an mata make up ɗin ta simple make up ne ta yi kyau kamar ka sace ta ka gudu. Sosai take jin farin cikin tana jin daɗi a ranta ashe ita ma da rabon za ta yi aure tana son ganin ranar da za a ɗaura mata aure ba ta san inda za ta saka ranta ba saboda daɗi.

Motoci sun hallara inda masu anko ƙawaye da ƴan uwa suke shiga motocin da aka tanada don zuwa wajen kamun. HEEDAYA da duk ta samawa ƙawayen ta motoci amma ita sai ta ƙi shiga kowace motar da aka tanada ta amarya da ango bayan sun shiga sai ga ta ta zo ta tsaya a jikin windown ta yi nocking Aunty ARABEEYA da fuskar ta take rufe da mayafin ta ta ɗago ganin HEEDAYA da sauri ta sauke glass ɗin ta ce

"HEEDAYA tah"

"Aunty ni a motar ku zan tafi" Ta faɗa tana yin raurau da ido tare da zunɓuro baki, shiru Aunty RABEEYA ta yi tana jinjina irin soyayyar da HEEDAYA take mata tare da cewa

"To shigo mu tafi" Momma da ta hango HEEDAYA tana shirin shiga motar amarta da ango da sauri ta taho har tana neman yin tuntuɓe cikin ɗaga murya tun kafin ta ƙaraso ya ce.

"HEEDAYA ke HEEDAYA!" Dakatawa ta yi tana juyowa tare da haɗe rai ta yi wa Momma wani kallon rainin hankali ba tare da ta amsa sunan ta da Mommar take kiran ta ba.

"Duk motocin nan da aka tara sai a motar amare za ki tafi?" Ta tambaya tana aika mata harara.

"Haba Momma ki bar ta mana ai wajen zai isje mu" Aunty RABEEYA ta faɗa tana kallon Momma da ta mayar da kallon hararar kanta don ta ji haushin furucin.

"To sai dai ta shiga gaban motar"

"Momma ki ƙyale ta mana HEEDAYA ai tamu ce" Ya ABDUL ya faɗa yana dariya don shi ya ɗauka kawai rigar HEEDAYA ce.

A ƙufule Momma ta kuya cike da takaici ba tare da ta furta komai ba, da sauri HEEDAYA ta juya ta bar jikin ƙofar da Aunty RABEEYA take ta koma saitin ƙofar Ya ABDUL.

Kawai sai buɗewa ta yi shi kuma sai ya matsa kusa da Aunty RABEEYA ita kuma ta shiga ta rufe ƙofar ya zamana sun saka shi a tsakiya sai sannan hankalin ta ya kwanta ganin ga ta ga

angon ta kyawun da ya yi ya tafi da ita sai satar kallon sa take tana jin kishin Aunty RABEEYA da take kusa da shi.

A haka gabaɗaya motocin suka lula a kan titi. Yadda aka tsaro wajen shiga wajen kamun yara a gaba sai ƴan mata wanda suke sanye cikin anko. Amarta da ango da suka bi sahu har da HEEDAYA. Waje ya kaure da kiɗa amarya da ango da HEEDAYA saboda ƙoƙari faɗawa mijin baya tariya har da ita suka zauna a kujerar amarya da ango masu hoto sai haska su ake yi. Bayan MC ya buƙaci amarya da ango a fili HEEDAYA ta buɗe bakin jakarta tana liƙi wa Ya ABDUL ita kuma Auntt tana liƙawa HEEDAYA shi kuma yana liƙa musu su duka. Sodai aka raƙa she har aka tashi kowa ya watse.

Washe gari ma ko a wajen dinner haka ce ta kasance duk inda amarta da ango suke ƙafar su ƙafar HEEDAYA.

Ranar asabar wacce ta ita ce ranar ɗaurin aure. Tun da sanyin safiya Umma da HEEDAYA suke ƙusƙus suna tsara yadda komai zai kasance, wato yadda za ta kai wa Aunty HEEDAYA abin da za ta ci riƙa da layar maganin a hannun ta. Ƙarfe sha ɗaya da rabi shi ne lokacin da za a ɗaura aure.

"HEEDAYA ki fara zuwa ki dubo inda take ki tabbatar tana nan kuma kin ga dai yadda gidan nan yake a ciki ki tabbatar babu wanda kika yi wa magana" Umma da ta jata cikin banɗakin ta take raɗa mata don ma kar wani ya yi laɓe a ɗaki ya ji su.

"To Umma bari na sake dubowa ɗazu dai na hango shigar ta part ɗin Abba Hajja ce a can take kiran ta "HEEDAYA take tabbatar mata da ta ga Aunty RABEEYA ta je wajen Hajja kakar su mahaifiyar Abba.

"Umma bari na je tana part ɗin Abba ita kaɗai tana zaune Hajja ta zaunar da ita, ita kuma Hajjar ta je ta ɗakko wani turare za ta shafa mata a goshi wai haka ƴan da suke yi zamanin su Hajj...

"Ba dogoj surutu za ki tsaya ba tun da Abban naku sun fita ki yi sauri ki je ki aiwatar" Umma ta katse ta don yanzu hankalin Umma gabaɗaya a tashe take ta fi so har sai an aiwatar da aikin nan na ƙarshe tun da an gama na duka ganyen. Da sauri HEEDAYA ta zaro layar daga ƙugunta da ta soke ledar, fito da layar ta yi ta damƙe tare da ɗaukan cake guda ɗaya ta fito daga part ɗin Umma tana ta sauri sai gifta mutane take ana mata magana amma babu wanda take tankawa hankalin ta ya yi part ɗin Abba. Zaune ta samu Aunty RABEEYA tana danna waya cake ɗin ta miƙa mata ba tare da ta ce komai ba, Aunty RABEEYA cike da jin daɗin kulawar da HEEDAYA ta mata ta miƙa hannu ta karɓa ta sanya a baki ta fara ci sai da ta cinye. Ganin haka HEEDAYA ta juya da sauri ta nufi bayan gidan ta haƙa rami ta binne layar ta taso ta baro wajen. Ɗakin Umma ta nufa tana zuwa ta rungume Umma da suke tare da Hajiya Aisha gabaɗaya daga Hajiya Aisha har Umma su ma rungume ta suka yi cike da murna don sun san aiki ya kammalu saura jiran sakamako.

"Ayyiriri-yiriyiri!!!." Hajiya Aisha da Umma suka rangaɗa guɗar farin ciki wanda hakan ya jawo hankulan gabaɗaya ƴan falon sai dai babu wanda ya nufi ɗakin sai Aunty Hafsa tana buɗe ƙofar suka haɗe rai Umma ta shiga jefa mata harara siyam-siyam ta juya bayan ta girgiza kai alamar basu kyautawa!.

Ƙaran tsayawar motocin ƴan ɗaurin aure da yake a babban masallacin juma'a aka je aka ɗaura da kiɗan ganguna haɗe da muryoyin maroƙa da suke tashi cikin lasifika. Ita ce ta assasa faɗuwar gaban mutane uku da mugun ƙarfi Umma, Hajiya Asha da kuma mai gayya mai aiki wato HEEDAYA a yanzu babu abin da kunnuwan su suke son ji sama da jin an ɗaura auren HEEDAYA da ABDUL duk da sun san babu makawa yin hakan tun da sun tabbatar da ingancin aikin da aka yi kuma an aiwatar. Amma duk da haka suna jin fargabar sakamakon!.

Muryar wani maroƙi da ya durfafo cikin gidan suka baza kunnuwa kamar na zomo suna son jin da wa aka ɗaura?

"Allah ya kawo mu, aure ya ɗauru tsakanin ABDULHAKEEM Mukhtar da amaryar sa...

MAMAN AFRAH
09013181851
[2/10, 2:13 PM] MOM MASHKUR & AFRAH:
https://chat.whatsapp.com/F7TUZezpOWLKYnyTNFuy2Y

BONONO

(RUFIN ƘOFA DA ƁARAWO)

NA

MAMAN AFRAH

First Class Writer's Asso.📝

*SADAUKAR*

Daga farko har ƙarshe sadaukarwa ne ga MARYAM SANI HAFIZ (Merry tah) Alkairin Allah ya kai gare ki Allah lulluɓe rayuwar ki da tarin ni,imomi da albarkatu Allah raya mana Abdallah fatan alkairi.

Daga marubuciyar:

Ruɓaɓɓiyar igiya
Ƴan adaidaita sahu
Ungozoma
Ƴar zaman wanka
Ƙara'in inna delu
Beelal
Jalli joga
Da sauran su.
*09013181851*

PAGE 6

Su duka ukun sai suka yi tamkar an dakatar da gudun numfashin su, domin kuwa kowanne sai ya yi tamkar za a sanar da mutuwar wani makusancin sa duk sun shiga mummunan yanayin son jin sunan wanda maroƙin zai ambata.

"Tsakanin ABDULHAKEEM Mukhtar da amaryar sa RABEEYA Bashir" Wannan furucin maroƙin ya daki gabaɗaya ƙwaƙwalwa da zuciyar su Umma, lokaci guda kunnuwan su suka yi dumm ya zamana sun daina jin kowane sauti. Amma saboda ƙarfin hali sai suka fara kokwanton abin da suka ji kowanne sai yake ganin ba daidai kunnen sa ya jiyo masa ba, kowanne yana jin kawai dai tsabar son jin abin da za a faɗa ne ya sa suka shiga ruɗani.

Kallon - kallo suka shiga jifan junan su da shi kowanne yana son ɗan uwan sa ya bashi tabbacin gaskiyar abin da kunnen sa ya ji.

"Auren masoya kuma ƴan uwa an yi auren zumunci ABDULHAKEEM da RABEEYA Allah kawo mu ranar suna" Suka ƙara jin furucin maroƙin daga lasifikar nan irin wacce maroƙa suke yawo da ita a hannu.

Idanu Umma ta zaro da sauri ta tashi tsaye tana yaƙi da hankalin ta ganin bai gudu ya barta ba don ji take tamkar dai ƙwaƙwalwar ta za ta samu taɓuwa saboda furucin da ta saurara mai cike da ruɗani!. Lokaci guda kuma HEEDAYA da hawaye ya wanke mata fuska take fusgo numfashin ta dakyar suka miƙe ita da Hajiya Aisha.

"Na shiga uku Umma!." HEEDAYA ta faɗa jikin ta yana karkarwa ƙirjin ta yana wani hawa da sauka.

"Mun shiga uku dai!" Umma da Hajiya Aisha su ma suka faɗa hankali tashe.

"Hajiya Aisha ashe bokan nan maƙaryaci ne? Mu zai yaudara? Ya sa muka saki jiki da aikin sa ashe ƙarya ya zabga, da a ce na san aikin sa ba zai yi ba da tuni ko a bangon duniya ne sai na je na samo magani, amma ya sa sai da ranar ta zo lokaci ya ƙure ga shi babu dama ko hali yarinyar nan su haɗa miji tun da uban su ɗaya, kin san dai ko a garin mahaukata HEEDAYA ba za ta auri mijin RABEEYA ba" Umma ta faɗa tana kallon Hajiya Aisha tamkar za ta kai mata dukan tsiya saboda kawai haushin ta take ji don ranta ya yi mugun ɓaci.

"Hajiya Aisha ta ce

"Hajiya Zainab kin san dai ba zan kai ki in da bani da tabbas ba, kin fi kowa sanin na san kusufa-kusufa lungu da saƙo na malamai da bokaye masu aiki tamkar yankan wuƙa" Duk maganganun nan da suke HEEDAYA tana tsaye tamkar zautacciya ta rasa wane kalar tunani za ta yi gabaɗaya bata gane mai suke cewa tamkar wata taɓaɓɓiya haka ta koma, basu ankara ba sai gani suka yi luuu ta yanke jiki ta faɗi sumammiya!.

A kiɗime suka durƙushe a gaban ta suna jijjijgata, Hajiya Aisha ganin Umma ta fara kuka hankali tashe da gudu ta nufi banɗaki ko takalmin ƙofar banɗakin bata saka a ƙafar ta ba, ruwa ta kwalfo a kofin wanka ta fito a ruɗe tana zuwa ta sheƙawa HEEDAYA. Farfaɗowa ta yi a firgice tana faɗin

"Na shiga uku Umma wata ta auri zaɓina, Ya ABDUL ba ni ba wayyo zan mutu ba da ni aka ɗaura ba wayyo na gama yaudarar zuciyata yau zan kasance a gari ɗaya, a unguwa ɗaya a gida ɗaya kuma a ɗaki ɗaya da Ya ABDUL ashe dai mafarki ne burina ba cika zai yi ba" Ta furta cikin kuka.

"HEEDAYA ki yi haƙuri na yi iya yina ban taɓa zaton hakan ba zai cika ba wallahi ban taɓa kawowa aikin nan ba zai ci ba, gabaɗaya na saki jiki da cewa an ɗaura da ke an gama ban san za a samu akasi ba ban san za a samu saɓanin tunanina ba HEEDAYA" Umma ma ta faɗa tana hawaye tana tuna cewa shikenan zumuncin ƙawancen Hajiya Fati da Hajiya Baturiga zai ƙara ƙarfafa, ashe dai duk shirin su ya tashi a banza da siyen kayan ɗaki da na kicin da komai da komai ba ma wannan ne abin jin ba sai magungunan matan da suka ɗirkawa HEEDAYA don sun ɗauka yau za ta kwana gidan miji ashe dai lisaafi da hasashen su ne.

"Na tsane ta Umma na tsani Aunty RABEEYA na tsane ta wallahi"

"Ni ma na tsane ta HEEDAYA da a ce ya halatta ku auri miji ɗaya da wallahi ko ta halin ƙaƙa sai na samo mafitar da sai an ɗaura da ke, sai kin rigata shiga gidan sai dai ta zo daga baya amma ke ce uwar gida dole ta zauna a ƙarƙashin ki sai dai kash!. Bakin alƙalami ya bushe f...

"Umma ki daina ambaton auren miji ɗaya ni fa bani da kishiya a duniya ba zan taɓa zama da kishiya ba a rayuwata mijina ni ce amaryar sa kuma ni ce  uwar gidan sa " Ta faɗa cikin kuka da tashin hankali.

"Ku yi haƙuri don Allah dole mu samu mafita a yau kuma a yanzu!" Hajiya Aisha ta faɗa tana tashi tsaye tare da kama ƙugu da hannu biyu tana ɗaga kai sama irin tana tuna yadda komai zai wakana. Kallon baki da hankali Umma ta jefe ta da shi tana kawar da kai wani tuƙuƙin baƙin ciki yana ƙara ratsa zuciyar ta, don tana ganin ita ce silar komai da ba don ta kai ta wajen da ta karɓo maganin ba, da bata ma saka ran cim ma buri ba daga ita har HEEDAYA.

"Dole ne ya san abin yi don a yanzu ba sai an jima ba za mu koma wajen sa"

"Wai maganar wa kike? In dai wannan tsohon ne na yafe aikin da ya mana a kwana ashirin da bakwai ma bai yi ba sai wanda zai yi yanzu ai bakin alƙalami ya bushe, tun ran gini tun ran zane, kin san dai an riga an ɗaura auren nan kuma ya haramta su aure shi su biyu kasancewar su jini ɗaya...

"Haba ƙawata ki daina mini magana cikin hargagi kina neman ɗora laifi a kaina bayan ni ma burina da fatan bai wuce irin naki burin ba"

"Na ji! Yanzu mene ne abin yi?" Umma ta tambaya tana ɗago kai ta kalle ta har lokacin tana rungume da HEEDAYA da take ta shashshekar kuka tamkar ranta zai fita irin yadda sautin kukan yake fitowa daga asalin ƙarƙashin zuciyar ta.

"Za mu koma wajen malam"

"Ki kira shi da sunan sa na asali kuma na yanka wato boka don wannan bashi da haɗi da malamai"

"To na ji! Mu koma wajen boka shi zai faɗa mana komai "

"Ni ban ga amfanin komawa ba tun da wuri ya ƙure!" Cewar Umma.

"Ki ƙara bani dama!"

"To shikenan amma kin san yanzu waje cike yake da jama'a kina ji sai kaɗe-kaɗe da bushe-bushe yake tashi shin idan ma Alhaji ya gan mu in ce ina zan je tun da dai ya san ana

taro ba za mu je ko ina ba bana son ya ɗora zargin sa a kan mu"

"In sha Allah ba zai gan mu" Ba don Umma ta gan su ba ta amince haka ta lallaɓa HEEDAYA a kan cewa ta daure za su je su dawo a kan gadon ta kwanta kamar matacciya suka fito suka rufo mata ƙofar. Yadda gidan yake a cike amma su hankalin su ba ya kan kowa hankalin su ya yi wajen bokan su.

Lokacin da suka fito cike da fargabar kar Abba ya gan su amma sai suka samu motocin suna ta ɗaukan ƴan ɗaurin auren zuwa wajen da aka tanada don cin abincin ƴan ɗaurin auren. Don haka Abba ya shiga mota shi ma daga can suka hango tsayawa suka ɗan yi duk motocin suka yi gaba sai ragowar wanda ba a ɗauka ba da maroƙa da almajirai haka da kuma yaran anguwa da suka zo. Motar Hajiya Aisha suka shiga ta fige ta  360 suka kama hanyar barin cikin garin. A daidai inda suka yi parking ranar nan yau ma a wajen suka yi bayan sun sha kwaɗa ihu kamar wasu sabbin ƴan tauri, ya amsa musu da ihun sannan suka shiga da baya. Kan su suka yi wa mazauni a gaban sa Umma da take cike fam da haushin sa don ranar nan girman sa take gani amma yau sai ta ji ya faɗo wanwar a gunta sheƙeƙe ta kalle shi cikin raini da izgilanci za ta fara magana don a ganin ta ha'intar su ya yi ya cinye kuɗin su amma babu biyan buƙata ga shi ya sa sun ɓata gishirin su a dahuwar ƙaho da tuni sun nemi mafita amma yanzu ya sa wuri ya ƙure!.

" Dakata!. Bana son jin bayani tuni na san komai" Ya faɗa yana ɗaga mata hannu. Wani kallon da wa muka zo ta masa, ba don ta so ba ta kama bakin ta ta masa ɓam a hakan ma don Hajiya Aisha tana tausar ta da ido amma duk da haka ta ci alwashin matuƙar ya raina musu hankali da shaci faɗin sa to tabbas sai ta masa wankin babban bargo ba wai a kan kuɗin ba ita damuwar ta rashin cikar burin nasu a kan aikin!.

"Ba ma aiki a zo da maganar banza! Mun fi ƙarfin a tuhume mu, mutum ya tabbatar ya aiwatar da komai cikin hikima kafin ya zo mana da maganar banza matsawar aka samu tangarɗa ba a bi sharaɗi ba to dama ba za a samu yadda ake so ba shi ya sa ma na gargaɗe ku na nannaga muku sharaɗin don ku kiyaye! Amma sai da aka samu matsala" Ya faɗa lokacin da yake kallon cikin ƙwaryar gaban sa.

Wani kallon rashin fahimtar inda zancen sa ya dosa suka shiga jefa masa kafin Umma ta ce

"Wallahi boka ta aiwatar da komai yadda ka faɗ...

"Ƙarya ne!." Ya faɗa a harzuƙe yanayin yadda ya yi maganar a tsawace cikin wata murya ya da suka razana don Hajiya Aisha har ta kai bakin ƙofa babu shiri, ita kuma Umma ta tashi tana neman faɗuwa tsabar tsoratar da suka yi don sai suka ji maganar har amsa kuwwa ta yi, duk zaton su ma aljannun da yake aiki da su zai kirawo musu. Sun san kuwa karo da aljani ba sauƙi.

"Ku dakata kar wacce ta fita" Ya faɗa wannan karon sai suka ji muryar sa ta sauya daga ta dattijo zuwa muryar saurayi. Da karkarwa suka dawo suna mamakin yadda suka tsorata haka, kowacce mazaunin ta ta koma tana rarraba ido.

Da ido suka kafe shi ganin yana yin wani rubutu a kan ƙwaryar da take da wani abu kamar madubi. Kamar daga sama sai suka ga HEEDAYA ta bayyana a cikin madubin. Kallon kallo aka shiga yi tsakanin Umma da Hajiya Aisha saboda kowacce cikin su ta tabbatar HEEDAYA ce sanye da kayan da suka baro ta a gida, kafin su mayar da kallon kan ƙwaryar tana sanye a cikin ta, ta fito tana ta waige -waige kamar marar gaskiya. Baki a sake suke kallon ta tarwai tamkar su ɗakko ta ko su mata magana ta amsa don tamkar bidiyo haka suka gani. Part ɗin Abba ta dosa tana ta faman waiwaye, su duka gaban su ne yake faɗuwa don basu gane inda bidiyon ya dosa ba, duk a zaton su yanzu bayan sun baro ta ne ta ware daga damuwar da take har ta fito amma dai suna son ganin mai yake son nuna musu ita Umma a zuciyar ta ma tana taraddadin kar ya cutar mata da ƴa tun da ta ji yana batun an masa ƙarya.

A falon Abba suka hango ta sai kuma Aunty RABEEYA zaune a kujera, tana hango shigowar HEEDAYA ta washe baki cike da murnar ganin ta, da haka suka ga HEEDAYA ta nufi wajen ta ba tare da ta ce komai ba ta miƙa mata abu sai da ta karɓa suka gane cake ne sai lokacin suka gane ashe lokacin da ta tafi aiwatar da aikin layar nan ne. Idanu suka ƙara zubawa ganin Aunty RABEEYA ta karɓa tana ci hankalin kwance sai kallon HEEDAYA take tana mata murmushi mai cike da so da ƙauna. Sai da ta cinye suka ga HEEDAYA ta juyo ta fito a wajen part ɗin ne suka hangi Daddy(Alhaji Mukhtar Daddyn ABDUL ) Ya nufi part ɗin yana ta baza babbar rigar kiciɓus suka kusa yi da HEEDAYA.

"HEEDAYA, HEEDAYA, HEEDAYA" Ya shiga kwaɗawa HEEDAYA kira da ta saka gabanta ko kallon sa bata yi ba cak HEEDAYA ta tsaya ba tare da ta waiwaya ko furta wata kalma ba.

"Sa'an wasan ki ne ni, ina miki magana za ki wofantar da ni? Hajja tana ciki?" Ya tambaya a harzuƙe rai a ɓace. HEEDAYA kai ta shiga girgizawa ba tare da ta juyo ba.

"Ni kike ba amsa da kai HEEDAYA bakin ki aikin mai yake? Na ce Hajja tana ciki?"

"Uhm-uhm" Ta bashi amsa a ciki-ciki da sauri Umma da Hajiya Aisha suka dafe ƙirji jin HEEDAYA ta bada amsa idanu suka zaro cike da fargaba! Tun da cikin sharaɗi ko uhm an ce kar ta yi. Daga haka sai suka ganta ta je ta haƙa rami ta binne layar ta tashi ta bar wajen. Daga nan ya saka yatsa a kan ƙwayar hoton bidiyon da suke kallo ya ɗauke.

"Ai na faɗa muku sai dai in sharaɗi aka ƙetara amma mu idan muka yi aiki babu makawa sai aiki ya ci sai dai in mai aiwatar da aikin ne ya samu akasi wajen aiwatarwa"

"Bata faɗa mana ba ko kaɗan kawai dai mun ji ba a ɗaur auren da ita ba" Umma ta faɗa cikin sanyin murya sai yanzu take jin haushin kanta na zargin laifin sa ne ashe dai HEEDAYA ce ta

kwaɓa musu aiki.

"Ai dama ba za a ɗaura da ita ba tun da ta ɓata aikin, amma da a ce bata ƙetara sharaɗi ba to da yanzu da igiyoyin auren sa uku ras a kan ta da yanzu kuna can kuna shagali da shirye-shiryen kai ta ɗakin ta, don babu wanda zai yi musu ko ya furta wata kalma marar kyau dangane da auren kawai za a fasa ne da ƴar uwar ta a ɗaura da ita" Ya faɗa hankali kwance.

"Kai amma yarinyar nan ta jiƙa mana aiki amma a mana wani ƙoƙarin mana, ba yadda za a yi yanzu a yi kwaskwarima?" Hajiya Aisha ta tambaya da zummar matsawar za a musu gyara a lamarin su samu cikar burin su ta ɗauki nauyin biyan duk yawan kuɗin da zai yanka musu.

"Aikin gama ya gama sai dai wani aikin da ban sai dai iya bincike na, na hangi akwai aure tsakanin ta da shi ABDUL ɗin tabbas ko ba yau ba akwai ranar da aure zai ɗauru tsakanin su su zauna a matsayin ma'aurata sai dai ban san yaushe ne ba kuma a ina ba ne" Shiru duk suka yi suna nazarin kalaman sa sun shiga ruɗani to yaya haka zai faru kuma yaushe ne hakan zai faru? Bayan su kan su sun san HEEDAYA da RABEEYA ba za su taɓa auren miji ɗaya ba saboda haramcin hakan ko dai yana nufin ABDUL ɗin ne zai saki RABEEYA ya auri HEEDAYA amma in haka ne ai kwaɗon ya yi yawa, kwamacalar ta isa haka gaskiya ba ma haka bane akwai dai wata maƙarƙashiya a gaba wacce basu san wace iri ba ce sai dai sun sanya a ransu cewa za su jira wannan rana!. Wannan suka ringa rayawa a rayukan su kafin suka masa sallama bayan sun jimƙa masa maƙudan kuɗi suka tafi a kan cewa idan buƙatar hakan ta taso za su sake dawowa, amma dai za su zubawa sarautar Allah ido su jira zuwan ranar da ya ce tana zuwa.

Lokacin da suka dawo su Abba basu dawo ba, cikin gidan suka tasamma. A farfajiya suka ci karo da Hajja tsohuwa mai shegen rangwangwan ɗin tsiya.

"Zainabu, Zainabu" Hajja ta shiga kwaɗa mata kira kamar za ta ari baki dakyar Umma ta lallashi zuciyar ta ta amsa tare da juyowa.

"Yanzu Zainabu ni ɗin kike wa magana getsetse kamar wata sa'arki fisabilillahi ina uwar mijin ki amma saboda ba uwarki ba ce" Ta faɗa tana kama haɓa.

"Haba Hajja kin kira ni na amsa to ya kike so na miki ko sunkuyawa zan yi ki hau in goya ki"

Salati Hajja ta kwasa tamkar an yi gagarumin wani abu ta ce

"Oh in da ranka ka sha kallo wannan zamani ai na haifa miki miji na gama miki komai ko zagina ma kya iya yi" Juyawa Umma ta yi za ta tafi don Hajiya Aisha tuni ta shige ta bar ta ga mutane suna ɗan wucewa jefi-jefi.

"Au Allah tafiya kika yi Zainabu kika bar ni ina zuba tamkar kin kunna rediyo"

"Wai mai kike so da ni ne Hajja? Ki bar ni da abin da yake damuna mana haba da wanne zan ji" Umma ta faɗa a zafafe tamkar za ta yi kuka don duniya ta rasa ina za ta saka ranta ta ji daɗi komai gani take ya kwaɓe.

"Allah baki haƙuri dama ɓangaren ki na je zan miki barka da arziƙi na auren ƴarki RABEEYA da aka ɗaura na samu bakya nan shi ne zan tambaya ina kika tafi"

'Wannan tsohuwa da tsinannan sa ido take ko ina ruwan ta da inda na tafi"

"Gudawa nake na tafi asibiti"

"Ayyo! Ko da na ji ki ce babu lafi... Bata gama jin mai za ta ce ba ta juya da sauri ta tafi ganin Hajiya Baturiya uwar amarya ta fito daga part ɗin ta sanye cikin wani dakakken leshi sai wani annashuwa take irin ta farin ciki, ita kuwa Umma ji ta yi kamar ta je ta shaƙe ta ma kowa ta huta.

A falo ta samu Hajiya Aisha da Aunty Hafsa suna magana, ga mutane nan sai abinci suke ci suna hira. Bugunzum-buguzum ta zo ta wuce ba tare da ta ce wa kowa ƙala ba ta nufi hanyar bedroom ɗin ta ranta yana mata suya. Ƙofar ta banka da ƙarfi ta shiga tare da maidawa ta rufe. HEEDAYA da take kwance fuska sharɓar da hawaye jin an buɗe ƙofa ta zabura haɗe da tashi ta sakko daga kan gadon ganin Umma ta nufi Ummar tana fatan samun wani daddaɗan labari da zai faranta mata ya tsamo ta daga dogon nutson da ta yi a cikin kogin tunani da damuwa.

"Umma!" Ta faɗa fuska a shagwaɓe tare da nufo Ummar. Umma da take cike da haushi da baƙin cikin abin da HEEDAYA ta yi na jiƙa musu aiki wajen ƙetara sharaɗi na ƙarshe a aikin bayan sai da ta yi kowanne cikin bin umarni amma sai da aski ya zo gaban goshi ta ɓata musu.

Umma sai da ta bari HEEDAYA ta zo gabanta ta ɗaga hannu ta zabga mata mari a ganin ta hakan zai rage mata raɗaɗin da take ji a ranta...

Wasa farin girki😅🙌

MAMAN AFRAH
09013181851

[2/12, 12:52 PM] MOM MASHKUR & AFRAH:
https://chat.whatsapp.com/F7TUZezpOWLKYnyTNFuy2Y

BONONO

(RUFIN ƘOFA DA ƁARAWO)

NA

MAMAN AFRAH

First Class Writer's Asso.📝

*SADAUKARWA*

Daga farko har ƙarshe sadaukarwa ne ga MARYAM SANI HAFIZ (Merry tah) Alkairin Allah ya kai gare ki Allah lulluɓe rayuwar ki da tarin ni,imomi da albarkatu Allah raya mana Abdallah fatan alkairi.

Daga marubuciyar:

Ruɓaɓɓiyar igiya
Ƴan adaidaita sahu
Ungozoma
Ƴar zaman wanka
Ƙara'in inna delu
Beelal
Jalli joga
Da sauran su.
*09013181851*

PAGE 7

*HUSNA*

Zaune take a tangamemen falon ta sanye take cikin riga da wando wanda suka kama jikin ta, sun yi matuƙar mata kyau! Duk wata sura ta ƴa mace ta bayyana kasancewar ta mai cikar halitta da duk wani abu da namiji zai buƙata ta mallake shi. Sauke idanun ta ta yi daga kallon TV take ƙarewa kanta kallo tana jinjina irin kyan da ta yi don kawai ta birge mijin ta wanda a ƙalla yau wata biyu kenan bata saka shi a idanun ta ba, kullum yana yawon garuruwa wanda a koyaushe yake faɗa mata cewa bussines ɗin sa ne yake sanya shi tafiye-tafiye. Waya ta ɗaga ta duba ƙarfe biyar da ƴan mintina na yamma amma bai samu ƙarasowa ba daga Lagos ɗin da ya ce zai taho. Ta yi nisa a cikin tunanin makomar rayuwar auren ta sai ta ji ƙaran buɗe get ɗin gidan kafin ƙwaƙwalwar ta ta gama saɓunta mata tunanin dalilin buɗe get ɗin, ƙaran dirin motar ya tabbatar mata da cewa mijin ta HAMEED ne ya iso. Duk da akwai damuwa a zuciyar ta amma sai ta ji wani sanyi a ranta ko ba komai dai ta san za take ganin mutum a kusa da ita tun da ita bata taɓa haihuwa ba sai ƴan aikin gidan kawai da suke kai kawo. Da sauri ta nufi window ta leƙo ai kuwa ta hangi direba ya buɗe masa ƙofa bayan ya fito ya rufe ƙofar. Ganin ya nufo part ɗin da ɗan hanzari ta shiga sakkowa daga saman domin tarɓar sa tana fatan kuma kada ya mayar mata da murnar ta cikin ta. A tsakiyar falon ta cim masa, tun kan ta ƙarasa sakkowa take sakin murmushi sai dai ganin ya cunkushe fuska, duk da ta ji babu daɗi na ganin yanayin sa amma haka ta ƙarasa gaban sa tana ƙoƙari rungume shi amma ya ja da baya tamkar ya ga wani abun tsoro, yana kuma ɗaga mata hannu saroro ta tsaya tana kallon sa dama ta san wannan rubutaccen abu ne yana kallon ta tamkar ya ga kashi a daidai nan direba ya shigo masa da jakar kayan sa amma ganin direban bai sa ya yi sassauci ga abin da yake son faɗa ba.

"Sau nawa zan ce miki bana son wannan al'adar turawan baki san irin waɗannan ɗabi'un lalata tarbiyar yara yake yi ba, yanzu idan kika saba da wannan ɗabi'un ba za ki fasa yi ba ko da mun haifi yara kin ga kenan yaran mu za su taso suna koya!." Ya ƙarasa faɗa a harzuƙe direban jakar ya ajiye da girmamawa ya juya ya fita. Kallon sa na tsaya yi tamkar na ga sabuwar halitta ina rayawa a zuciyata.

'Shin sai yaushe ne zan fita daga wannan baƙin ƙangin? Shin sai yaushe ne HAMEED zai faranta raina a matsayina na matar sa mai ya sa ya gwammace kullum yake nuna mini kansa a tukunya yake bai waye ba amma yanayin sa da yadda yake gudanar da al'amuran sa ya nuna shi wayyayyan mutum ne, amma ba ya son ko kaɗan ya nuna hakan a kaina ya fi so kullum ya yi fatali da duk wani abu da ya shafi auratayyar mu.

"Haba HAMEED yau tsawon wata biyu ban sanyaka a idona ba, shin laifi ne don na tunkare ka, ko kewar ka da na yi a matsayina na matarka ka bari in ji ɗumin jikin ka" Ta furta tamkar ta yi kuka saboda takaici da kuma yanayin yadda ya nuna.

"HUSNA!. Sau nawa kike so in faɗa miki ni bana son irin wannan rayuwar turawan ko so kike kullum nake biya miki kamar karatu sannan ne za ki haddace wane ne ni? Mai ya sa ku mata a koyaushe bakwa tsayawa ku yi tunanin halayyar abokin rayuwar ku, mai ya sa bakwa amfani da

kalmar nan da bahaushe yake faɗin in an san halin mutum sai a ci maganin zama da shi?" Ya kai ƙarshen maganar yana mata wani kallon rainin wayo.

"Su turawan wasu mutane ne da ban? Su turawan sun fi mu son farantawa junan su ne da suke halayyar ai a ganina don ma'aurata sun yi wani abu a tsakanin su hakan ba yana nufin laifi ba ne tun da komai aka gabatar matsawar bai saɓawa addini ba to halal ne...

"Idan kuma ya saɓawa al'ada fa?" Ya katse mata hanzari da jefa mata wata tambaya da take ganin da yin tambayar da rashin ta duk uwar uban su ɗaya.

"Baki da amsar tambaya ta, abubuwan da kike sun saɓawa al'adar malam bahaushe kuma wannan ɓata tarbiyar yara ne iyaye suke rungume -rungume ko sunbatar junan su matsawar ba a lokacin kusantar junan su ba wato a keɓantaccen wuri"

"HAMEED, da addini da al'ada wanne ne a gaba?" Bata jira cewar sa ba ta ɗora.

"A cikin gidan nan daga ni sai kai sai ƴan aiki, shin mun haihu ne da za ka fara maganar ɓata tarbiyar yara...

"Ya ishe ki HUSNA, mai ya sa kike uzzurawa rayuwata? Daga shigowata gida ko hutawa ban yi ba kin tsare ni da yawan magana to ki dakata!. Ni HAMEED ba ni da lokacin ɓatawa" Yana kai wa nan ya wuce ya bar ta baki sake, sama ya haura ai kuwa bata daddara ba ta take masa baya. Sai dai kamar yadda ya saba hakan ya mata yau ma yana shigewa ɗakin sa ya banko ƙofar tana zuwa ta tura ƙofar ta ji ya saka mukulli ya kulle. Jingina ta yi da ƙofar tana jin yadda zuciyar ta take suya tana jin yadda ruwa ya taru a kwarmin idanun ta, ta rasa sai yaushe ne za ta yi farin ciki kamar yadda kowace mace take yi a gidan mijin ta sai yaushe ne HAMEED zai sauke nauyin haƙƙin ta matsayin ta na matar sa ita duk wani jin daɗi da mace take samu na dukiya da sauran abubuwan more rayuwa a gidan aure ta mallake su, babu abin da HAMEED ya rage ta da shi idan ta ce komai tana nufin komai da komai, sai dai a cire abu ɗaya wanda shi ne ginshiƙin aure kuma shi ne kashi saba'in cikin ɗari na aure wato HAƘKI duk abin da yake na haƙƙin aurataýya ne to ita bata san shi ba duk abin da yake kulawa ce daga namiji ga matar sa sai dai ta ji a labari ko wajen ƙawaye ko ta karanta littafin hausa kai ita har bata son kallon film saboda duk inda take ganin ana soyayya ko ba mace kulawa wanda ita ta rasa sai ta ji hankalin ta ya tashi sai ta ji da tana da ikon sauya HAMEED da ta sauya shi amma kash!.

Ta daɗe a jingine a ƙofar tana jin sa har ya shiga bayi ya daɗe kafin ya fito hakan ya mata alama da wanka ya yi, bayan wasu mintuna ta fara jiyo dirin maganar sa da alama waya yake. Kunne ta ƙara kasawa a jikin ƙofar.

"Haba Baby ni ma ai ban ce na gaji da ke ba, ke kin sani bakya taɓa ginsa ta a rayuwa iya magana da taushin kalaman ki kaɗai sun isa ki janye alakar duk wani ɗa namiji da yake jin kansa domin ke ta daban ce" Waɗannan kalaman ne ta jiyo su a cikin dodon kunnen ta, wanda ta ji shigar su tamkar tafashashshen ruwan zafi a hankali cikin sanyin jiki ta bar jikin ƙofar

dakyar take ɗaga ƙafafun ta har ta sakko ƙasa a ɗaya daga cikin kujerun ta yi wa kanta masauki, tare da saka hannuwan ta biyu ta rufe fuskar ta hawaye masu ɗumi suka ci gaba da wanzuwa a dakalin kyakkyawar fuskar tata.

'Sai yaushe ne? Mai na rasa a halitta? Wane irin gyaran jiki ne bana yi? Tsafta kwalliya tatttali tsara kalamai duk don in ja hankalin mijina, duk wani abu na gyara da mace za ta buƙata don gyaran auratayyar ta ina yin sa amma sai dai ban yi dace da mijin ƙwarai ba. Shin dama duk matar da mijin ta bai damu da ita ba bata da wata dama a wajen mijin ta? Duk namijin da hankalin sa yake kan matan waje matar sa ta gida bata dame sa ba? Duk haɗuwa da ladabi da biyayyar ta? Mai ya sa matan irin mazan nan suke tamkar duwatsu ko bishiyoyi a cikin gidajen su? Mai ya sa suke rayuwa tamkar ba ma'aurata ba kuma duk gyaran da za su yi basa birge mazajen su, sai ki ga macen marar aji marar galihu wacce ma kina mata kallo ɗaya za ki mata kallon raini wacce bata ma kai su yi ko da gaisuwar fatar baki da namijin ba saboda rashin kamun kai da aji amma sai ta ɗauke masa hankali, shin kowace macen ce take fama da irin ciwon ko kuwa ita kaɗai ce?' Ta shiga rattabowa kanta waɗannan tambayoyin duk da har yanzu zargin sa take bata tabbatar da cewa yana neman matan ba amma dai abubuwa da dama suna mata kama da hakan. Ai shi ba dutse bane kuma ba icce ba ne da za a ce matarsa bata dame shi ba, to don mai aka y auren, tun da yana da lafiya amma kullum maganar sa ɗaya ce shi yana da raunin sha'awar mace ne, wanda tana ganin amsar nan tashi rainin wayo da rainin hankali ne kawai.

Duk da ta san mafi yawan maza kashi casa'in cikin ɗari basa zama ba tare da suna da ƴan mata ko zawarawa ba, tun da kowane namiji ƙarya yake ya ce bashi da budurwa ko bazawara sai dai in munafurtar matar yake, kai ko da a ce akwai su a cikin mazan to basu da yawa, sai dai ita irin yadda yake banzantar da ita ya yi yawa irin yadda yake waya da sauran su da wasu mazan ya sha bamban kuma irin yawan tafiye-tafiye da yake ya yi yawa kai ko da a ce yana tafiyar ai kamata ya yi yake yi da ita in ba zai yi ba aƙalla idan ya dawo ya tarayraye ta ya bata kulawa tare da sauke haƙƙin ta amma ina!.

Wasu daga cikin ƙawayen ta mazajen su matafiya ne wasu aiki mijin yake wasu kuma kasuwanci amma yadda mazajen su suke ma'amala da su ya sha bamban da yadda HAMEED yake a ko yaushe kuma duk daɗewar da za su yi ba ya kewar ta ko nuna ya damu da nisan tazarar da ya shiga tsakanin su tsawon tafiyar da ya yi. Waɗannan abubuwan su suke ci mata tuwo a ƙwarya kuma su take son samu bakin zaren su duk da bata so ta tsawaita zargi kasancewar zargi haramun ne, amma ya zame mata dole, kuma ya zama wajibi ta yi karatun ta nutsu domin ta gano bakin zaren domin ta gano irin binne tan da yake yana nuna mata shi kawai dai bai damu da mace ba ne, shin idan bai damu da mace ba a kan mai zai aure ta ya kawo ta gidan sa ya turke ta ya kasa sauke nauyin buƙatar ta ya bar ta da buƙatar sa danƙare a zuciyar ta, kenan da ita da marar aure basu da bambanci? A yau dai ta yi wa kanta alƙawari ko shi ne ƙuda wajen ƙwawa sai ya bata haƙƙin ta ko don magungunan da ta bankama.

HAMEED bai tashi fitowa ba sai da aka kira magriba, tana sallah ta ji fitarsa da alama

masallaci ya tafi, da sauri ta fito daga ɗakin ta, da ƙullin maganin tada sha'awa na maza da ta siya wajen wata mai maganin mata, da kuma na ƙarfin maza ta nufi ruwan shayin da take dafa masa mai ɗauke da lifton da kayan ƙamshi maganin ta zuba ta gauraya ta dawo ta ajiye a ɗakin nata. Ta san duk runtsi sai ya sha shayi da dare yake kwanciya, ko da ba zai ci komai ba, a tea flask ta juye ta ɗakko kayan abincin ta jera a dining kan kujerar ta koma ta zauna tana jiran dawowar sa. Sai da aka yi isha'i ya shigo da murmushi a fuskar sa ta amsa masa sallama wani haɗe rai ya yi don ya san zancen gizo bai wuce na ƙoƙi wato dai za ta zo masa da buƙatar auratayya ya san ta da jaraba shi ne take ta washe baki shi kuma gaskiya bacci ma yake son yi.

"HAMEED ya za ka haura sama ga abinci na jera a dining?" Ta jefa masa tambayar ganin ya nufi sama gadan-gadan. Kamar ba zai amsa ba sai da ya ƙara tafiya sannan ya tsaya ba tare da ya juyo ba ya ce.

"Bana jin yunwa" Yana gama faɗar haka ya juya zai ci gaba da tafiya. Gabanta ne ya faɗi jin furucin sa, hankalin ta ya tashi saboda ko yanzu marar ta ta fara ciwo, saboda maganin da ta sha, duk da ta san ko da ya bata haɗin kai ba ya bari ta samu biyan buƙatar ta don ba ya ɗaukan wani lokaci amma dai a ƙalla za ta samu sassauci don ita bata cikin matan auren da suke neman maza a waje ko kuma yin lalata da wasu mazan ta waya don biyan buƙata ko ma neman jinsi da jinsi wato lesbian ko kuma biyawa kai buƙata duka ba al'adarta ba ce.

"Shayin naka fa?" Ta furta a ɗan diririce don bata taɓa zaton zai ce ba zai ci abinci ba.

"Ki kawo mini ɗakina" Yana faɗar hakan ya tafi ba tare da ya jira cewar ta ba. Wata nannauyar ajiyar zuciya ta sauke tare da nufar dining ɗin ta ɗauki shayin da ƙofi da kuma kwalin sugar sai tea spoon da nascafe a kan ƙaramin faranti ta haura saman.

Abin mamaki a kulle ta tarar da ƙofar zuciyarta ta danne ta ƙwanƙwasa, da ya buɗe maimakon ya bata hanya ta shiga ɗakin sai ya miƙo mata hannu alamar ta bashi. Ɗan dim ta yi ta ce

"Ina son shigowa na zuba maka, kuma fa ko ƴar hira bamu yi ba da ka dawo"

"Bana buƙata, kuma ina buƙatar hutu bana son yawan hayaniya" Bata ce komai ba ta miƙa masa ya karɓa haɗe da rufo ƙofar. Juyawa ta yi tana ta mamaki duk da ya ci a ce zuwa yanzu ta saba da halayyar HAMEED ɗakin ta ta nufa ta zauna tana zaman jiran zuwan sa tun da mai maganin ta ce da kansa zai neme ta ƙaryar namiji ya sha maganin nan ya iya bacci ba tare da ya buƙaci mace ba don haka sai ra zauna ta zuwabawa sarautar Allah ido tana jiran ta inda HAMEED zai zo tana son gane mai maganin ƙarya take ko kuwa maganin yana aiki bata yi asarar kuɗin ta ba?!.

*MARYAMA*

Gabaɗaya ta rasa inda za ta saka ranta da furucin da Inna ta yi a kanta, wai ita MARYAMA take ɗauke da ciki, cikin ma na haihuwa to a ina kuma ta yaya tun da ita dai babu wani namiji da ya taɓa riƙe ko da hannun ta ne bare kuma har ta samu ciki. Sai dai idan ana shan cikin a cikin ruwa wannan kuwa. Sai dai ganin Baffan ya yanke jiki ya faɗi hankalin ta ya yi mummunan tashi ta nufe shi za ta dafa shi sai dai Inna Tasalla ta saka hannu ta ture ta, Maimunatu ma da ta ƙaraso wurin hankali tashe tana zuwa ta ƙara hangazata sai da ta faɗi wanwar.

"Kar ki kuskura ki ce za ki taɓa mini ubana!. Kuma ki sani duk abin da ya samu mahaifina ki yi kuka da kan ki banzar bazara kawai ai dama tsintacciyar mage bata taɓa mage" Maimunatu ta kai ƙarshen maganar tana jefa mata harara. Hawaye ne suke sintirin zubowa daga idanun ta duk da tana cikin ruɗin furucin Inna na cewa tana ɗauke da juna biyu, duk da tana kokwanton kasancewar hakan amma sai dai  tashin hankalin ta ya fi ruɓanya da faɗuwar Baffan ta tausayin sa game da jin haushin kanta sun taru sun mata rubdugu a zuciya ganin ita ce silar shiga damuwar sa duk da ba laifin ta ba ne ita ma bata san hawa ba bare sauka.

"MARYAMA!" Baffa ya kira sunan ta yana miƙa mata hannu alamar ta kama hannun sa. Da sauri ta taho tana kiran sunan sa.

"Wai Malam kai yanzu duk abin da ta yi har kana da ƙarfin halin kiran ta tare da kama hannun ta?" Inna ta tamabaya tana taɓe baki haɗe da kama haɓa.

"Baffa ka ganni fa ni ma a kusa da kai" Maimunatu ta faɗa tana kama hannun da ya miƙawa MARYAMA.

"Yo ina fa zai ganki Maimunatu ai wannan jarababbiyar ta ɗauke masa hankali ni ma matar sa baki ga ba ta ni yake yi ba" Ta ce tana bankawa MARYAMA harara. MARYAMA hannun Baffa ɗayan ta kama da yake Maimunatu ta riƙe ɗayan.

"MARYAMA!. Kin ji abin da Innar ku ta ce?"

"Baffa wallahi babu abin da na aikata...

"Na san halin ki MARYAMA na san abin da za ki aikata da wanda ba za ki aikata ba sai dai yanayin yadda ta faɗi maganar ne ya daki zuciyata tunanina ko fyaɗe aka miki baki faɗa ba har ciki ya shiga, tsorata da ruɗun da na shiga don kar fa na kasa ɗaukan amanar da na ɗauka, kar fa na kasa riƙe ki da gaskiya kamar yadda na yi wa kaina alƙawari" Ya faɗa yana yin ɗan tarin da yake jin ya riƙe masa ƙirji dakyar yake yi.

"Wallahi Baffa babu wanda ya mini fyaɗe!" Ta faɗa tana hawaye.

"Ƙarya zan miki ke kin isa in miki ƙarya ba kallon ke ba ko shi Malam ɗin da ya ajiye ki bai isa in masa ƙarya ba" Inna ta ce tana  zazzaga masifa da bala'i tamkar ta ari baki.

"Maimuna je ki asibitin cikin gari ki ce ina kiran Jazuli likita"  Dakyar ta amsa masa ta tashi tana zunɓura baki kasancewar bata son aike.

"Yo ita ba da cuta ba ita da shan magani, ai ita wacce ta kwaso abin kunyar sai ta je ta kira shi, kuma wallahi matuƙar aka tabbatar da cikin nan ba za ta zauna a gidan nan ba sai dai ta san na yi, tun da ka ƙaryata ni duk inda za ka je za a faɗa maka cikin ne dai da ita, in ban da lalacewar zamani da mu a can da wani likita muka sani ko mene ne indai ana da ciki daga mun gwala idon mace mun san mene ne" Ta ƙarasa faɗa tana juyawa ta bar wajen cike da jin haushi.

MARYAMA tana riƙe da Baffa da yake yashe a wajen, ko da ta ce za ta taimaka masa ya tashi cewa ya yi ta bari. Ba a ɗauki lokaci ba Jazuli da Maimunatu suka shigo da sallama. Jazulin ne ya taimakawa Baffa ya dawo da shi kan tabarma nan Baffan ya faɗa masa abin da yake son ya yi wa MARYAMA amma cikin sirri ba ya ma so a san wane irin gwaji za a mata kar ko da ƙarya ne mutane za su zarge ta saboda yanzu kiwon mutum ake ba na dabba ba bare ita da gabaɗaya ƙauyen ido yake a kanta abu kaɗan ake faɗin ƴar tsintuwa, shegiya ce ba ta da uba! Duk da Baffan ya yi iya yin sa don dakatar da hakan amma abin ya ci tura! Duk da ya san dai daga amai ba a ce sai ciki ba amma dai furucin da Inna ta yi ya sa tana son a yi gwajin ko hankalin sa ya kwanta, duk da ya san Inna akwai kinibibi da abubuwa marar kyau sai dai ya san da wuya ta faɗi ƙarya sai dai kawai ta yi kissa.

Duk da shi kansa Jazulin ya yi mamaki kuma dai da ya ɗan duba idanun ta ya so ganin wata alama amma ya fi so ya yi gwajin ko ya tabbatar. Asibitin ya koma ya ɗakko jakar sa ta aiki ya dawo ya sanya MARYAMA ta yi fitsari ya gwada da PT abin mamaki da ruɗu PT ya nuna layi biyu raɗo-raɗo alamar tabbas akwai ciki!. MARYAMA jingina kawai ta yi da bango tana salatin annabi S.A.W a ranta amma ita kanta ta rasa duniyar da take. Baffa kuwa ƙirjin sa ya masa nauyi yana ji a ransa wannan ne ajalin sa don ba zai iya zama ya rayu da ganin wannan abin kunyar ba. Jazuli jinin ta ya ɗauka ya koma lab na asibitin amma sakamako yana fitowa nan ma ya ga tabbas da cikin!. Cikin tsawon watanni uku.

Tun da aka tabbatar da cikin MARYAMA ta rasa sukuni a rayuwar ta jaraba da masifar Inna su ne suke ci mata tuwo a ƙwarya uwa uba rashin lafiyar da ta samu Baffa ta sanadin sakamakon samun cikin ta.

A wani daren alhamis ta lallaɓa zuwa ɗakin Baffa wanda cutar ta kwantar da shi don numfashi ne kawai yake aiki a jikin sa.

"Baffa ban aikata komai ba wallahi, ka yarda da ni" Ta furta tana kuka marar sauti hannayen ta cikin nashi ta sani bata da wani uba bayan shi bata da wasu dangi bayan shi bata da mai so da ƙaunar ta sai shi hasali ma ƙyamatar ta ake saboda ba a san asali da tushen ta ba. Cikin muryar sa da bata fita sosai ya kira sunan ta, sai da ta kara kunne ta a bakin nasa take iya jiyo abin da yake faɗa.

"MARYAMA"

"Na'am Baffa"

"A cikin akwatin ƙarfen can ta saman lokata, akwai ledar Viva wannan ledar tana ɗauke da kayan jariri da zanin goyo da wani ƙaramin zoben azurfa, a ranar da na tsince ki a bakin ruwa a ƙarƙashin bishiya shekaru goma sha takwas da suka wuce, kina sanye da kayan a jikin ki zobe a babban yatsan ƙafar ki shi kuma zanin kina kwance a kan shi an lulluɓe ki da ɗaya gefen zanin. A lokacin muna ƙauyen Mai tsamiya inda aka ƙyamace ki wasu suna cewa ba ta hanyar aure aka haife ki ba shi ya sa aka jefar da ke, tun da a lokacin ko cibiya ba a yanke miki ba. Gabaɗaya ƙauyen aka ɗora mini karan tsana wasu suna faɗin ba tsintar ki na yi ba ni ne na yi wa wata cikin ta kawo mini ke shi ne na yi wannan ƙaryar, shi ne farkon husumar da Tasalla ta tada a kan cewar sai na mayar da ke inda na ɗauke ki saboda na ɓata musu suna, kuma ta san cewar tsintar ki na yi. Goggon ki Shafa ta riƙe ki hannu biyu. Maganganun da suka karaɗe ƙauyen shi ne ya sa muka bar can muka dawo nan. Har yadda ya kai kika fara wayo da sauran abubuwan da idanun ki suke gani na tsangwama daga mutane har kawo yau. Ni kaina MARYAMA har yau ban san wa ya haife ki ba ban san asalin ki ba shin iyayen ki suna raye ko sun mutu Allah ne masani sai dai ba na jin akwai wasu iyaye da za su wofantar da abin da suka haifa tsawon lokaci har yau basu neme shi ba. Na ajiye kayan can a matsayin tarihi har sai ranar da nake saka rai wato bayyanar iyayen ki ko wani daga cikin dangin ki in nuna su a matsayin shaida sai dai kash! Ɓullowar wannan mummunar al'amari jikin ki MARYAMA ya sa na cire rai daga rayuwa don a yadda nake ji yanzu ba na jin zan iya wayar gari da numfashi a jikina, na sani baki aikata ba ko qur'ani zan iya dafawa a kan shaidar ki MARYAMA amma kuma haƙiƙanin gaskiya ban san ta ina ne hakan ya faru ba don ba a samun ciki sai an yi tarayya mace da na miji amma ke ta yaya haka ya faru? Ki yi haƙuri da rayuwa da yadda rayuwa za ta ƙara juya miki a bayan raina tabbas na san za ki shiga ƙalubale da tashin hankali amma Allah yana tare da ke MARYAMA kuma in sha Allah ina ji a jikina watarana za ki haɗu da dangin ki za

ki yi farin ciki" Tun da ta kara kunnne ta a jikin bakin sa take jin maganganun nasa tamkar bugawar guduma yadda suke shigar ta suna dukan ƙirjin ta da duk wata gaɓa ta jikin ta, tashin hankali marar misali ya ziyar ce ta. Da sauri ta saki hannayen sa ta rungume shi tana faɗin.

"Baffana kai kaɗai ne dangina kai nake so kar ka tafi ka barni wallahi ban aikata ba" Kuka take da iya ƙarfin ta, har Inna da ta fito fitsari daga ɗakin ta da jiyo kukan nata wani uban tsaki ta ja don babu abin da take ji sai haushin su daga MARYAMAR har Malam Nuhun. A duniya babu halittar da ta tsana sama da MARYAMA ita ce farkon wacce ta saka ake mata gugar zana a duk inda ta saka ƙafa ana mata bita da ƙulli dukan kabarin kishiya.

"Ba zan taɓa yarda ba dama MARYAMU akwai dai wani ɓoyayyan al'amari wanda ni da ke bamu san shi ba, sai dai na san watarana za ki san ko mene ne na san a lokacin ƙasa ta daɗe da rufe idanuna amma ki saka a ranki na yarda da ke" Yana gama faɗar maganar nan sai ta ji ya fara kalmar shahada, da iya ƙarfin ta ta dage tana faɗin

"Kar ka barni Baffa" Sai dai jin daga kalmar shahadar da ya yi bai ƙara cewa uffan ba sai ji ta ɗif kamar an yi ruwa an ɗauke, jin jikin sa ya saki ta ɗago da sauri tana kallon fuskar sa ta hasken fitilar da take ajiye a gefen sa, idanunsa a rufe ruf tamkar mai bacci. Jijjiga shi ta shiga yi da iya ƙarfin ta a ƙoƙarin ta na ganin ya farfaɗo don tana fatan ya zamana suma ne ya yi ba mutuwa ba...

*HEEDAYA*

Dafe da kuncin take kallon Umma wacce ranta yake suya tamkar ƙosai a ruwan tafashashshen mai. Sai huci take tamkar wata zakanya.

"Umma!. Laifin mai na miki da har na ci hukuncin duka? Baki tausayawa halin da nake ciki ba na yin ɓarin makauniya da ƙaddara ta yi da burina amma kike ƙara mini maimakon na samu sasaauci daga gare ki, duk a tunanina ma tafiyar da kuka yi kun samo mafita amma da alama saɓanin haka aka samu shin ga mari ga tsinka jaka Umma da wanne zan ji?" HEEDAYA ta faɗa tana kafe Umma da rinannun jajayen idanunta wanda a halin yanzu ma suke cike taf da hawaye.

"Ke kika cuci kan ki HEEDAYA ke kika wofantar da burin ki, ke ce dai kika saka ƙafa kika yi fatali

da ɗaurin auren  da ya so hawa kan ki a yau" Umma ta faɗa a harzuƙe tana nuna ta da yatsa. Dummm gabanta ya bada wani sauti ta ƙara shiga wani gararin wanda ya fi wanda take ciki muni da fargaba. Furucin ya yi tsauri bai kamata ko ana sharri ba a ɗaura mata ko a ɗaura alhakin laifin a wuyanta ta san da cewa muddin akwai wani mahluƙi da zai so cikar burinta to ko waye shi bayanta zai bi, tun da ita ta san irin gwagwarmayar da faɗi tashin da zuciyarta take fama da shi a kan ƙaunar Ya ABDUL.

"Kin san gabaɗaya na zargi cewa aikin ne ba a yi daidai ba, ashe dai ke kika karya sharaɗin shi ya sa aikin bai yi ba, da yanzu an daɗe da ɗaurawa da ke sai dai yanzu bakin alƙalami ya bushe" Umma ta faɗa idanun ta suna kawo ruwa. Da sauri HEEDAYA ta dafa kafaɗar Umma, Umma duk da ta so tankwaɓar da hannun HEEDAYA amma sai ta tsinci kanta da kasa hakan.

"Umma wane sharaɗi na karya kuma wallahi duk yadda aka ce haka na y...

"Babu wani nan HEEDAYA kin yi wa Daddyn ABDUL magana"

"Wallahi ban masa magana ba" HEEDAYA ta faɗa hankali tashe duk ta ruɗe, don ita bata ɗauki uhm-uhm ɗin da ta ce masa a matsayin magana ba bare har ta yi zaton za ta karya sharaɗi.

"Na ga komai a wajen boka tamkar muna nan aka yi uhm-uhm ɗin da kika faɗa ita ce ummul aba'isin komai ai na faɗa miki ko uhm kar ki sake ki ce"

"Na shiga uku na ɓata aikina da kaina ya za a yi yanzu Umma?" Ta tambaya tana zaro idanu tana jin ina ma ana mayar da hannun agogo baya da kuwa ta sauya wannan abin da ta yi sai dai kash aikin gama ya gama.

Hajiya Aisha ce ta turo ƙofar ta shigo. Bakin gadon ta ƙarasa ta zauna jiki sanyi ƙalau don yau dai sun faɗo ƙasa wanwar ga shi sun iyo gayyata ta fitar hankali kaf ƙawaye da abokan hulɗa babu wanda basu gayyata ba ta san wuyar ta la'asar ta yi jama'a za su fara musu dafifi ga kayan rabo da suka yi kamar ba gobe sai dai ta san za a zo a tarar da su jingum-jingum indai ba dariyar yaƙe za auke yi ba ta san da wuya fuskar su bata fallasa asirin zuciyar su ba. Amma tana fatan taro ya watse ba tare da matsalar da suke ciki ba ta bayyana kanta.

"Babu yadda za a yi" Umma ta faɗa tana tahowa ta zauna kusa da Hajiya Aisha tare da sakin ajiyar zuciya.

"Wallahi ba da son raina ba haka ta faru Daddyn ne da shegen faɗa a hakan ma dakyar na tsira da na san hakan da na yi zai ɓata aiki wallahi da ko kashe ni zai yi ba zan ce komai ba" Ta faɗa tana dawowa inda suke ta kifa kanta a cinyar Hajita Aisha tare da fashewa da matsanancin kuka. Bubbuga bayanta Hajiya Aisha ta shiga yi tana lallashin ta.

"Ki yi haƙuri boka ya ce akwai aure tsakanin ki da ABDULHAKEEM" Hajiya Aisha ta faɗa cikin lallashi. Da sauri HEEDAYA ta ɗago tana kallon ta da alamar son ƙarin bayani gabanta tana faɗuwa ta ce.

"Ta yaya? Bayan an ɗaura masa da Aunty RABEEYA ko sakin ta zai yi?" Ta tambaya.

"Mu kan mu bamu da amsar tambayar nan HEEDAYA haka dai ya ce kuma shi kansa bai san yaushe ne ba amma ya tabbatar mana da haka" Shiru ta yi tana nazari tare da son gano bakin zaren da kuma manufar bokan a kan furucin nasa sai dai ƙwaƙwalwar ta bata hasaso mata komai ba.

"Yanzu ki tashi ki koma ɗakin ki, sannan ki saki jiki ki cigaba da aiwatar da al'amuranki cikin natsuwa kar ki yarda a fahimci akwai damuwa a tare da ke bare har magauta suke tunanin baƙin ciki kike da auren" Hajiya Aisha ta ce

"Wallahi ba zan iya ba ba zan iya ɓoye damuwata ba hakan ma ƙarfin hali ne kawai amma dai ko kaɗan ba zai ɓoye ba dama bahaushe ya ce labarin zuciya a tambayi fuska" HEEDAYA ta faɗa tana tashi ta haura kan gadon ta kwanta rubda ciki. Ranta tana ƙuna tana jin yadda son Ya ABDUL yake ta safa da marwa a tsakanin birnin zuciyar ta.

Ƙaran wayar ta ne ya dakatar da ita. MEEMA ce ƙawarta ɗagawa ta yi.

"HEEDAYA wai kina ina ne halan baki ji sanarwar ɗaurin auren nan ba, shin baki san kwaɓar ki ta cika da ruwa ba"

"Na sani MEEMA duk wanda suka zo domin gayyatar da muka musu wato ƙawayen mu ki ce musu bani da lafiya ina kwance na samu bacci" Tana jin MEEMA tana ƙoƙarin magana amma ta datse kiran tare da jifa da wayar a kan gadon ta cigaba da kukan zuci wanda ya fi na zahiri ciwo da suka a zuciya.

Da yamma taro ya yi taro ko ta ina mutane ne, gida ya cika da jama'a amarya RABEEYA nemab duniyar nan ta yi wa HEEDAYA amma bata ganta ba hasali ba wayarta a kashe har Ya ABDUL ma sai da ya tambaye ta ganin jiya duk inda suka saka ƙafa a wajen kamu sai ta ɗora tata amma yau kamar an yi ruwa an ɗauke. Su Umma ma sai yaƙe suke yi wa baƙin su amma kana ganin su ba haka aka so ba wai ƙanin miji ya fi miji kyau!.

Sai da dare aka fara riɗin tafiya kai amarya, amarya ta shirya cikin shiga ta alfarma, Aunty Hafsa da baki ya ƙi rufuwa ita ce mai taya ta komai kuma ta ji daɗi da aka ɗaura auren da ita duk da ta ga HEEDAYA da Umma har ma da Hajiya Aisha suna fushi da ita amma wannan mai sauƙi ne wai cire wando ta ka, hatta Ihsan ma sai wani cin magani take Mubashshar ne ma yana wajen Abba. Naeema sai shiga ake ana fita ita da Momma har sai da dare ya yi suka tsagaita lokacin ana ta fafutukar kai amarya. Amarya da addu'a aka shigar da ita tafkeken gidan ta wanda ya ji kaya kamar ba gobe sai ƙamshin turaren wuta ɗan mai duguri ne ya cika ko ina. Kowa ya watse aka bar amarya ita kaɗai hatta ƙawayen amarya babu wanda ya zauna.

An bar ta ita kaɗai zaune a tsakiyar luntsumeman gadon ta tana ta addu'a a zuciyar ta haɗe da godiya ga ubangiji da ya nuna mata wannan rana mai matuƙar tarihi a rayuwar ta. Duk da tana ta mamakin yadda aka rako ta ɗakin ta ba tare da masoyiyar ta HEEDAYA ba don a wani ɓangare na zuciyar ta ma tana jin babu daɗi ganin bata ga HEEDAYA ba.

Za ku ji mun shigo da sabbin fuskoki ckn labarin mu, to kowa da rawar da zai taka a ciki, da sannu zan ke feɗe muku biri gar wutsiya kun san dai taken alƙalamin MAMAN AFRAH ba ya rubuta shirme📝😍

MAMAN AFRAH
09013181851
[2/13, 9:10 AM] MOM MASHKUR & AFRAH: https://chat.whatsapp.com/F7TUZezpOWLKYnyTNFuy2Y

BONONO

(RUFIN ƘOFA DA ƁARAWO)

NA

MAMAN AFRAH

First Class Writer's Asso.📝

*SADAUKARWA*

Daga farko har ƙarshe sadaukarwa ne ga MARYAM SANI HAFIZ (Merry tah) Alkairin Allah ya kai gare ki Allah lulluɓe rayuwar ki da tarin ni,imomi da albarkatu Allah raya mana Abdallah fatan alkairi.

Daga marubuciyar:

Ruɓaɓɓiyar igiya
Ƴan adaidaita sahu
Ungozoma
Ƴar zaman wanka
Ƙara'in inna delu
Beelal
Jalli joga
Da sauran su.
*09013181851*

PAGE 8

*MARYAMA*

Amma duk jijjigar da take masa babu alamun ko motsawa zai yi lamarin da ya ƙara saka ta shiga tashin hankali, gabaɗaya ta firgice tana kukan tamkar ranta zai fita. Inna da ta fito daga bayin da ɗaki za ta shige amma jin kukan MARYAMA ya tsananta sai ta ƙara jan tsaki tare da nufar ɗakin Baffan a nufin ta ta koro ta daga ɗakin don a tunanin ta, jikin sa ne ya matsa take ta faman maganganun nan da kuma kukan. Sai dai ganin kansa ya langaɓe gefe bata bi ta kan MARYAMA ba ma nufar sa ta yi ƙirjin ta yana bugawa ta shiga dudduba shi sai dai abin da ta gani ya mugun ɗaya mata hankali domin kuwa ta tabbatar da cewa rai ya yi halin sa, don har dafara ta fito masa. Wani kuka ta fashe da shi tana kiran sunan sa MARYAMA ita ma ganin hakan ta tabbatar Baffa ya yi bankwana da duniya mutum ɗaya tamkar da miliyan a wajen ta, masoyin da duk duniya bata da kamar sa. Maimunatu da take bacci tun tana jin kukan su sama-sama har ya zamana ta buɗe idanun ta da sauri ta fito daga ɗakin Inna, ta nufi ɗakin Baffa inda a can take jiyo kukan da ya karaɗe gidan tamkar gidan makoki, duk da zato da tunanin ta bata taɓa kawowa Baffa mutuwa ba duk ta zaci jikin sa ne ya matsa sosai sai dai tana zuwa ta yi mugun gani wanda aka haɗu da ita aka cigaba da kokawa.

"Shegiya baƙar ƙaddara annoba, mai mugun hali maciya amana, kin kashe mini uba kin ji daɗi dama ke shegiya ce baki da shi uban, tashi ki fice a ɗakin tun da babu ƙwandalar ubanki a wajen gina ɗakin" Maimunatu ta faɗa cikin muryar kuka tana jin kamar ta rufe ta da duka.

"Ta sa baƙin cikin, ɗan gaba da fatihar da ta samo ya yi ajalin sa wallahi kin cuce mu MARYAMA haƙƙin Malam ba zai barki ba" Inna ma ta faɗa cikin kukan tana jan hanci. Dakyar ta iya miƙewa jiri yana ɗiban ta jin ta take tamkar ba a raye take ba ji take tamkar a wata duniyar ta daban take, ɗacin da magagin mutuwar Baffa haɗe da zargin ita ce silar mutuwar sa ya taru ya haɗe mata.

Ko gabanta bata gani haka take jefa ƙafafun ta, ɗakin Goggo ta nufa wanda ya kasance makwancin ta ita kaɗai a yanzu a baya kuma kafin mutuwar Goggo tare suke kwana a ɗakin. Tana shiga ɗakin ta durƙushe a wajen tare da sakin kuka mai cin rai, ta sani tabbas cewa kuka ga mamaci ba alkairi ba ne, ba a hana kukan mutuwa ba amma irin kukan nan da ake iface-iface ana an mutu an lalace babu kyau sam!.

Tana daga ɗakin tana iya jiyo sautin kukan su Inna, ita kuma tana daga ɗakin nata tana yi wa Baffa addu'a da nema masa gafarar ubangiji sai dai ta kasa dakatar da zubar hawayen ta. Tana jin ƙaran buɗe ƙofar gidan da alama fita aka yi kiran wani jim kaɗan ta ji an shigo tana iya jiyo muryoyin maza. Ita dai bata fito ba sai doshin asuba, idanun ta sun yi luhu-luhu. Har aka shirya Baffa tana daga can ƙofar ɗakin Goggo a zaune don mugun tabon da jama'ar gari suke mata bisa jahilci ko cikin mutane bata shiga, idan kuwa ta shiga ta san tabbas ranar za ta yi ta jin baƙaƙen maganganu. Yanzu ma daga inda take matan wasu daga ciki suna jifanta da wani kallo suna taɓe baki wasu suna raɗa. Ko gawa ba a ɗauke ba amma mutane basa tuna tasu mutuwar, basu su san cewa watarana ko yau ko yanzu ma tasu tana iya riskar su.

"Iyalan mamacin su shigo su masa addu'a" Muryar liman ta katsewa MARYAMA tunani. Kamar wacce aka tsikara haka ta miƙe tsaye tana son yi wa Baffa kallon ƙarshe duk da ta san ba lallai ta samu hakan ba. Inna da Maimunatu ne sai wasu ƴan uwan sa guda biyu suka nufi ɗakin da sauri ta bi bayan su ita ma. Kwance yake sanye da likkafani har fuskar an rufe wacce ita ta so ta ƙara yin tozali da ita sai dai Allah bai nufa ba domin kuwa an gama shirya shi tsaf.

A gaban gawar ta durƙushe tana shirin fara masa addu'ar kuka ya kufce mata.

"Sanadin abin kunyar da ta jawo ne Malam ya haɗiyi zuciya ya mutu!" Inna ta faɗa cikin muryar kuka. Umarni aka mata ta tashi ta fita saboda yadda Maimunatu da Inna suke kuka suna maganganu haka ta fito jiki a saɓule ta zo ƙofar ta tsaya bayan sun fito aka ce a bayar da hanya za a fito da gawar daga can gefe ta tsaya hannunta ɗaya a tsakiyar kanta, a haka aka fito da makarar da aka saka Baffa gida ya ruɗe da koke-koke Inna da Maimunatu sai riƙe su aka yi ganin kukan nasu ya zartar hankali. Bakin ƙofar gidan ta je ta tsaya tana kuka marar sauti. Tana jin yadda mata suke yi da ita a kan cikin jikin ta da kuma wai baƙin cikin ta ne ya kashe shi wai bata yi halacci ba. Tana nan tsaye har aka tafi da shi har sai da ta daina hango su, bata bar wajen ba sai da aka kawo zanin da aka lulluɓa masa.

" Kukan munafurci kike ai ki haɗa kayan ki ki san inda dare ya miki wanda kike zaune don shi

ɗin kin kashe shi kin huta, kuma sanin kan ki ne baki da gadon sa! Ai ni dama na san barewa ba za ta yi gudu ɗanta ya yi rarrafe ba, yadda ta samar da ke ta ɓarauniyar hanya shi ne ke ma kika ɗakko naki cikin za ki samar da wani ko wata ta ɓarauniyar hanyar" Inna da ta samu MARYAMA zaune a ɗaki ta faɗa mata.

"Don Allah Inna ki yi haƙuri wallahi ban san inda zan je bani da kowa kuma bani da komai" Ta faɗa cikin roƙo hawaye yana zuba don ganin ta tausaya mata amma babu wani tausayi ta ce ta bata minti ashirin ta fice musu daga gida ta tsani ganin ta. Kayanta ta haɗa ta fito daga ɗaki ta ƙarasa gaban tabarmar da su Innar suke zaune ta ce

"Inna Baffa ya ce mini in ɗauki kaya a akwaitin ƙarfen saman lokar sa"

"Ba sai ki je ki ɗauka ba indai wannan kayan ne da yake ajiye da su shekara da shekaru" Jiki babu ƙwari ta je ta ɗaukko ta fito ta saka a cikin kayan nata.

"Inna zan tafi don Allah ku yafe mini wallahi ba ni...

"Har duniya ta naɗe ba zan taɓa yafe miki ba, kin yi silar rabani da mahaifina" Maimunatu ta faɗa tana aika mata kallon tsana Inna kuwa ko kallo bata ishe ta ba sauran matan wajen ma maimakon su bada baki sai zuga suka shiga yi. Haka ta tashi ɗauke da kayan a hannun ta har ta kusa fita ta juyo tana yi wa gidan kallon ƙarshe tare da ficewa.

A ƙofar gidan ta samu maza zaune a tabarma. Haka ta wuce tana sunkuyar da kai ta nufi hanyar bayan gari tana iya hango hanyar maƙabartar daga nesa tana jin kewar Baffan ta maganin kukan ta, Baffan ta mai share mata hawaye Baffan ta mai yarda da ita mai faɗa da kowa don ganin ya kare ta amma yau an wayi gari ƙasa ta rufe masa idanu. Tafiya take a ƙafafun ta bata san ina za ta dosa ba, bata kuma san ina za ta je ba sai dai ta san ko ina za ta je dole ta yi tazara da garin don daga garin nasu da ta baro har sauran ƙauyukan waɗanda suke maƙotaka da shi duk sun san wace ce ita kuma ta san babu wanda zai yarje ta zauna masa a gida kai hatta gari ma sai an yi da gaske, can ma ana ƙyamatar ta sanadin bata da iyaye ba a san su waye iyayen ta ba bare yanzu kuma ita ce mai ɗauke da cikin!.

*HEEDAYA*

Bacci ya ƙauracewa idanun ta, ranta a ɓace yake tana jin tamkar ta zama tsuntsuwa ta je gidan Ya ABDUL ɗin ta hana su gabatar da komai ko ta samu saasuci amma ina!.

Baƙin cikin da take ji a zuciyar ta kwatankwacin baƙin ciki da ɓacin ran da wacce aka yi wa kishiya take ji a ranar da amaryar ta tare. Haka ta kwana da zulumin Aunty RABEEYA ta hau matsayin ta yanzu kam ƙiyayyar da take mata ta zama biyu don ta kusanci mijin ta yanzu zafin

yana damfare da zafin kishin Ya ABDUL da take jin hawa da sauka na farashin soyayyar sa tamkar wanda ake rura wuta haka wutar son sa take balbala a zuciyar ta so take ma ta yakice shi amma abu ya ci tura!.

Wajen ƙarfe huɗu na asuba ta ji ta kasa jure yanayin da take ciki, ji take tamkar an ɗakko dutse an ɗora a ƙarƙashin ƙirjin ta, ƙirjin ya yi mata nauyi sosai. A ƙarshe ta yanke hukuncin kiran wayar Ya ABDUL ɗin don ko ta rage zafi da raɗaɗin da take ji na kishi fatan ta a zuciyar ta shi ne Allah sa dai babu wani abu da ya wakana a tsakanin ma'auratan biyu!. Don ko da su Umma suka ce bokan ya ce akwai aure tsakanin ta da Ya ABDUL sai ta ji ta ƙara ɗora rai a kansa duk da kasancewar sa miijn ƴar uwar ta kuma da a ce tana da iko da ta dakatar da komai don a jira lokaci a jira ranar da zai zama nata mallakin bata so ko kaɗan ya kusanci wata ƴa mace matsawar ba ita ba ce.

Cikin dakiya da rashin gudun abin kunya ta ɗaga wayar ta kamo sunan sa ta shiga doka masa kiran.

A can gidan amarya kuwa bayan komai ya gama wakana tsakanin su, cikin farin ciki da annashuwa kowa ya yi murna da kasancewa da abokin rayuwar sa Ya ABDUL sai albarka yake sanyawa Aunty RABEEYA  ita kuma duk kunya ta dabaibaye ta ji take tamkar ƙasa ta tsage ta shige ciki saboda nauyi da kunyar sa. Ganin dosowar asuba sai ya ce su je su yi wanka, da to ta amsa masa tana shirin sakkowa daga gadon sai ji ta yi an yi sama da ita, hannu ta sanya ta rufe idanun ta gabaɗaya kunyar sa take ji bata san dai ko don ranar farko ba ce kuma a daren farko amma dai ji take tabbas za ta dawwama da kunyar sa. Ruwan ɗumi ya haɗa ya saka ta a ciki ta gasa jikin ta. Sannan suka gabatar da wankan tare kamar yadda annabi S.A .W ya ce yana da kyau ma'aurata su yi wanka a tare hannayen su suna gwauraya a ruwan. Kasancewar tana ta jin kunya ta ƙi sakin jiki da shi, sai ta riga shi gana alwala ta fito daga bayin ta bar shi zai yi alwalar.

Towel ne ɗaure a jikin ta sai wani ƙarami da ta naɗa a kan nata tana tsane ruwan. Wayar Ya ABDUL da take ajiye a gefen bed side drower ta hanga tana kawo haske tana ɗaukewa har ta banzantar da wayar ganin ba hurumin ta ba ne, kuma dai ta san an ce duba wayar miji tamkar mace tana yankan albasa ne wato tana gani idanun ta yana hawaye don ba lallai abin da za ta gani ya zama mai farantawa ba ita kuwa ta daɗe da sanyawa ranta cewa babu ita babu binciken wayar miji kamar yadda ta ji ana labarin wasu suna yi har a yi faɗa a kan hakan wasu har igiyar auren su ake tsinkewa ta sanadiyyar hakan shi ya sa ta ga maganin kar a yi to kar a fara.

Har hasken wayar ya ɗauke sannan ta juya wardrobe tana son samu kayan da za ta sanya a jikin ta, amma sai ta ƙara ganin wayar ta kawo haske a karo na biyu, a wannan karon sai ta kasa haƙuri ta nufi wayar ba don binciken wanda yake kiran ba sai don son ta ga mai kiran sabon ango a wannan lokaci.

'Ko dai Ya ABDUL yana da wasu ƴan matan ne shi ne suke kiran sa watakila bai sanar da su ya yi aure ba' Wani sashen na zuciyar ta ya kissima mata hakan.

"HEEDAYA" Shi ne abin sa ta gani yana yawo akan screen ɗin wayar, gabanta ne ya yi mummunar faɗuwa tana ji a ranta anya lafiya kuwa? Sannan dama zuciyar ta tun jiya take cike da zulumin rashin samun wayar HEEDAYA kasancewar a kashe, sannan tana ta mamakin yadda ba ta zo kawo amarya ba, ta yi kewar ta, tabbas za ta so a ce ita HEEDAYA ta kira saboda ta san ta fi Ya ABDUL kewar ta sai dai zulumin kiran na lafiya ne kuwa shi ne abin da ya fi ɗaga mata hankali.

"Mene ne" Ta tsinkayi muryar Ya ABDUL ashe har ya fito daga bayin ya zo bata sani ba.

"HEEDAYA ce fa take kiran ka"

"Kuma mene ne na ruɗewar?"

"Kar fa ko ba lafiya ba"

"Sai ka ce baki san rigimar HEEDAYA ba watakila saboda ke bata yi bacci ba yau"

"Amma a wayar ka ta kira fa"

"Kuma ke take nema ba" Ya bata amsa tare da juyawa ya haura sama ɗakin sa domin shiryawa. Shiru ta yi dai tana zulumi a zuciyar ta har wani kiran ya shigo, wayar ta ɗauka ta zauna a bakin gado tare da manna wayar a kunnen ta.

HEEDAYA wacce take jin bugun zuciyar ta yana sama da ƙasa jin duk kiran da take ba a ɗauka ba, ta fara tunanin suna can suna soyewa wanda tunanin hakan da ya faɗo mata ba ƙaramin baƙin ciki ta ƙunsa a ranta ba. Sai dai jin wannan karon an ɗaga kiran sai da ta ƙara dubawa ta tabbatar an ɗaga ɗin kafin ta kai wayar kunnen ra bayan ta sauke ɓoyayyar ajiyar zuciya. Ji take tana kewar sa sosai ji take tamkar ta shekara bata ji muryar sa ba. Idanu ta lumshe bayan ta gyara kwanciyar ta, tana jin damuwa da ƙuncin zuciyar ta yana wankewa cikin wata muryar da bata san tana da ita ba ta ce.

"Hlo Yayanah!" Aunty RABEEYA da sauri ta janye wayar a kunnen ta don yanayin yadda HEEDAYA ta yi furucin sai da ta ji wani iri da a ce ba HEEDAYA ba ce wata macen ce da ban da babu makawa za ta ce budurwar sa ce don yanayin yadda ta yi furucin ya nuna tamkar akwai wani abu a ƙasan zuciyar ta. Amma sanin HEEDAYAR ta ce sai wani murmushi ya suɓuce mata ta ce

"HEEDAYA tah" Da mugun sauri HEEDAYA ta cire wayar daga kunne ta, tare da tashi zaune gabanta yana faɗuwa don bata taɓa zaton za ta ji muryar Aunty RABEEYA ba duk da ta san za

su iya zama waje ɗaya a yanzun amma bata kawo cewa har an kai lokacin da za ta iya ɗaga kiran ba sai dai wani ɓari na zuciyar ta ya tunasar da ita cewa yanzu fa matsayin matarsa take. Wani ƙululun baƙin ciki ne ya tokare mata zuciya tabbas bata ƙara tabbatar tana da mugun kishi ba sai yanzu da ta ji Aunty RABEEYA ta ɗaga wayar Ya ABDUL a take zuciyar ta ta shiga hasko mata huton su na wataƙila ma kan Aunty RABEEYAR ma yana kafaɗar Ya ABDUL ɗin.

Wani kuka ne ya ƙwace mata wanda ta kasa iya riƙe shi.

"Auntyyyy" Ta faɗa cikin kukan, wanda a zahiri HEEDAYA ta nuna wa Aunty RABEEYA tana kukan rashin ta ne da kewar ta a baɗini kuma tana kukan kishin Aunty RABEEYAR ne.

"HEEDAYA tah mene ne wa ya taɓa mini ke?" Ta tambaya hankali tashe.

"Ba ke ba ce"

"Mai na yi kuma?"

"Tun jiya ba na samun wayar ki kwana na yi ina tunanin ki na yi kewar ki Aunty shi ne yanzu da na ga asuba ta yi sai na ce bari na kira Ya ABDUL ya haɗa ni da ke" Akiyar zuciya Aunty RABEEYA ta sauke sai yanzu ta tabbatar da cewa lafiya sannan ta ƙara tabbatar da ƙaunar ƴar uwar ta gare ta tamkar dai ba ƴan uba suke da HEEDAYA ba suna ƙaunar junan su.

",Tuba nake HEEDAYA ni ma na yi cigiyar ki har na gaji kuma bana samun wayar ki"

"Matsalar network ne ina Ya ABDUL?" Ta tambaya don ta matsu ta ji ina yake har ta ɗauki wayar kafin ya ɗauka.

"Ya fito wanka ne yana shiryawa ne da na ce masa kina kiran wayar sai ya ce ni kike nema"

'Dole sai na tashi tsaye na zage dantse kenan dai har wayar ma ta koma hannun ta? Kuma da ta ce yana shiryawa da alama wanka ya fito to ma in ba wanka na ibadah ba wankan mai za a yi da asubar farin nan?' Ta jefawa kanta tambayar a zuciyar ta.

"To Aunty ki gaishe da shi tun da na ni lafiyar ki hankali na ya kwanta" Tana gama faɗar hakan ta datse kiran ba tare sa ta jira cewar Aunty RABEEYA ba, don ba za ta iya jure cigaba da magana da ita ba wataƙila ma in aka jima tana iya jin abin da zai fi wannan ƙona mata rai. Aunty RABEEYA kuwa murmushi ne kwance a saman fuskar ta tana jinjina ƙaunar sa HEEDAYA take mata kuma ita ma haka ne a nata ɓangaren.

*BAYAN SATI UKU*

Kwance take a ɗakin ta tana ta tunanin mafita don yanzu sai ta yi kwana da kwanaki bata sanya Ya ABDUL a idanun ta ba wanda ta kasa jure hakan. So take a kullum a ce tana tozali da kyakkyawar fuskar sa mai haifar mata da nutsuwa da kwanciyar hankali. Yau kwana uku kenan rabon da ta saka shi a idanun ta tun ranar da suka zo gaishe da su Abba da daddare shi da Aunty RABEEYA yadda suka murmure suka yi wani kyai daga shi har Aunty RABEEYAR shi zau nuna maka tare da tabbatar maka suna ba juba kulawa kuma suna cikin kwanciyar hankali. Wannan abin da ta gani ya daɗa rura soyayyar Ya ABDUL a zuciyar ta, kullum abin cigaba yake a maimakon ci baya ga kishin Aunty RABEEYA da take ji yana ƙaruwa tare da nuƙurɗusar zuciyar ta. Babban abin da yake damun ta ma bai wuce yadda ta ga Ya ABDUL tun da ta yi aure shaƙuwa ta ragu a tsakanin su idan ba ƙarya idanu da zuciyar ta suka mata ba sai take ganin ma yanzu kamar ya daina son ta da tarairayar ta kawai daga asibitin sa sai matar sa ne kaɗai yake ba kulawa sai kuma iyaye.

Zuwan ta gidan sa ɗaya wansa sai da ta yi da na sanin zuwa domun mummunan angamon da idanun ta suka mata a tsakanin masoyan biyu. Amma dai yanzu so take ta samarwa kanra mafita.

"Hajja ta furta a fili tare da tashi ta ɗauki jakar ta ta saka wayar ta a ciki Umma ta sanar wa za ta je gidan Hajji baki Umma ta taɓe ta ce sai ta dawo. Abba kuwa tana faɗa masa ya yi murna da hakan jin za ta je gaishe da mahaifiyar sa. Direba ya sauke ta a ƙofar gidan na Hajja ta shiga da sallama.

"Lale marhabin da ƙawata" Hajja ta faɗa tana tafa hannu tare da yin dariya a lokaci guda. HEEDAYA ma dariyar ta yi ra samu waje ta zauna suka dasa hira bayan ta bata lemo da bakilawa da alkaki tana ci suna taɓa hira.

"Hajja wata magana nake son faɗa miki ki faɗawa Abba ni tsoron faɗa masa nake"

"Kin samu mijin ne?" Hajja ta tambaya baki washe.

"Ba wannan ba ne mijin ma yana nan zuwa in sha Allah lokaci kawai ake jira"

"Allah kawo shi amma mene ne"

"Amin Aunty RABEEYA ce ta ce mini bata jin daɗi in je gidan ta in mata kwana biyu to ina tsoron tunkarae Abba da maganar kin san halin sa"

"Ayyiri-yiri" Hajja ta carara guɗa.

"Kai na fi kowa farin ciki yo ki ce an samu ɗan baba, ai rashin lafiyar mai dalili ce kuma dole a je a taimaka mata da wasu ayyukan kafin cikin ya yi ƙwari "

"Wallahi kuwa Hajja kin san ta bata son ƴan aiki suke mata komai" HEEDAYA da maganar cikin ta doke ta duk da ta san maganar ba haka ba ce Hajja ce ta faɗa amma sai da ta ji wani iri, sannan ta san wani ƙudurin ta ne zai kai ta gidan don ita Aunty RABEEYA ma bata san da maganar ba.

"Ai Abban naku zan kira in masa jawabi"

"Barka da yamma Hajja" Abba ya faɗa bayan ya ɗaga kiran Hajja.

"Barka Bashir ya gida da iyalin"

"Kowa lafiya"

"Ma sha Allah, Allah yi albarka"

"Amin Hajja"

"Wannan yarinya RABEEYA ce bata jin daɗi shi ne ta kira ni a waya rake so HEEDAYA ta je gidan nata ta yi kwana biyu kafin ta ji ƙarfin jikin ta ka san ƙaramin ciki akwai laulayi" Shiru ya yi yana ɗan nazari ya yi mamakin da RABEEYA ta faɗi maganar nan kasancewar ta santa da alkunya amma in ya duba cewa Hajja kakar ta ce sai ya ga hakan ba komai ba ne.

Amsa mata ya yi da cewa HEEDAYA za ta je. HEEDAYA kuwa ta ji daɗi sosai don za ta cim ma ƙudurin ta ga kuma komawa kusa da masoyin ta take sanya shi a idanun ta a kullum.

Sai magriba ta baro gidan Hajja, bayan isha'i Abba ya kira ta a waya part ɗin sa ta nufa ta same shi a falo yana duba news.

"HEEDAYA mai ya samu Aunty naki?" Dumm gabanta ya buga sai dai ta yj gaggawar saita nutsuwar ta ta ce

"Abba bata faɗa mini ba sai dai ta ce mini kawai in je bata da lafiya" Bai yi magana ba ya shiya latsa waya gabanta sai faɗuwa yake bata ankara ba sai jin muryar Aunty RABBEYA ta yi tana cewa

"Ina yini Abba" Ta faɗa bayan ta yi sallama. Idanu HEEDAYA ta shiga zarawa tana jin faɗuwar gabanta yana tsananta muddin aka tabbatarwa da Abba gaskiyar magana ta san kashin ta ya

bushe.

"Lafiya ƙalau ina ABDULHAKEEM ɗin?"

"Yan lafiya Abba"

"Madalla!. Ya jikin naki?" Aunty RABEEYA da take kwance kanta a cinyar Ya ABDUL ta ma rasa abin cewa tun da ita dai ta san lafiyar ta ƙalau kuma babu wanda ta cewa bata da lafiya.

"Alhamdulillah!." Ta samu kanta da faɗa saboda bata son tambayar Abba wanda ya ce bata da lafiya kuma hakan tamkar tuhuma ce. HEEDAYA wata ɓoyayyar ajiyar zuciya ta sauke jin ba a ƙaryata ta ba.

"Gobe za ta dawo nan ɗin ai HEEDAYAR har zuwa ki samu ki warware Hajja ai ta kira ni a waya ta bani umarnin in bar HEEDAYA ta je ta taya ki zama kamar yadda kika buƙata baka jin daɗin jikin ki" Shiru ta yi don zuwa yanzu ta kasa magana ma mamaki ya kashe mata jiki.

"To Abba" Ta ce don bata san mai za ta ce ba. Sallama suka yi ya kashe wayar tare da cewa HEEDAYA gobe sai ta je. Da farin ciki ta koma ɗakin ta.

Aunty RABEEYA kuwa dakyar ta ƙirƙiri murmushin yaƙe wanda iyakar sa fatar baki, duk da ta san HEEDAYA ƙanwar ta ce amma ta yi girma ta zo suna da sati uku da tarewa ba za su sake ba idan tana nan amma sai ta danganta hakan da cewa HEEDAYA ce ta kasa jure rashin ta a gidan shi ya sa har ta ɓullo da wannan batun.

MAMAN AFRAH
09013181851

[2/16, 7:55 PM] MOM MASHKUR & AFRAH: https://chat.whatsapp.com/F7TUZezpOWLKYnyTNFuy2Y

BONONO

(RUFIN ƘOFA DA ƁARAWO)

NA

MAMAN AFRAH

First Class Writer's Asso.📝

*SADAUKARWA*

Daga farko har ƙarshe sadaukarwa ne ga MARYAM SANI HAFIZ (Merry tah) Alkairin Allah ya kai gare ki Allah lulluɓe rayuwar ki da tarin ni,imomi da albarkatu Allah raya mana Abdallah fatan alkairi.

Daga marubuciyar:

Ruɓaɓɓiyar igiya
Ƴan adaidaita sahu
Ungozoma
Ƴar zaman wanka
Ƙara'in inna delu
Beelal
Jalli joga
Da sauran su.
*09013181851*

PAGE 9

"Hayati mene ne?" Ya tambaya yana ranƙwafowa yana leƙen fuskarta da ya ga ta lunshe ido da alamar kamar an faɗa mata wani abu da bai mata daɗi ba sai dai ya san ta da zurfin ciki ba lallai ta bari ma ya fuskanci damuwar ta ba.

"HEEDAYA ce ta kasa jure rashi na shi ne ta cewa Abba za ta zo ta mana kwana biyu" Fuska ya yamutsa cike da mamaki yana kallon idanun ta da har lokacin suke a rufe sai gashin idanun da suke zare-zare sun rufe saman idanun.

"HEEDAYA ce za ta zo nan ta yi kwana biyu?"

"Eh" Ta faɗa cikin sanyin murya tare da tattaro jarumta a jikin ta ta tashi zaune tana ɗan kallon cikin ƙwayar idanun sa ta sakar masa murmushin nan da yake tafiya da shi.

"Ko baka so ta zo?" Ta faɗa tana rausayar da kai tare da ɗan jujjuya idanun ta. Dimm ya ɗan yi shi dai ya san RABEEYA da kunya iya su ma sai yana ɗan dagewa wajen ganin ta sake jiki da shi saboda matsananciyar kunyar da take da ita duk da kunyar tata tana birge, shi amma kuma dai ya san matsawar HEEDAYA za ta dawo ba lallai take iya nuna masa so da ƙauna haɗe da kulawa ba saboda alkunya ga shi a iya ɗan zaman nan ya fara sabawa da kulawar ta ba ya iya komai cikin nutsuwa matsawar bata kusa da shi sai yanzu ne ya gane rayuwar sa tana damfare da tata ne sosai yake ƙaunar ta ita ma ya fahimci hakan a tattare da ita.

"Ina son ƴar uwata" Ta furta tana kallon sa, duk da ta ji babu daɗi a ranta ganin HEEDAYA idan ta zo za ta ɗan kasa sakewa amma girman gidan ya isa su sake matsayin su na sabbin ma'aurata  sannan duk da Ya ABDUL ɗan uwa yake wajen ta kuma ta san ba zai hana HEEDAYA zuwa ba amma ya zama wajibi a wajen ta ta nuna masa muhimmancin ƴan uwanta a wajen ta don namiji ba a masa haka daga lokacin da ka nuna masa ƴan uwan ka basu da muhimmanci daga lokacin zai fara tunanin wofintar da su gwara tun farko ka nuna masa kana son ƴan uwanka.

"Ni ma ai ina son ta" Ya ce yana sakar mata murmushi haɗe da lakato dogon hancin ta. Sosai ta faɗaɗa murmushin ta.

"Gadkiya na iya kiwo dubi hatta hancin ki ya ƙara tsawo" Ya faɗa yana ƴar dariyar zolaya. Ita ma dariyar ta saki ta ce

"Kai kuma hatta bakin ka ya ƙara tsawo"  Fuska ya cukuni cikin sigar wasa ya ce

"Wato ya yi tsawo kenan nan gaba irin na jaɓa zai zama" Dariya ta yi sosai ta tashi tsaye sai da ta dubi hanyar bedroom ta ce

"Yanzu ma ai iri ɗaya ne" Tana faɗa ta gudu ya tashi ya bi bayan ta da nasa gudun amma bai cim mata ba har ta shige ɗakin nata zaune ya same a bakin gado  aikuwa ya shiga mata cakulkuli yana tambayar da na waye bakin nasa yake kama. Cikin dariyar da ta ci ƙarfin ta saboda cakulkulin ta ce

"Da nawa" Dariyar suke su duka suna jin su tamkar babu wasu masoya kuma makusanta a duniyar soyayya fiye da su. Fitilar ya kashe musu suka lula duniyar ma'aurata.

*WASHE GARI*

Tsabar farin ciki bacci sai ɓarawo ne ya suri HEEDAYA asubar fari ta cika akwati da kaya da duk wani abu da za ta buƙata. Umma sosai ta ji daɗin hakan don a ganin ta wannan ce hanya mafi sauƙi da HEEDAYA za ta hana su RABEEYAR rawar gaban hantsi ta samawa kanta gurbi a wajen Ya ABDUL ɗin tun da sun tabbatar da boka ya ce akwai rabon aure tsakanin su.

Momma kuwa tun da ta samu labarin zuwan da HEEDAYA za ta je gidan RABEEYA ranta ya yi mummunan ɓaci ta san duk abin da Abba ya zartar babu mai sauya shi amma dai tabbas ta san sai dai in wata maƙarƙashiyar ce za a shirya in ba haka ba daga yin aure sai a ɗauki zabgegiyar budurwa a kai gidan sabbin ma'auratan da ko gama amarci basu yi ba. Tana dawowa daga falon Abba don a wajen dinner ya sanar da hakan tana shiga ɗakin ta dokawa Ammie waya ta yi tana ɗauka ko gaisawa basu yi ba ta shiga faɗin.

"Wai kin ji baƙin shirin da baƙar munafukar nan ta yi?"

"Shirin me kuma?" Ta tambaya cikin rashin fahimta. Kwashe komai ta yi ta faɗa mata cikin hargowa Ammie ta luƙa wata ashariya tana ganin abin ya zo da kissa da rainin hankali don ita dai ta san ABDUL bai faɗa mata cewa RABEEYA bata da lafiya ba, sai dai in maƙarƙashiya ce aka shirya ta hana su wali tun da dai su basu san da cewa HEEDAYA tana son Ya ABDUL ɗin ba sun dai san Umma tana baƙin cikin haɗin wannan shi ne za ta yi wani abu don hana zama lafiya ko ta hana su sakewa za ta ɗauki ganɗamemiyar budurwa da ta isa a kaita ɗakin miji ta tura musu ita gida.

"Wallahi ni ma na san sai dai da wata manufa aka yi kuma ta hannun Hajja HEEDAYA ta bi ita kuma Hajjar ta kira Abban nasu ta sanar masa kin ga kenan wannan tunanin ba na HEEDAYA ba ne na uwar HEEDAYA ne ita take shirya komai.

"Dama ita ce mana, ga shi kin san dai in Alhaji ya yi magana babu sauyi babu kuma mai sanya shi ya sauya bare magana da ta biyo daga hannun Hajja kin san kuwa ba zai taɓa janyewa ba. Ƙwafa Ammie ta yi zuciyar ta na suya ta yi wa Momma sallama tana ta tunanin mafita amma ta rasa.

"Kin gama naki saura namu, kin aika musu gardiya gida don ki hana su soyewa to da sannu za ku kwashi kashin ku a hannu, in ma wani abu kike ƙullawa to ta Allah ba taki ba" Momma da suka yi kiciɓis da Momma a harabar gidan ta furta tana aika mata wani kallo. Wata dariyar rainin hankali Umma ta saki tana mata kallon uku saura kwata ta ce

"Kar wanda ya fasa duk abin da ya yi niyya, idan kuma akwai wanda zai hana to wanda ya zartar da maganar yana falon sa za ki iya zuwa ki tsawatar masa" Tana gama faɗar hakan bata jira cewar Momma ba ta juya ta bar ta a wajen tana jin tamkar ta je ta shaƙo Umma amma ba hali haka ta juya buguzum-buguzum ta nufi sashen ta.

Lokacin da HEEDAYA ta isa gidan Aunty tana kicin tana haɗa abinci  da murna ta fito suka rungume juna suna ta farin ciki. A falo suka zauna kafin Aunty ta ɗauki jakar ta ce ta zo ta rakata ɗakin da za ta zauna.

"Aunty ɗakin nan... Sai kuma ta yi shiru.

"Mai ya yi ɗakin ?"
"Kawai sai nake ganin kamar zan ke jin tsoron sa idan dare ya yi" HEEDAYA ta faɗa tana kallon ɗakin lokacin da suka shiga don a son samun ta suke kwana da Aunty RABEEYA don ba za ta juri suke shigewa ɗakin su biyu ita suna barin ta ita kaɗai.

"Haba HEEDAYA mai ɗakin kuma ya yi ke da a gida ma ke kaɗai ce a ɗakin ki" Aunty RABEEYA ta ce tana ƴar dariya.

"Shikena Aunty" Ta ce tana murmushin yaƙe.

"Wai ya aka yi kika cewa Abba bani da lafiya?"

'Don in zo in kasance inuwa ɗaya da masoyina mana, tun da boka ya yi duba ya ce akwai aure tsakanina da shi na san duk daren daɗewa dole mallakina ne, dole na matso kusa da shi kar in zauna a nesa da shi ki sa ya manta da ni' Ta faɗa a zuciyar ta a fili kuma ta ce

"Kawai ji na yi ina son zuwa wajen ki Aunty kuma na san in ban ƙirƙiri wani abu ba babu yadda za a yi in zo"

"Allah sarki HEEDAYA tah ni ma ina cike da kewarki"

"Ina Yayan?"

"Yana asibiti mana" Murmushi ta yi ta ce

"Kuma yaushe yake dawowa Aunty?" Da yamma mana"

"Kamar ƙarfe nawa?" Ta tamabaya don ta yi shirin tarɓar sa na musamman.

"Ƙarfe huɗu" Ta ce tana cewa bari ta duba tukunya a kicin. Gidan ta shiga kallo tana rayawa a ranta cewa ko sai yaushe ne za ta dawo gabaɗaya da zama ta kasance tare da masoyin ta Ya ABDUL matsayin ma,aurata don ko a ranta bata jin wani cewa haramun ne su auri miji ɗaya da ƴar uwar ta, kawai burin ta sanya a gaba da kuma tunanin jiran ranar sakamakon boka tun da ta san akwai auren bata damu da abin da zai faru har su yi auren ba duk kuwa da ta san ba za su haɗa miji ɗaya ba.

Ya ABDUL yana zaune a office yana ganin marar lafiya kiran Ammie ya shigo wayar sa ɗagawa ya yi.

"Ammie barka da wannan lokaci"

"Barka ya aiki, wai wace magana ce nake ji akan cewa HEEDAYA ta ƙaura gidan ka?" Goshi ya dafe don dama ya san sai an haɗa masa zafi, don ya san a rina wai an saci zanen mahaukaciya.

"Ba fa ƙaura ta yi ba Ammie zuwa ta yi za take taya RABEEYA aiki kin san bata jin daɗi"

"Yaushe ka koyi ƙarya yaushe ka fara ɓoye mini abu, ko har ka fara zaɓar dangin matarka a kaina?"

"Haba Ammie ba haka bane"

"To yaya ne ai ga shi nan ni dai da bakina ban taɓa ji ka ce tana rashin lafiya ba" Shiru ya yi don ya rasa ma mene ne mafita.

'Gaskiya auren zumunci cakwakiya ne' Ya ce a zuciyar sa a fili kuma sai ya ce.

"Ki yi haƙuri Ammie"

"Kawai ka yi takatsan-tsan don na san wannan yarinyar ba yin kanta ba ne zuwa wannan gidan ka san dai yadda muke da uwar ta, kuma ban da ma rashin hankali HEEDAYA ce mai zuwa gidan Allah kyauta" Bata jira cewar sa ba ta kashe wayar ajiyar zuciya ya sauke ya cigaba da aikin sa.

HEEDAYA tun da ta ga ƙarfe uku da wani abu ta shiga ta yi wanka ta ɗauro alwala ta fito ta shirya cikin silky doguwar rigar da duk ta kama jikin ta sallah la,asar ta yi jin an fara kira, ta ɗakko turare ta shafa lokaci guda ƙamshi ya haɗe jikin ta.  Kallon kanta ta yi a madubi ganin haɗuwar da ta yi wani murmushi ta yi ta fito ta zauna a falo tana danna waya. Aunty RABEEYA da ta shiga ɗakin ta yi sallar la'asar ra fito tana sanye da riga da skirt na atamfa sun amshi jikin ta. Da kallo ta bi HEEDAYA ganin ta sauyo kaya ta yi kwalliya tamkar mai shirin zuwa gidan biki ga wani ƙamshin turare da ya haɗe falon.

"Wannan gayun fa ko fita za a yi" Ta faɗa cikin tsokana.

"Wanka na yi fa Aunty kuma wannan kwalliyar ai Ya ABDUL na yi wa" Ta faɗa da wasa tana dariya. Dumm gaban RABEEYA ya buga duk da ta san HEEDAYA da wasa ta yi maganar amma sai da ta ji faɗuwar gaba tare da jin babu daɗi a ranta. Amma sai ta hau neman tsari da shaiɗan mai sanya wasi-wasi son ta san sharrin sa ne .

"Ai kuwa yana dab da dawowa" Ta ce ita ma tana dariya tare da wucewa ta je tana jera masa kayan abinci a dining. Da wani kallo mai cike da harara HEEDAYA ta bi Aunty a fakaice ba tare da ta bari ta gani ba, don ganin yadda ƙugun Aunty RABEEYAR yake juyawa a cikin skirt ɗin bare Aunty RABEEYA mai hips sosai saɓanin HEEDAYA da take shafal.

Suna zaune suna ɗan taɓa hira wayar  RABEEYA ta yi ƙara a ɗaki tafiya ta yi tana dubawa ta ga Momma. Bakin gado ta zauna tana amsa kiran bayan sun gaisa.

"Da baki kira kin faɗa mini ba ai na ji"

"Mai Momma?" Ta tambaya cikin sanyi murya.

"Ban sani ba, wai ke mai ya sa RABEEYA kamar wata nusara kike yanzu HEEDAYA ce za ta ƙaura gidan ki amma kika saki baki shameme kike zaune"

"To ina zan je Momma, kuma HEEDAYA fa ƙanwata ce sannan shi ma Ya ABDUL ai ba bare ba ne ɗan uwanta ne sannan ma Abba ne fa ya ce ta zo kin...

"Ya isa haka RABEEYA sau nawa zan faɗa miki ƴan uba kuke da HEEDAYA ni kuma kishiyoyi muke da uwar ta kuma ba zaman lafiya ba ne a tsakanin mu a kan mai za ki yarda ta zo ta tare miki a gida ai da Abban naku ta kira da kin sanar masa cewa kin ji sauƙi ba sai ta zo ba" Ta faɗa a harzuƙe.

"To Momma za a kiki gaba"

"Kar ma a koka" Ta ce tana datse kiran. Ajiyar zuciya ta sauke tare da tashi ta saka wayar a caji. Fitowa ta yi a daidai lokacin kuma Ya ABDUL ya shigo falon ɗauke da sallama a bakin sa. Da ɗan gudu HEEDAYA ta nufe shi tana masa oyoyo tana zuwa ta kama hannun sa ɗaya da yake ɗayan yana riƙe da jakar wajen aikin sa. Aunty RABEEYA da ta ƙaraso tsakiyar falon sai suka zame mata hoto jin shaiɗan yana neman kissima mata jin kishin ƙanwar ta sai ta yi saurin kawar wa tare da ƙirƙirar murmushin yaƙe wanda iyakar sa leɓanta, ta sani cewa HEEDAYA tana iya kama hannun Ya ABDUL a baya duk da ba muharramar sa ba ce amma tun sabon yarinta har yanzu bata daina ba, amma ta ɗauka tun da ya yi aure yanzu ita ma kuma ta mallaki hankalin kanta za ta daina sai dai kuma ga shi bata daina ba.Yana ƴar dariya yana kallon HEEDAYA don shi ko kaɗan bai kawo cewa hannun sa da HEEDAYA ta kama zai ƙona ran Aunty RABEEYA ba.

Ganin ta yi turus a gefe ɗaya sai ya ce

"Yau ba oyoyo Hayati?" Ya ce yana jifanta da wani kallon wanda ya sa fuskar HEEDAYA

sauyawa tamkar dai mijin ta ne ya yi wa kishiyar ta kallon, hatta sunan da ta ji ya kira Aunty RABEEYA da shi sai da ya sosa ranta ta ji babu wanda ya dace ya kira da sunan sama da ita.

"Oyoyo sannu da zuwa" Ta faɗa da baki tana dariya a maimakon da tana zuwa sai ya rungume ta amma yau ga shi an samu sauya sai ya fara tunanin ko ganin HEEDAYA ne ya sa ta ƙi masa hakan.

"Na ƙi wayon" Ya ce yana ƙoƙarin janye hannun sa daga riƙon da HEEDAYA ta masa amma sai ya ji ta ƙi saki kallon ta ya yi sai kuwa ta saki hannun nasa, wajen Aunty RABEEYA ya nufa yana sanya hannu ya janyo ta tare da maƙalo ƙugunta ɗaya hannun riƙe da jakarsa.

"Mu je ki haɗa mini ruwan wanka" Ya ce yana kallon fuskar ta. Bata masa musu ba don ta ji daɗin yadda ya nuna kulawar sa gare ta hakan yana nufin zai iya nuna soyayyar sa gare ta a gaban kowa tuni ta shagala da cewa HEEDAYA tana wajen. Sama suka haura har lokacin yana riƙe da ƙugunta ita kuma ta ɗan kwantar da kanta a gefen kafaɗar sa. Tun da suka nufi matakalar benen take kallon bayan su ranta yana matuƙar suya tana ji tamkar ana watsa mata ruwan barkono a idanun da take kallon su. Har suka ɓacewa ganin ta tana tsaye a wajen tamkar an dasa dutse. Hawaye ne suka shiga sintiri a fuskar ta da gudu ta yi hanyar ɗakin da aka sauke tana zuwa ta faɗa kan gado tare da fashewa da kukan baƙin ciki da kishin da ya cika mata zuciya. Tana tunanin wataƙila ma yanzu sai sun yi wani abu kafin ya yi wankan, tana ganin ta zo gidan don samun warakar abin da take ji a zuciyar ta ashe dai ta zo inda za a ke fama mata ciwon ne...

*MARYAMA*

Tana tafiya gabaɗaya jikin ta ya mata nauyi saboda mutuwar Baffa ga damuwar rashin sanin takamaiman inda za ta je, sannan ma uwa uba abin da za ta tarar a inda za ta je ɗin. Tana tafiya tana haɗuwa da mutane waɗanda suke tahowa don zuwa wurin mutuwar wasu a ƙafa wasu kuwa a mashina. Wasu mata da ta haɗu da su tana ji da za ta gifta su suna cewa an ce ita ce silar mutuwar mariƙin nata baƙin cikin, abin da take ɗauke da shi ne ya sa ya haɗiyi zuciya ya mutu!. Wannan furucin nasu ya tabbatar mata da cewa zance har ya fara yawo daman yaɗa jita-jita ai ba ƙaramin abu ba ne ga mutane bare kuma ƙaramin ƙauye da ko ina dama ba wani tazara ne da garin nasu ba.

Ta wuce gari uku kenan a ƙafafun ta ga gajiya zuwa yanzu dakyar take ɗaga ƙafafun ta sai ɓaƙogwaron ta da ya bushe saboda buƙatar ruwa don ita bata ji ko abinci za ta iya sakawa a bakin ta saboda mutuwar mahaifin ta. Tana dab da shiga ƙauye na huɗu ta ga wasu yara suna ɗaukan ruwa a famfo ta ruƙi su bata ruwa za ta sha, a marfin bokiti wani yaro ta taro ya miƙa mata karɓa ta yi sai dai tana kurɓa ta ji ɗaci ruwan kawai Baffa ne a ranta hakan ya ta ji wani

kuka ya taho mata ruwan ta watsar ta miƙa musu marfin ta ce ta gode ta cigaba da tafiya. Tana dab da fita daga garin can ƙarshen garin ganin wani tsohon gini na asibiti ganin magriba ta yi kuma babu mutane wajen da yake ƙarshen gari sai wani gida da ta gani daga can gefe shi kaɗai. Cikin asibitij ta shige duk sai ƙura kasancewar ma duk an ciccire windoji da ƙofofin haka ta shiga wurin ta ajiye kayanta sai kuma tunanin yin sallah ya faɗo mata don babu sallar da ta yi ba azhar ba la'asar ga yanzu magriba ta yi. Tsoron kar a ganta duk da bata zaton garin za su iya sanin wace ce ita tun da akwai tazara sosai da ƙauyen su tun da gari uku ne a tsakani sai shi ƙauye na huɗu. Tana zaune a kan kayan nata ta dafe fuskarta da hannu biyu kuka take marae sauti ji take tamkar ta koma ƙauyen su ta yi tozali da kabarin Baffa kewar sa take ji sosai tana jin ciwo da raɗaɗin rashin sa. Tabbas!. Shi ne gatan ta ga shi yau ɗaya da ba ya raye har ta fara maraici ta shiga wani hali wanda ko wurin zama ya gagare ta hasali ma bata san ina za ta je ba haƙiƙa idanun sa ma mashi ne tun da ga shi idanun sa suna kawa har ta yi ban kwana da gatan da take jin ya rage mata a duniya.

'Mai ya sa? Mai ya sa aka haife ni a haka? Mai ya sa mahaifiyata ta samar da ni ta makauniyar hanya? Ashe tana tsoron abin kunya amma ta yadda ta same ni ba ta hanyar aure ba, amma duk wanda ya sayi rariya ya san za ta zubar da ruwa. Shin mene ne laifina? Yanzu ga shi ni ban san ba ma shin tana raye ko ta mutu? Idan tana raye mai ya sa ta haife ni bayan bata sona shin ta jefar da ni, ina mahaifin nawa? Su duka basa buƙatata, bani da laifin komai bani na zaɓi zuwana duniya ta wannan hanyar ba amma mai ya sa nake girbar abin da ba ni na shuka ba?. Bayan waɗannan abubuwan ga wata ɓoyayyar ƙaddarar da ban san ta yaya ta wanzu a jikina ba, ya aka yi nake da ciki ba tare da na yi zina ba? Ko wannan yana cikin biyan bashin da iyayena suka ci na zina? Dama ko baka kusanci namiji ba kana iya samun ciki anya? Ko dai a kaina ne hakan ta faru ga rashin Baffa wayyo ni!. Tabbas ni kaina tausayin kaina nake' Ta ƙarasa faɗar hakan a zuciyar ta wani kukan tausayin kanta yana ƙwace mata ta shiga rera shi a fili ba tare da ta shiryawa hakan ba.

"Waye a nan?" Ta tsinkayi ana tambayar ta wata faɗuwar gaba ce ta ziyarce ta da sauri ta saka hannu ta damƙe bakin ta da hannu biyu tana zare ido ta cikin ɗan duhun magribar da ya fara yi wa wajen ƙawanya...

MAMAN AFRAH
09013181851
[2/16, 7:55 PM] MOM MASHKUR & AFRAH: https://chat.whatsapp.com/F7TUZezpOWLKYnyTNFuy2Y

BONONO

(RUFIN KOFA DA ƁARAWO)

NA

MAMAN AFRAH

First Class Writer's Asso.📝

*SADAUKARWA*

Daga farko har ƙarshe sadaukarwa ne ga MARYAM SANI HAFIZ (Merry tah) Alkairin Allah ya kai gare ki Allah lulluɓe rayuwar ki da tarin ni,imomi da albarkatu Allah raya mana Abdallah fatan alkairi.

Daga marubuciyar:

Ruɓaɓɓiyar igiya
Ƴan adaidaita sahu
Ungozoma
Ƴar zaman wanka
Ƙara'in inna delu
Beelal
Jalli joga
Da sauran su.
*09013181851*

PAGE 10

*HUSNA*

Tana nan zaune amma babu alamar HAMEED zai fito daga ɗakin bare har ta saka ran za ta samu biyan buƙata sai dai bata karaya ba domin kuwa a ranta tana tunanin ko dai maganin ne bai gama bin jikin sa ba bare har ya fara masa aiki. Hakan ya saka take zaune tana danna waya wtsapp ta shiga ta buɗe group ɗin nan nasu wanda iya matan aure ne kawai a ciki, duk wata mace wacce ba matar aure ba ko ta shiga waje ake yi da ita, shi ya sa ma kana shiga group ɗin za ka ci karo da dokokin group ɗin wanda waɗanda suka san su ƴan mata ne ko

zawarawa ma suna ganin dokokin suke fita daga group ɗin shi ya sa ma yawanci duk sai ta dalilin wasu ake shigowa ma'ana sai kina da ƙawa a cikin group ɗin sannan idan za a saka ki sai kin bi ta hannun admin ta tsare ki da tambayoyi kamar ba gobe shi ya sa ma sun fi yin adding da wuya su fitar da link. MANYAN MATA shi ne sunan group ɗin.

Saƙonnin ta hau duddubawa kamar kullum don bata yarda ta bar saƙonnin group ɗin MANYAN MATA bata buɗe ba saboda abubuwan da ake gabatarwa a ciki. Hirar da ta ga ana yi ce ta ƙara mata damuwa a kan wacce take ciki, don dama matan group ɗin basu da aikin da ya wuce bankaɗa sirrin mazajen su da yadda kowacce take samun tarayraya da kulawa a wajen mijin ta wannan shi yake ci wa HUSNA tuwo a ƙwarya domin ita a wajen ta babban abu ne tun da ba samu take yi ba abu ne mai wahala shi ya sa ma ko hira ake sai dai ta ja gefe tana karantawa tana mamakin dama akwai irin waɗannan mazan a duniya amma mai yasa ita bata yi dace ko gam da katar na samun irin su ba? Tana alaƙanta hakan da cewa ƙaddarar ta ce haka sannan ita bata iya ƙarya ba wato ta zauna tana yabawa haɗe da koɗa miji a kan kulawar sa gare ta tun da ta san ba samu take yi ba.

Ta yi nisa a cikin karanta saƙonnin kafin ta ga kowacce tana yin sallama a kan cewa babyn ta yana buƙatar kasancewa da ita haka kowa ya watse admin ta kulle gidan ya koma only admin can send message. Hakan ya sa ta sauka ma daga whatsapp ɗin gabaɗaya ta ajiye watar tare da sauke nannauyar ajiyar zuciya, tagumi ta yi da hannu biyu tana tuna ita sai yaushe ne za ta samu waraka daga wannan damuwar gidan auren nata kowacce mace tana jin daɗi da kasancewa kusa da mijin ta amma ban da ita abu babu marmari koyaushe cikin wannan matsala shin sai yaushe ne za ta yi ban kwana da damuwar rashin kulawar miji? Ko a haka za ta ƙare rayuwar ta cikin ƙunci. Tun tana zaune har ta fara gyangyaɗi bacci ya soma awon gaba da ita a zaunen ba tare da HAMEED ta ji ko da ƙaran buɗe ƙofar ba ne bare har ya zo da haka ta zame ta kwanta wani ɓarawon bacci ya yi gaba da ita.

HAMEED kuwa tun daya karɓi kayan da ta miƙo masa ya ajiye zaunawa ya yi zai tsiyaya sai kawai wayar sa ta yi ƙara ganin budurwar sa sai ya washe baki ya koma bakin gado ya zauna, katse kiran ya yi don ba ya so kuɗin ta ya tafi gwara na shi ya tafi duk da shi yake saka mata katin. Kiran ta ya yi tana ɗauka ta fashe da wani kukan shagwaɓar da ya sa ya ja filo ya kwanta yana sauraron muryar ta da take rikita duk wata nutsuwar sa. Lallaɓa ta ya shiga yi ita kuwa ta shiga kashe murya tana mashe murya ta fara masa hirar don akwai wasu kuɗaɗe da take son karɓa daga hannun sa.

"Sai in ji duk muryoyin matan duniya amon ta tamkar ƙaran jiniyar ƴan sanda suke idan suna magana, matsawar kika yi magana to fa taki tamkar busar sarewa ce" Ya ce yana wani koɗata tare da zuzutata jin haka sai ta ƙara zage dantse ta shiga masa yadda suka saba a ƙarshe suka koma video call cikin hirar banza da nuna abin da ya haramta, nan suka raba dare suna haramtacciyar soyayyar da suke ganin more rayuwa ce kuma wayewa ya manta da matarsa ta sunna da take ta faman bibiyar haƙƙin ta ma ya hana ta bayan wanda yake bi ɗin babu abin da za su nuna mata tun da babu abin da ta rage sa da shi sai dai ƴan magana suka ce abincin ƙwalama ya fi daɗi.

Hakan ya sa ya mata alƙawarurruka da dama bayan maƙudan kuɗin da ta tambaya. Yana kashe wayar ya yi wankan ibada ya yi shame-shame a kan gadon bacci ya yi awon gaba da shi ba tare da ya bi ta kan shayin da HUSNA ta sha wahala wajen dafa masa ba, tare da amfani da magani don samun biyan buƙatar ta a matsayin ta na mace mai lafiya kuma wacce bata bibiyar mazan waje ta tsare kanta.

Ko sallar asuba bai yi ba don sai wajen bakwai ya tashi shi ma kiran SUMY budurwar sa ne ya tashe shi. Ɗaga wayar ya yi yana kallon sunan ta da yake yawo a saman wayar ya ce.

'Kai sai ni HAMEED mai kala-kala mai buhu -buhun ƴan mata' Ya faɗa a zuciyar sa yana tashi zaune ya ɗaga kiran.

"Haba baby HAMEED ya haka za ka manta da ni kwana ɗaya tal fa ka ce za ka yi" Ta ƙarasa faɗa cikin shagwaɓa.

"Haba SUMY yanzu fa ƙarfe bakwai amma kuma har kin fara ƙorafi kin san dai yau ba za ta wuce ba komin dare a Lagos zan kwana" Wannan furucin ne ya sa ta ji daɗi suka gaisa cikin soyayya sannan suka yi sallama. Ajiye wayar ya yi tare da tashi ya shiga wanka ya ɗauro alwala sai da ya shiya sannan ya gabatar da sallar asuba, jakar kayan sa da ya dawo da ita jiya ya zazzage a kan gado tare da ɗakko wasu kayan a wardrobe ya shirya a jakar tashi da suk abin da zai buƙata sai kuma ƙarama mai wasu takardu. Kasa ya sakko da su. HUSNA da take kicin tana haɗa break fast sai jin ƙara gara akwati ta yi gabanta ne ya faɗi da sauri ta leƙo daga kicin ɗin, abin da ta zata ne ta gani wato jakar HAMEED shi kuma yana tsaye tana ɗaura agogo. Tsabar takaici ma ta rasa bakin magana gas ta koma ta kashe don bata ga dalilin dafa abincin ba tun da wanda take yi don shi ba ci yake ba ko na jiya da dare ma bai ci ba.

Falon ta fito zuciyar ta babu daɗi lokacin ya zauna yana waya, jim kaɗan direban da ya yi wa waya ya shigo ya ɗauki jakar ta fita da su.

"Akwai wani abu da kike buƙata a cikin gidan ne ko akwai abin da ya ƙare? Cikin kayan store mene ne babu?" Ya tambaya haɗe da ɗakko 500k ya ajiye a gabanta. Hawayen da take maƙalewa ne suka surnano mata ta ɗago ta tsare shi da idanun ta ce

"Bana buƙatar komai, akwai komai da komai, sai dai abin da na fi buƙata shi ne babu akwai shi amma bani da iko a kan sa" Ta ƙarasa faɗa muryar ta tana fallasa asirin zuciyar ta na raunin da ta yi.

"Mene ne shi mene ne ya ƙare da har kike so ai babu wani abu da baki da ikon ko nawa ne zan

siya miki...

"Kai ne HAMEED kai nake buƙatata, kai ne bani da iko, sai yaushe za ka zauna da ni a gida? Kullum kai hankalin ka a bussines babu ruwanka da ni da haƙƙina ka yi wata biyu baka nan amma ka zo ka yi kwana ɗaya ka ce za ka tafi kuma ba tare da ko makwanci ka haɗa da ni ba, shin dutse ce ni? Ko ka fi son na fara siyar da mutunci na ga wasu mazan ko kuma in fara holewa da mazan banza a socila midea...

"Wace irin magana ce wannan HUSNA sau nawa kike so in maimaita miki gida kike so in dawo in zauna kin sani da cewa kamfanina nake zuwa aiki nake ko zan fasa al'amurana ne saboda ke shin ni mace ne da zan dawo gida in zauna ai zaman gidan sai mata, ko nusarin namiji zan mayar da kaina saboda in daɗaɗawa mace? Na zo a jiya saboda da ke na dawo yau an mini waya da sassafe ana buƙatata a kamfani domin saka hannu a wasu takardu shin sai in bar komai in zauna a gida in ke soyayya shin soyayyar za mu ci?" Ya katse mata hanzari cikin hargagi. Gabaɗaya sai ta ji ranta ya ɓaci a nata ganin yana sane amma yake take gaskiya.

"Shikenan bari na shirya kayana mu tafi tun da ai kana da gida a can"

"Babu inda za ki bini wallahi, ke da kika samu ma kina ganina mata nawa ne wata sai ta shekara da shekaru bata sanya mijin a idanun ta ba kuma take zaune amma ke sai rashin haƙuri, da kike batun bamu haɗa makwanci ba jiya in ce dai a gajiye nake ko bakya duba nisan tafiyar da na yi? Ko cewa aka yi soyayya dakusantar juna ne zaman aure? Abu da zamani ma ya zo ga waya nan sai ka ji muryar mutum" Ya faɗa yana tashi tsaye sai wani muzurai yake tamkar ta zagi iyayen sa.

"Ni na tafi sai mun yi waya" Ya faɗa tana dosar ƙofar fita.

"Allah tsare" Ta furta tana ƙoƙarin danne kukan da ya taho mata. Da amin ya amsa ko a kwalar rigar sa ya fice. Da ɗan gudu ta haura sama ta je jikin window tana kallon sa har mai gadi ya buɗe musu get suka fice tana jin haushi da ciwon abin da HAMEED yake mata da a ce yana bata kulawa kuma yana karɓar kulawar da take bashi da babu dalilin da zai sa mijin ta zai yi tafiya amma bata masa rakiya ko da bakin mota ba ne.

Ɗaki ta koma bayan ta gama shan kukan ta, fitowa ta yi ta nufi ɗakin sa saboda tana so ta tabbatar da ƙaryar da mai maganin nan ta mata tun da dai ga shi bai zo ko inda take ba bare a yi batun biyan buƙata. Abin mamaki komai a yadda ta bashi a haka ta gani har ta fara tunanin ko dai HAMEED ya gane abin sa ta saka a ciki shi ya sa bai sha ba sai dai bata da wanda zai bata amsar wannan tambayar.

*HEEDAYA*

Zaman gidan Aunty ya zame mata tamkar wanda take a kurkuku domin duk abin da tw zo don

ta gabatar amma hakan bai samu ba kullum tana fito da sabbin abubuwa don jan hankalin Ya ABDUL amma abin ya ci tura saboda shi kwata-kwata ma bai fahimce ta ba kuma ta lura ba ta gabansa matar sa ce kaɗai a gabansa. Yadda suke sakewa suke nunawa junan su kulawa tamkar dai basu san an yi ta a wajen ba shi ne abin da ya saka ta kasa ko da zaman falon idan Ya ABDUL yana gidan, sai dai ta koma ɗaki ta yi ta ƙunsar baƙin ciki daga ƙarshe da ta ga ba ci satin ta guda ta haɗa kayan ta lokacin suna zaune a falo sai ganin ta suka yi da akwati niƙi-niƙi.

"Sai ina kuma?" Aunty ta tambaya da mamaki.

"Sai gida" Ta faɗa tana ƙoƙarin danne ɓacin ran da yake taso mata domin zaman ta a gidan ba ƙaramin tsanar Aunty RABEEYA ya ƙara mata ba ta ƙuduri cewar wallahi ba don ya haramta su auri miji ɗaya ba da ko ta halin ƙaƙa sai ta auri Ya ABDUL kuma ta shigo gidan ta gasa mata aya a hannu yadda da ƙafafun ta za ta bar gidan kuma da bakin ta za ta nemi saki sai dai kash! Haramcin auren ne ya sa take ɗaga mata ƙafa.

"Ga kuɗi kya shiga mota" Ya ABDUL ya faɗa cikin halin ko in kula. Kanta ta sunkuyae tana jin ranta yana suya, ta ɗauka zai ce ta bari ba yau ba ko ma ya nuna kulawarsa cewa ta bari sai da safe mana amma kamar wanda ta gundure shi kamar wanda dama yake jiran ranar tafiyar ta wai zai bata kuɗin mota.

"Haba dai ka kai ta mana" Aunty RABEEYA ta faɗa ganin kamar rashin kyautawa ne a ce ta zo tsawon sati guda amma a bata kuɗin mota.

"Ni ban san ma dalilin da zai sa ki tafi gidan yanzu ba mai ya sa ba za ki bari sai da safe ba?" Aunty RABEEYA ta faɗa tana kallon ta.

'Wato in zauna baƙin ciki ya kashe ni kina nan maƙale da mijin ki ni ina ɗaki tamkar wata mayya in dare ya yi ku shiga ku bar ni ni kaɗai dama abin da na zo yi da ban kuma na ga babu haza dole na san na yi' Ta ce a zuciyar ta a fili kuma sai ta ce

"Babu komai Aunty sai in shiga motar ko ma napep na samu sai in shiga, kawai na yi kewar Umma ne ina so na gan ta"

"Inyee wato da kika gama boarding school ɗin ba da ina za ki ganta ma " Ta faɗa tana dariya.

"Ya ABDUL ina da kuɗin mota na gode sai da safen ku" Ba tare da ta ba Aunty RABEEYA amsa ba ta juya ta nufi ƙofar fita, don kallon su liƙe da juna yana neman saka zuciyar ta bugawa. Tana jin Aunty tana kiran ta amma ta yi kunnen uwar shegu don tana buɗe baki kuka ne zai fito.

"Ka tashi ka je ka miƙa ta plss" Ta ce tana ɗan yawo da idanun ta, da to ya amsa yana cewa sai dai ta zo su je amma ta ce masa Abba ya hana yawan fita haka ya ɗauki makullin ya fito mai gadi ya buɗe get masa don lokacin har ta fice daga harabar.

Tsaye ta same ta da alama abin hawan take jira, bata zata ba bata tsammata ba sai ganin motar sa ta yi ta tsaya a gefen ta wani irin daɗi ya mamaye mata zuciya, ta ɗan juya kai gefe a ɓoye ta goge hawayen da yake mata sintiri.

Duk tsawon kwanakin nan tana so su ɗan keɓe ma da shi amma abin ya ci tura! Hannu ta harɗe a ƙirji tana jiran fa fito ta ɗan lallashe ta ko ta ji sawaba a ranta amma sai ta ji yana danna mata horn. Ɗan taɓe baki ta yi ta sungumi jakar ta saka a baya ita kuna ta buɗe gaba tana rayawa a ranta cewa w ce dai ta ga Aunty RABEEYA a gaban da kuwa sai ta ce musu su je ta hau napep. Tana zaunawa ta rufe ƙofar tare sa sakin wata bayyananiyar ajiyar zuciya, don ita yanzu gani take bata jin kunyar za ta iya bayyana masa son da take masa ko a aikace ne don ta gaji da dakon son sa tana cutuea da yawa.

"Ya ABDUL ni yanzu ban san laifin da na maka ba duk ka tsane ni sai in ga kana jin haushi na ban san dalili ba, ko dai ka daina sona ne?" Ta furta cikin wata irin murya mai sanyi tana kafe fuskar sa mai kyawun gani da ruɗa ta . Ba tare da ya waiwayo ya kalle ta ba ya ce.

"Yaushe Hayatiy ta ce miki bata da lafiya" Wani takaici ne ya turnuƙe ta tamkar ta kai masa duka ga maganar da take su tattauna kafin su isa gida a ƙalla ya ce mata.

'Haba HEEDAYA nah ina son ki mana' Amma sai ya shigo da wata magana da ban.

"Kawai dai ina son zuwa wajen ku ne" Ta faɗa kamar za ta yi kuka. Kuma ta ce wajen su ne don ita saboda shi ma ta je. Bai ƙara cewa uffan ba, ya kunna karatub qur'ani ya shiga bin karatun. Sosai ta ji haushi har tana mamaki ta rasa gane kan Ya ABDUL a auren wata ɗayan da ya yi gabaɗaya ya sauya matar sa kaɗai yake nunawa so da kulawa.

Yana tsayawa a ta buɗe ƙofar tare da buɗe bayan ta ɗauki jakar ta ko ta kansa bata bi ba ta shige gidan. Shi ma bayan ta ya bi ya je ya gaishe da su Abba ya shiga gidan su ya fito ya koma gidan sa don ba ya son yin nisa da matar sa ko kaɗan.

*BAYAN WATA BIYAR*

Yanzu gabaɗaya jikin Umma da na HEEDAYA kai har ma da na Hajiya Aisha ya yi sanyi, sun sare da lamarin da boka ya ce HEEDAYA za ta auri Ya ABDUL domin kuwa sun ga babu niyya wai ango ya kwana da wando.  Saboda yanzu Aunty RABEEYA ciki ne da ita na tsawon wata shida ga ta ƙara yin wani kyau ta yi ƙiba fatar ra tamkar ba a Nigeri'a suke rayuwa ba gabaɗaya ta sauya kowa sai murma yake mata da aamun nagartaccen miji mai ƙaunar ta da nuna mata kulawa. Umma da Hajiya Aisha har sum gaji da zuwa wajen boka amma sai ya ce musu akwai dai lokaci su jira shi ba ya taɓa gano abin da ba zai faru ba. Ba ma wannan ne damuwar HEEDAYA ba yadda Abba yake yawan tambayar ta wanda za ta fitar matsayin miji shi ne tashin hankalin ta wannan ya sa take kula samari don kar a ga kamar ta rasa ne. Ga shi aminiyar ta

MEEMA har an yi bikin ta ita RAUDA duka ƙawayen ta ne da take ganin sai ta riga su aure amma ga shi dai ta tsaya kallon ruwa kwaɗo ya mata ƙafa. Yanzu daga ita sai Ifteehal su ne dai suka rage a cikin makusantan ƙawayen nata.

Ta gaji da jiran gawon shanu don ko gida Aunty RABEEYA ta zo ta tsani ta ga cikin jikin nan nata tana jin baƙin ciki a ce ɗan jinin Ya ABDUL ne a jikin ta hakan ya sa ko ta zo gidan sai ta yi wunin ɗaki ko dai ta kaucewa duk hanyar da za su haɗu watarana kuma ta tsiri fita unguwa, bare ita dama yanzu bata ma sha'awar zuwa gidan ta tun da yanzu wanda take yi domin shi hatta wayar ta sai ya ga dama yake ɗauka kwata-kwata ya sauya tamkar daj ya san abin da yake zuciyar ta.

Kwanci tashi asarar mai rai Aunty RABEEYA ta shiga watan haihuwa, cikin ya tsufa ya mata nauyi duk ta sauya kama ga wani kumburi da har an yi ta maganin an gaji sai aka ce ba zai ware ba har sai da haihu. Gata sosai Ya ABDUL yake nuna mata tamkar dai ya ɗauke mata cikin ya mayar jikin ta ga kaya sun saya kamar za a buɗe shago da yake shi da kansa ya mata scanning a asibitin saya ga ƴa mace kwance a marar ta hakan ya sa siyayyar ta zo da sauƙi don yana ganin sun san mai za a haifa. A wata ranar alhamis da safe naƙuda mai ƙarfi ta sarƙe Aunty RABEEYA a kiɗime sula tafi asibitin Ya ABDUL duk ya bi ta ruɗe tamkar ya mayar da ciwon jikin sa haka yake ji. Sai dai haihuwa ta ƙi daɗi gabaɗaya sai wuya take sha, ga shi ƴan uwa da iyaye duk sun tare a asibitin. Dab da magriba ta samu ta haihu bayan ta sha baƙar azaba, ana ta murna Ya ABDUL tamkar ya yi tsalle saboda farin ciki ji yake bai taɓa shiga farin ciki mai tarin yawa ba kamar na yau musamman da ya ga babyn kamar ta ɗaya da maman ta. Sai dai ana cikin murna da farin ciki sai murna ta koma ciki domin kuwa jini ne ya ɓallewa Aunty RABEEYA an yj ta ƙoƙarin tsayar da shi sai dai abu ya ci tura don ana ƙara wani, wani yana fita. Tuni hankalin kowa ya tashi musamman Ya ABDUL da ya fi kowa shiga tashin hankali musamman da ya ga Aunty RABEEYA ta riƙe hannun sa cikin galabaita tana faɗin ya yafe mata tare da bar masa wasiyyar kulawa da jaririyar da ta bari don gabaɗaya ta sare da mutuwa za ta yi!.

Kuka kawai yake tamkar mace tamkar ba likita ba gabaɗaya ya fita hayyacin sa ganin hatta magana ta gagare ta shi kuma ji yake tamkar dai idan har ajalin ne zai saukar mata gwara mutuwa ta ɗauke su tare son har ya fara tunanin yadda zai rayu ba tare da RABEEYA ba a wannan duniyar!.

HEEDAYA wacce da take jin tamkar ta yi wa Aunty RABEEYA addu'ar mutuwa wajen haihuwa amma ganin halin da take ciki sai ta ji zuciyarta ta yi rauni ta ji tana tausaya mata kai har ma ta ji da za ta warke da ta haƙura da aure mata miji sai dai kash! Abin da Allah ya rubutu babu mai gogewa a wannan lokacin ne rai ya yi halin sa Aunty RABEEYA ta amsa kiran mahalicci tana mai ambaton kalmar shahada dakyar don sai dai ka gane furucin bakin ta amma ba a jin sauti ko kaɗan. Allahu akbar! Rai baƙon duniya.

Ya ABDUL sai da aka rirriƙe shi Abba da Daddy suna ta bashi baki amma ina!. Sunan ta

kawai yake ambato hatta su Abba sai da suka zubar masa da hawaye riƙe yake da jaririyar yana ta kuka tamkar ƙaramin yaro, HEEDAYA ma tausayin masoyin ta da kuma rabuwa da Auntyn ta mai ƙaunar ta tsakani da Allah ya sa ta fashe da kuka tare da rungume Ya ABDUL da babyn suna kukan tare.

Kwanan keso ta yi ana ta nema mata gafara ga mahalicci kamar yadda annbin rahma S.A.W ya ce a nemawa mamaci gafara. Da yake dama gidan Abba aka kai ta, bayan an shirya ta aka sallace ta tare da tafiya da ita makwancin ta!. Ya ABDUL wanda Allah ya dasawa haƙurin danne zuciyar sa bisa ga wannan babban rashin da ya yi shi ne wanda ya sanyata a kabarin ta.

*A gafarce ni da mutuwar Aunty RABEEYA haka labarin namu ya zo ne, sannan ita dama mutuwa a har kullum tana zuwa ne ba tare da an shirya ba. Sai dai ftn Allah sa mu cika sa imani ya mana kyakkyawan ƙarshe.* 👏😭

MAMAN AFRAH
09013181851
[2/16, 7:55 PM] MOM MASHKUR & AFRAH:
https://chat.whatsapp.com/F7TUZezpOWLKYnyTNFuy2Y

BONONO

(RUFIN ƘOFA DA ƁARAWO)

NA

MAMAN AFRAH

First Class Writer's Asso.📝

*SADAUKARWA*

Daga farko har ƙarshe sadaukarwa ne ga MARYAM SANI HAFIZ (Merry tah) Alkairin Allah ya kai gare ki Allah lulluɓe rayuwar ki da tarin ni,imomi da albarkatu Allah raya mana Abdallah fatan alkairi.

Daga marubuciyar:

Ruɓaɓɓiyar igiya
Ƴan adaidaita sahu
Ungozoma
Ƴar zaman wanka
Ƙara'in inna delu
Beelal
Jalli joga
Da sauran su.
*09013181851*

PAGE 11

*MARYAMA*

Tunanin inda za ta nufa ta gujewa haɗuwa da mai muryar da ta ji yana jefo tambayar waye a nan. Don a halin da take ciki yanzu kowa ma tsoron sa take tun da ita bata da kowa, amma ina! Babu wata hanya da za ta bi ta fita sai inda ta shigo kuma ta nan ne take jin muryar mai maganar yana nufowa, sannan matsawar ta motsa ta ce za ta koma wani ɗakin ta ɓuya to tabbas zai iya cim mata don ya riga da ya zo dab.

Hasken fitilar da ya dalle mata idanu ne ya sa ta yi tsuru-tsuru tamkar an tsamo ɓera daga ruwa.

"Wace ce ke? Kuma kukan mai kike?" Tambayar da ya guntso ya fesar mata ya sa gudun numfashin ta ƙaruwa gabaɗaya ta ruɗe ta rasa bakin magana sai wani kukan da yake taso mata, a ganin ta ta samu maɓoya amma ashe asirin ta zai tonu.

"Na ce wace ce ke?" Ko aljana ce ke?" Ya ƙara jefo mini tambayar a zafafe. Da sauri na shiga girgiza kai ina cewa.

"Mutum ce ni wallahi ba aljana ba ce"

"Me kike a nan?"

"Tafiya nake dare ya mini shi ne na zauna kafin gari ya waye in cigaba da tafiya"

Bai ce komai ba ya shiga zagaya ta yana ƙara haske ta, tare da haske kayan nata.

"Shi ne baki zauna a cikin gari ba, ko kin shiga wani gida kin nemi alfarma kika zo dokar daji

cikin tsohon ginin nan da bashi da tsaro kika zauna bakya tsoron wani abu ya cutar da ke? Ko bakya tsoron matsayin ki na mace wasu mazan su far miki?"  Kai ta sunkuyar hawaye suna zuba tun da ta tabbata maganar da yake yi ita babu wannan abin a ranta tun da ga shi ni cikin wata baiwa ta samu ciki a jikin ta ba tare da namiji ya kusance ta ba to gudun mai za ta yi?.

"Daga ina kike?" Shiru ta yi tana tunanin faɗa masa daga inda nake a ganin ta ba abin da ya shafe shi ba ne sannan daga ganin sa bai yi kama da mutumin ƙauye ba don sai yanzu ta lura ma ashe ba fitila ba ce a hannun sa waya ce.

"Suna na HAFEEZ ni mutumin garin Dutse ne ina zaune da Kakata a can sannan ni ma'aikaci ne a wannan asibitin na ƙauyan nan, wannan gidan shi ne wanda nake zaune a ciki, tun da kin baro cikin gari ki zo ki shiga akwai ɗaki ki yarda da ni ba zan cutar da ke ba kuma ki saka a ranki cewa Allah zai kare ki ko da na yi niyyar cutar da ke da safe sai ki tafi inda kika nufa" Cewar HAFEEZ mutum mai tausayi haɗe da riƙo da addini mutum ne da ya tsani zina da kuma duk wani aikin alfasha duk da kuwa bashi da aure. Idanu ta ɗaga ta shiga kallon fuskar sa ganin ya haske mata fuskar tashi alamun ta gan shi. Baƙi ne ba sosai ba irin baƙin kyau nan, dogo ne sosai yana da ɗan jiki don ba za a kira shi rammamme ba yana da faɗin ƙirji duguwar fuska da dogon hanci haɗe da kwantaccen gashin kansa da yake kwance luf kamar na mutanen ƙasar indiya, sajen sa da ake kira da kwata million ya ƙara ƙawata fuskar. Ɓoyayyar ajiyar zuciya ta sauke amma har cikin ranta sai ta ji hankalin ta ya kwanta da shi har zuciyar ta take ji ba zai cutar da ita ba!.

Ba tare da ta yi magana ba ta ɗauki kayan nata ta rungume, murmushi ya saki ganin kamar dai bata saki jiki da shi ba ya rasa ma daga ina take yanayin ta ya nuna masa tamkar tana cikin matsananciyar damuwa amma bata son ta faɗa. A gaba yake tana bin sa a baya har suka ƙarasa gidan ya buɗe ƙofar ya shiga hasken sola da ya haske gidan sannan gidan share ƙal kamar akwai mace a ciki ginin siminti ne tamkar ba a ƙauye da dama haka ake idan an gina asibiti sai a gina gidan ma'aikatan a gidan. Ciki da falo ne sai wasu ɗakunan guda uku a jere sai bayi da kuma kicin.

Ɗakin da ya nuna mata ta shiga ta zauna babu komai sai ƙaramar katifa. Da sallama ya shiga ɗakin.

"Akwai abin da kike buƙata?"

"Ina so zan yi sallah" Shiru ya yi yana bin ta da kallo yanayin ta babu nutsuwa akwai alamar damuwa, sannan kana ganinta ka san tana jin yunwa amma kuma sai ta ce sallah, ta birge shi sosai kasancewar yana lura da wasu matan ƙauye basu damu da sallah ba sannan ma ya lura ita kamar ba ƴar ƙauye ba amma suturar jikin ta ta yamushe da yawa.

"Ga banɗaki can a waje akwai ruwa" Yana faɗar hakan ya juya ya fita. Fitowa ta yi ta shiga banɗakin wanke yake ƙal sai ƙamshi ma yake tsarki ta yi ta yi alwala ta fito tana komawa ta ga sallaya a ajiye da alama shi ya kai mata sallolin ta jero ta gama ta zauna tana ta jerowa Baffan

ta addu'ar samun gafara ta gama ta shafa sai bata cire hannuwan daga fuskarta ba ta bari a haka hawayen tunanin Baffan ta yana zubowa tana ji a ranta bata san ranar da za ta daina kukan rashin sa ba gaskiya mutuwar Baffa tabo ne a zuciyar ta wanda ba zai taɓa kankaruwa ba har abada!.

Da sallama ya shiga bayan ta amsa, plate ya shigo da shi a rufe ya ajiye da cibi (Fork) A kan plate ɗin ya ce

"Ki ci abinci"

"Na ƙoshi" Da kallo ya bi ta sai lokacin ya lura da lema a fuskar ta kuma idanun jawur da alama kuka ta sake yi. Shiru ya yi yana nazarin ta sai ya ce

"Amma akwai yunwa a tare da ke ba zan cutar da ke ba, wallahi ban zuba komai a ciki ba, indomie ne na dafa miki"

"Ba zan iya ci ba"

"Baki isa ba ni babu wanda ya isa in ɓata lokaci na in girka abu saboda shi ya ce ba zai ci ba" Ya faɗa cikin faɗa-faɗa don ya lura akwai yunwar a jikin ta cin ne kawai ba za ta yi ba. Yana gama faɗar haka ya zauna tare da buɗe plate ɗin ya ɗora fork ɗin a kan indomien da take ta turiri ta sha attaruhu da albasa.

"Ɗauki ki ci" Ya ce cikin bada umarni muryar sa babu alamun wasa. Gabaɗaya yadda ya yi maganar sai ya bata tsoro duk sai ta ruɗe ta ma rasa mai za ta yi.

"Ki ɗauka ki ci na ce" Hannun ta har karkarwa yake ta ɗau fork ɗin ta ɗauki indomie ɗin ta nufi bakin ta sai dai tuno da Baffan ta sai kawai ta rushe da kuka. Jikin sa ne ya yi sanyi ganin tana kuka ko abincin bata kai baki ba.

"Mene ne damuwar ki?"

"Baffana ne ya mutu jiya da dare" Da mamaki yake kallon ta.

"Yanzu ina Baffan naki?"

"An binne shi da safe"

Shiru ne ya ratsa ɗakin sai shashshekar kukan ta ne kawai don tambayar ta da ya yi ina Baffan sai ta ji an tada mata mikin mutuwar.

"Ki yi haƙuri Allah ya jiƙan sa mu ma zaman jiranta muke yi" Ya faɗi hakan amma zuciyar sa

cike take da tarin tambayoyi sai dai ya ja bakin sa saboda ya ga bata da aiki sai kuka sai yanzu ya san mene ne damuwar ta, kuma ba zai matsa mata da cewa sai ta ci ba don ya san ciwon mutuwa tun da shi daga uwa har uban nasa basa raye duk da ba shi da wayo sosai suka mutu amma tabbas!. Ya san mutuwa tana da ciwo.

Fita ya yi jim kaɗan sai ga shi da shayi mai kauri a kofi, matsa mata ya yi sai da ta shanye tas. Bai ƙara bi ta kanta ba ko da ya je masallaci sallar isha ya dawo rufe gidan ya yi ya wuce ɗakin sa ya kwanta. MARAYAMA kuwa haka ta kwana ido biyu ga damuwar rashin Baffa ga damuwar inda za ta dosa daga nan goben sai kawai ta kwana tana nafila da addu'o,i a kan Allah kawo mata ɗauki cikin lamuran ta.

Da safe ma shayin ya haɗa ya kai mata duk da yana jin motsin ta da asuba da alama alwala ta yi, ya yaba da riƙon addinin yarinyar sosai. Ko da ya shiga ɗakin ma samun ta ya yi tana zaune ta yi nisa a tunani ganin sa cikin sanyin murya ta ce

"Yaya HAFEEZ ina kwana" Sai da ya lumshe idanun sa kafin ya amsa ya ji daɗin kiran sa da Yaya da ta yi, saboda shi bashi da ƙanwa bashi da Yaya shi kaɗai iyayen sa suka haifa.

"Lafiya lau" Ya amsa cike da murmushi.
Bayan ya fita ta shanye ganin gari ya yi haske jim kaɗan sai ta fito da kayanta a riƙe ta tsaya daga bakin barandar tana cewa.

"Zan tafi" Amma ta ji shiru ta maimaita ya fi sau biyar amma babu amsa da niyyar ta ta masa godiya amma ganin shirun ya yi yawa sai ta juya ta tafi, a bakin ƙofa suka yi kiciɓis da shi riƙe da leda a hannun sa. Da mamaki yake kallon ta.

"Ina za ki je?"

"Zan cigaba da tafiya"

"Zuwa ina?"

"Ni ma ban sani ba"

"Juya ki koma ciki" Sororo ta yi tana kallon sa ta san dai wajen kwana ya bata amma kuma yana mata umarnin ta koma mai yake nufi. Bata masa musu ba ta koma tana son ganin gudun ruwan sa duk da ta yi mamaki yadda yake kamili da har ya iya kwana da ita gida ɗaya ba tare da ya nemi lalata da ita ba.

"Wannan rigar a gidan wata tela da take ɗinka kaya tana siyarwa na siyo miki ki shiga ki yi wanka ki saka" Ya faɗa bai jira cewar ta ba ya juya zai fita.

"Da baka ba kan ka wahala ba ga kayana a cikin nan" Ta ce cikin sanyin murya bai ma kalle ta

ba bare ta saka ran zai tanka mata illa ficewa da ya yi daga ɗakin. Wankan ta yi tana fitowa ta tarar da mai haka ta shafa duk da zuciyar ta babu daɗi amma kamar yadda Baffa ne kaɗai a duniya yake bata kulawa ta ji daɗi da wannan ma ya nuna mata ita ma mutum ce.

Tana zaune ya shigo ya zauna ya haɗe rai kai ta sunkuyar.

"Ki bani labarin ki a taƙaice ko da ba za ki faɗa mini komai ba ina so ina sani" Shiru ta yi tana nazari sai kuma ta samu kanta da ƙin masa musu ta ce.

"Suna na MARAYAMA ni ƴar tsuntuwa ce ba a san iyayena ba tun ba a yanke mini cibiya ba aka jefar da ni... Da sauri ya ɗago yana kallon ta sai ya ji ta ɗora da faɗin

"Baffa ne ya riƙe ni da nuna kulawa, ya saka auduga ya toshe kunnuwan sa daga maganganun mutane, jiya Allah ya masa rasuwa shi ne matar sa ta kore ni daga gidan kuma ni ban san ina zan je ba ko ina ƙyamata ake an ce mini bani da uba ni shegiya ce...

"Ya isa haka!" Ya furta ransa yana ƙuna sosai ya ji furucin nata ya daki ƙwaƙwalwa da zuciyar sa. Bai ce mata ƙala ba ya tashi ya dice daga ɗakin, hawaye ta shiga gogewa dama ta san da wuya wani ya ji wace ce ita a yi maraba da ita don ma bata faɗa masa ɗaya ƙaddarar da ta same ta ba ta ciki wanda bata san ta ya aka yi ta same shi ba, don ta sani babu wanda ya taɓa kusantar ta ba sannan har ƙasanta take dubawa ko za ta ga wata alama ta cewa an kusance ta amma bata ganin komai, ita har yau tana da na sanin wanzuwar ta a wannan duniyar mai cike da makafin mutane da basu san mece ce ƙaddara ba!.

"Ki ɗauko kayan ki tare za mu wuce Dutse" Shi ne kawai abin da ya furta. Sororo ta bi bayan sa da kallo sai ƙamshin turaren sa da ya bar mata a ɗakin.

'Kenan bai guje ni ba?' Ta jefawa zuciyarta tambayar. Riƙe da kayanta ta fito tana sanye da doguwar rigar atamfar da ya kawo mata ta ɗora hijabi a kai.

Tana fitowa ta ga wata haɗaɗɗiyar mota sai ɗaukan ido take, daga gefe ta samu wuri ta tsaya, ƙofar gidan ya kulle. Gaban motar ya buɗe mata ya ce ta shiga, tana shiga ya rufe ya koma mazaunin direba ya shiga ya tada motar maimakon ya bi cikin gari sai ya miƙe ya bi ta can tun da dama bayan garin ne babu wanda suka haɗu da shi sai wani tsoho da ta ji yana ce masa likita bokan turai wanda hannu kawai HAFEEZ ɗinya ɗaga masa suka fara tafiya.

Shiru sai karatun qur'ani da yake tashi a motar, kowa da tunanin da yake, ita tana tunanin yadda za a karɓe ta a inda za su je ba ma wannan ne ba abin jin sai abin da take ɗauke da shi wanda bata sanar masa tana ɗauke da shi ba. Shi kuma yana tunanin ta ina zai fara? Mai zai cewa Kaka game da wannan yarinyar shin za ta yarda ta zauna da ita ko kuma yaya shi dai ya ji yana tausayin yarinyar kuma dai ya yarda da ita bai ga alamar ƙarya a maganganin ta ba.

*YA ABDUL*

Tun da aka yi bakwai sai ya ƙara komawa tamkar ba a wannan duniyar ba, haka yake jin sa tamkar wanda ya rasa ɓarin jikin sa haka yake ji, bai taɓa zaton haka yake ƙaunar Aunty RABEEYA ba sai da ta bar duniya!. Ya shaƙu da ita irin shaƙuwar da ko a mafarki bai taɓa kawo mata mutuwa a kwana kusa ba, kullum tunanin sa sai sun hayayyafa sun aurar kai sai tsufa ya riske su suna tare da juna, in da san samu ne su mutu a tare amma kash!. Ashe dai ihu yake bayan hari mai duka ya daɗe da rubuta cewar rayuwar ta gajera ce.

Ya zama tamkar wani mutuntumi, an yi nasihar an yi wa'azin har an gaji, don shi wuyar ta ka fara masa nasiha a kan ya manta da RABEEYA ya yi lamuran sa sai kawai ya fara maka kuka. Abu ɗaya ne yake kwantar masa da mikin rashin ta shi ne Little RABEEYA yarinyar da take kama da uwar ta sak tamkar an tsaga kara, kallon ta ne kawai yake sa ya ji tamkar dai tana wannan duniyar amma in ba wannan ba komai ya zame masa hoto a wannan duniyar.

Momma ma hakan ne a wajen ta don ta sani RABEEYA mutum ce mai haƙuri da kawar da kai ga ladabi biyayya ga riƙon ibada da son ƴan uwa hakan ya sa ta kasa jure rashin ta, dakyar ma Abba ya bar mata Little RABEEYA saboda take rage raɗaɗin mutuwar Aunty RABEEYA don mutuwa ce da ta riske su babu zato babu tsammani kasancewar ba a taɓa musu mutuwar ba ma. Gidan Abba nan ne ya zama mazaunin YA ABDUL don shi ko kunyar surukuntaka ba ya ji ta Momma haka zai shigo ta miƙa masa yarinyar ya zauna ya saka ta a gaba watarana ya ringa wa yarinyar magana yana kuka in ta ga abin ya yi yawa sai ta karɓe ta.

Madarar da ake bata kuwa har gajiya Momma take da tara su, gasu nan jingim da famfas da duk wani abu na yarinyar kawai libgowa yake ya kawo. Har kayan wasa yake kawowa sai dai a kai store na ajiyar kayan wasa a ajiye tun da bata isa wasan ba. A haka har aka yi wa Aunty RABEEYA arba'in.

*HEEDAYA*

Sun yi jimami na wuni ɗaya ita da Umma, daga ƙarshe kuma sai su shiga ɗaki suna ƙusƙus ita da Hajiya Aisha da Umma don Hajiya Aisha har sai da aka yi bakwai sannan ta daina zuwa a cewar ta zaman makoki take zuwa wanda ba haka bane illa shirye-shiryen yadda za su ɓullowa al'amarin HEEDAYA da ta mutu a kan son Ya ABDUL.

"Umma wai yanzu ya za a yi da wannan sakaran Ya ABDUL ɗin wannan Umma kina gani ya kafe a kan tunanin mace ɗaya kowa har ya gane shi, ko office ya je babu abin da yake

tsinanawa sai dai sauran ma'aikatan suke yi ko a ina kika gan shi ya yi jugum tamkar shi aka fara yi wa mutuwa a duniya" HEEDAYA ta ce tana jan wani uban tsaki.

"Haba HEEDAYA kar ma ki fara kishi da kushewa, don ita tata ta ƙare, ai kamar yadda hausawa suka ce mutuwar wani tashin wani, haka ce za ta kasance, a gaba za ki zo ki murza kambun ki yadda kike so" Umma ta ce tana dafa kafaɗar ta.

"Na ji Umma amma fa ba ma wai tunanin Aunty RABEEYAR da yake yi ba ne kaɗai abin ji waccan filillikar jaririyar mai kama da ɗiyar roba duk ya ƙwallafa rai a kanta, ni wallahi haushin ta nake ji ita ma Ammien da ta bari ɗanta ya zama lusarin namiji duk ya ƙare a kan mace ɗaya da ƴarta"

"Rabu da sakarkaru da sannu duk za mu damƙa musu kashin su a hannu, ke ni ma diddibtun da yake a gidan nan ya ishe ni ya zauna yana reno kamar mace"

"Rabu da shi Umma zai daina ne wallahi ni in na shiga gidan sa ba zan ɗauki wannan cin kashin ba yo ina dalili yarinya uwar ta ta mutu ana ganin kamar an jefar da ƙwallon mangwaro za a huta da ƙuda ashe dai an kashe miciji ne ba a sare kansa ba wato akwai sauran rina a kaba" HEEDAYA ta ce tana kama haɓa.

"Bar ni da su ai gobe za mu koma wajen boka kin sa tun ranar kwana ukun mutuwar nan muka je muka masa godiya a kan binciken da ya mana na cewa akwai aure tsakanin ku da shi, to sai ya ce idan an yi arba'in mu koma"

"Gwara dai ku je, don na ga sai an zage dantse an hau kan su don wallahi wannan Ya ABDUL ɗin yadda kika san ƙiyayyta ake dasa masa kullum a rai haka yake nuna mini ko gaishe shi na yi dakyar yake amsawa sai ka ce ni na kashe masa matar"

" Zai yi bayani ne bari dai ke mu gani sai ya koma bita zai-zai kuma mijin ta ce" Wani murmushi HEEDAYA ta yi jin furucin nan na Umma don ya daɗaɗa mata sosai, har ta fara hango yadda za ta gara Ya ABDUL tamkar ƙwallon ƙafa, ba iya shi kaɗai ba hatta Ammie sai ta jogale mata ɗan matsayin da take ganin tana da shi a wajen ɗan nata.

Washe gari Umma da Hajiya Aisha suka tasamma wajen boka, bayan sun shiga kamar yadda suka saba suna zaune tamkar wanda suke jiran tsammani sai dai kowa fuskar sa da annuri.

"Ku daina sarewa akwai aure a tsakani don kamar yadda na faɗa muku a baya to tabbas!. Auren nan babu fashi sai an yi"

"Boka ka san dai an ce mai zurfin ido da wuri yake fara kuka, to shi yaron ne ko kallo HEEDAYAR bata ishe shi ba, har yanzu hoton matarsa ne liƙe a zuciyar sa sai kuma ƴar da ta mutu ta bari, shin ita HEEDAYA ce za ta furta masa kalmar so ko kuwa jira za ta yi ya furta mata, sannan ka san hatta uwar sa akwai takun saƙa a tsakanina da ita ba lallai ta amince da auren nan, bare kuma shi mai gayya mai aiki mahaifin ta shi ne abin da yake ci mini tuwo a ƙwarya"

"Ita ɗin banza ai babu wani shege babu shegiya, kowa sai mun saka shi a taitayin sa,sannan kuma ina so ki sani sai dai HEEDAYA ta je masa da kalmar so amma shi ba zai faɗa je mata ya ce yana son ta ba, kuma son matarsa marigayiya ya gama wanzuwa a zuciyar sa mu ba za mu iya fitar masa ba lokaci guda sai dai a sannu haka ma son ƴarsa fatan mu kawai auren ya shiga tsakani daga lokacin komai zai zama tarihi don sai na kafa ta a gidan sa"

"Yawwa kamar ka san tana da mugun kishi kuwa bata son kowa ya raɓe shi, shi ma bata son ya raɓi kowa"

"An gama!" Ya furta yana buga bayan wata ƙwarya wata wuta ta fito bul sai kuma ta ɗauke.Wata laya ya ɗakko baƙaƙirin ya goga a bayan ƙwaryar inda wutar ta fito sai ya miƙa mata.

"Ta haɗiye wannan da ruwa" Daga Umma har Hajiya Aisha idanu suka zaro.

"Hajiya Fatin wato mahaifiyar ABDULHAKEEM ɗin ce za ta haɗiya?" Umma ta tambaya muryar ta tana rawa.

"Kar ki zo mana da zancen banza da wofi!. Ita HEEDAYA ce za ta haɗiye layar wannan da sannu idan ta haɗiya zai fara ganin farin ta a maimakon yanzu da yake ganin baƙin ta da ni ma ban san dalilin hakan ba"

"To an gama godiya muke za ta haɗiye kuwa" Ta faɗa tana sakawa a jaka suka ɗan kalli juna ita da Hajiya Aisha kafin suka biya shi kuɗin sa suka kamo hanya.

"Wai kin ji yadda gabana ya faɗi, ya za a yi ta haɗiyi laya ni Zainab?" Umma ta ce tana kallon Hajiya Aisha da take tuƙi.

"Ni ma na ji hakan amma kar ki manta biyan buƙata muke nema komai ma za mu iya yi kin san

an ce ranar biyan buƙata rai ba a bakin komai yake ba, kuma biyan buƙata ya fi dogon buri" Da haka suka ƙaraso cikin gari ta ajiye Umma ta wuce gida.

"Gaskiya aikin bokan nan ya fara bani tsoro ya za a yi a ce a haɗiye laya ba ma a ƙona ta ba ko a binne" Umma ta ce tana kallon HEEDAYA.

"Yanzu Umma haɗiyar layar ne kamar dai wanda ya ce a haɗiyi wuta?!. To ko mai ya ce ai mu namu to ne tun da biyan buƙata muke nema duk abin da zai faɗa zan zama mai aiwatarwa in dai a kan Ya ABDUL ne fatana dai idan an yi auren Umma ki saka bokan ya mini asirin mallaka yadda zai zamana babu shi babu kallon wata mace sa sunan so ya zamana nu kaɗai yake ƙauna ni kaɗai yake gani"

"Sha kurumin ki ki kwantar da hankalin ki kamar tsumma a randa ai fa za mu buga shi yadda muke so sai yadda kika ce ko kara kika ajiye bai isa ya tsallaka ba, yanzu dai ki samu ki haɗiyi layar sai ki je masa goben da maganar soyayyar"

Da safe ta fito daga part ɗin Umma suka yi kiciɓis da Ya ABDUL da ya sanya gaban shi hanyar part ɗin Momma ta san kuwa zancen gizo ba ya wuce na ƙoƙi wato wurin Little RABEEYA zai je. Duk da fuskar sa babu walwala amma a hakan ma ya mata kyau ji take tamkar ta je ta kama hannun sa ta tambaye shi dalilin fushin sa gare ta mai ya sa ya daina son ta sai dai tunowa da cewa komai ya zo ƙarshe ta marairaice murya ta ce

"Ya ABDUL ina kwana"  Kamar ba zai amsa ba har ma ta cire rai zai yi magana ya ce

"Lafiya" A taƙaice ya wuce ta tamkar dai bai ma santa ba. Da harara ta raka bayan shi tare da yin ƙwafa ta ce

"Duk ranar da ka shigo hannu za ka gane shayi ruwa ne" Ta juya ta tafi. Da yamma ta haɗiyi layar don ta san dole zai dawo ganin Little da yammar kafin hallaw ya ƙara zuwa da dare. Tana laɓe tana ganin sa har ya shiga ya fito bayan daɗewar da ya yi. Ganin ya nufi hanyar waje ta fito daga maɓoyarta ta bi bayansa don zuwa ta aiwatar da abin da bokan ya ce. Yana zaune a mota ya kifa kansa a kan sitiyarin ta je, sanin a shirye take don ta haɗiyi laya ta san ba zai taka mata birki ba ko mata shamaki da zuwa wajen sa. Motar ta buɗe ta shiga kujerar mai zaman banza, hannu ta kai ta shafo fuskar sa ya ɗago da sauri yana kallon ta da idanun sa da suka rine da ja don tunanin Aunty RABEEYA ne da kewar ta yake addabar zuciyar sa.

Kai ta langaɓar gefe, shi kuma ya sanya hannu ya dafe kansa kamar dai wanda ya sara masa, baki ta cije tare da yin murmushin gefen baki don ta san tarkon ta ya kusa kama tsuntsu da a ce maganin bai fara aiki ba da ba yadda za a yi ya ganta cikin motar bai tsawatar mata ba, kuma har ta kai hannun ta kan fuskar sa bai taka mata birki ba.

Komawa ta yi ta jingina bayanta da jikin kujera, idanu ta lumshe tana hango irin yadda za ta ci duniyar ta da tsinke idan ta mallaki Ya ABDUL matsayin miji.

"Ya ABDUL tafe nake da wata magana mai girma ina son ka bani amsa ta" Ƙurr ya mata da idanu tamkar wani dolo ganin bai ce komai ba ta ɗora da cewa.

"Ina son ka Ya ABDUL, ba so na ƴan uwantaka ba so na aure mene ne ra'ayinka kan hakan?"

MAMAN AFRAH
09013181851

*Ina siyar da zannuwan gado, masu filo biyu, masu filo huɗu, akwai masu labuleye masu bargo da sauran su. Ina siyar da labulaye kala-kala, kayan yara, lesuna atamfofi, abayas takalma sarƙoƙi, frames na bango, materials. Sayan ɗaya ko sari ina aikawa kowane gari, ga link nan mai son sari ya shiga ko a mini magana ta no ta 09013181851 idan ba saya zaki yi ba kar ki mini magana bana son ɓata lkc. Wanda basu da jari za su iya shiga grps su ɗauki kayan su ɗora ruvar su idan sun samu masu siya su ɗauke ribar su ni kuma zan aikawa duk wanda ya siya ta hannun su. NGD MAMAN AFRAH🥰*

[2/19, 5:22 PM] MOM MASHKUR & AFRAH:
https://chat.whatsapp.com/F7TUZezpOWLKYnyTNFuy2Y

BONONO

(RUFIN ƘOFA DA ƁARAWO)

NA

MAMAN AFRAH

First Class Writer's Asso.📝

*SADAUKARWA*

Daga farko har ƙarshe sadaukarwa ne ga MARYAM SANI HAFIZ (Merry tah) Alkairin Allah ya kai gare ki Allah lulluɓe rayuwar ki da tarin ni,imomi da albarkatu Allah raya mana Abdallah fatan alkairi.

Daga marubuciyar:

Ruɓaɓɓiyar igiya
Ƴan adaidaita sahu
Ungozoma
Ƴar zaman wanka
Ƙara'in inna delu
Beelal
Jalli joga
Da sauran su.
*09013181851*

PAGE 12

*MARYAMA*

Horn ya yi mai gadin da sauri ya wangale musu get tana ta kallon gidan yadda ya tsaru kuma yake da kyau. Fitowa suka yi tana riƙe da kayan ta sai ɗan noƙewa take irin na rashin sakin jiki.

"Gidan mu ne nan ba siyar da ke zan yi ba" Ya ce yana kallon ta ɗauke da kurmushi. Bata ce komai ba fuskar ta ta yi fayau da alama har lokacin damuwa tana nuƙurƙusar zuciyar ta.

Gaba ya yi ta bi bayan sa.

"Kin saka ni a gaba sai ka ce wani ɗan ki" Ya ce lokacin da ya ja ya tsaya yana kallon ta tana tahowa da sanyin jiki da yake akwai tazara daga get zuwa cikin gidan, ga shi kuma ya ɗan bar ta a baya sosai.

"Ai da yake ni ban san gidan ba" Ta faɗa cikin sanyin muryar ta.

"Tun da baki sani ba sai ki ɗago ƙafa don in na ɓace miki va samun hanya za ki yi ba"

Da sallama suka shiga gidan wata mata ta amsa musu tana musu marhabin.

"Likita bokan turai" Ta ce cikin zolaya tana dariya.

"Wannan dai bokan ƙauye ne, tun da a can yake aiki" Ya faɗa shi ma yana dariya.

"Duk ɗaya dai" Dariya ya yi suka shige falon bayan MARYAMA ta gaishe da ita.

Zaune take a falon farantin kankana da lemon fata a gabanta tana sha, bayan ta amsa musu sallamar ta ɗago ta kalle su.

"Zauna MARYAMA ya ce bayan ya samu waje ya zauna kusa da Kaka, tare da ɗaukan kankana ya kai bakin sa.

"Sai zuwa ba sanarwa" Kaka ta ce tana kallon sa.

"Ni da gidan mu?" Ya ce yana ɗaukan lemon ya sha.

"Barka da rana, ina yini" MARYAMA da ta samu wuri a kan carpet ta zauna ta faɗa cikin girmamawa.

"Lafiya ƙalau ƴan mata" Kaka ta ce tana bin ta da kallon rashin sani.

"Sunan ta MARYAMA mun haɗu a ƙauyen da nake aiki jiya da dare marainiya ce bata da kowa ma a taƙaice" Ya kai ƙarshen maganar yana kwashe komai da MARYAMA ta faɗa masa ya faɗa wa Kakar yana fatan Allah ya sa ta amince da maganar don ya santa wani likacin butsuwa ce.

Kallon ta Kaka take yi tana nazartar ta, MARYAMA kuma ta sunkuyar da kai idanun ta suna cikowa da ƙwalla, don babu abin da yake saurin karyar mata da zuciya irin ta ji ana batun bata da kowa musamman da ya ce shekaran jiya mariƙinta ya mutu.

"Daga wane ƙauyan kike?" Kaka ta faɗa tana kallon ta.

"Ƙauyen KANYA"  Bayan ta bata amsae ta shiga mata wasu tambayoyin da har sai da ta gamsu da gaskiyar ta, sannan ta ce ta amince ta zauna da su. Ɗaki aka saka Mero ta raka ta, wacce aiki take yi kuma dai a gidan take zaune ita da Kakar sai kuma sauran ma'aika maza.

Bayan sun keɓe da Ya HAFEEZ ɗin take ta masa faɗan kar ya ƙara mata kwashe-,kwashe sannan ma ta ce sai ta saka an binciko mata can ƙauyen KANYA a ɓoye a kan abin da MARYAMAR ta faɗa duk da ta fahimci iya gaskiyar ta ne ta faɗa.

Bayan kwana biyu, zaune take a gidan Kaka hankali kwance don babu kyara babu tsangwama ga shi sai suke ta jan ta a jiki ko kuma jan ta da zance, hakan yana rage mata ƙunci sai yanzu take jin tana  rayuwa ta ƴanci tamkar wata mai gata ko mai iyaye a raye ba irin rayuwar gidan Baffa ba da take yin ta cikin tsangwama da rashin galihu sai ta ɓangaren Baffa ne ko Goggo kafin ta mutu take samun salama. Ya HAFEEZ ya koma ƙauye tun washe gari tana jin sa in suna waya da Kaka yana tambayar ta ita. Yanzu Kaka ta ce ma idan ya dawo za a saka ta a makaranta tun da ta kusa kammalawa tana ss 2 ne.

*BAYAN WATA GUDA*

Kaka zaune take tana kallo sai MARYAMA da take moppin a falon kasancewar bata son zama sai take aiki ko da an hana ta an ce da masu yi. Kaka ce ta yi tsai tana ƙarewa MARYAMA kallo mamaki da fargaba cike a zuciyar ta ganin fuskar MARYAMA ta sauya duk ta ciko hatta jikin ta duk ya sauya tamkar dai mai ciki haka Kaka take mata kallo don dama wani lokacin tana yi mata kallon hakan sai dai yau abin ya ruɗa ta.

Bata san ya aka yi ba ƙurawa marar MARYAMA ido da ta yi sai kuwa ta yi kiciɓis da ganin tudu a marar MARYAMA, yawun bakin ta ne ya ƙafe lokaci guda zufa ta wanke mata fuska ta shiga gangarowa zuwa wuyan ta. Dakyar ta samu kalmomin da ta haɗa haruffan wajen kiran MARYAMA. MARYAMA jin Kaka ta kira ta, sai ta ajiye mofa ta taho wajen Kaka, sai dai kallon da ta ga Kaka tana jifanta da shi ya saka mata tsoro da kuma ruɗani.

Saboda gabaɗaya ma ita shagala take da cewa akwai wani ciki a jikin ta, saboda yanzu bata da damuwa sosai tun da dama ita gorin da ake mata ne yake damunta na cewa ita shagiya ce tsintacciya yanzu kuwa babu mai mata gori sai kuma damuwar mutuwar Baffa duk da tana masa addu'a kuma hakan yana sanya salama a ruhin ta.

"Tashi tsaye" Kaka ta faɗa tana kallon ta don tana zuwa gaban Kaka ta durƙusa alamar girmamawa, ita Kaka ta rasa ma mai yake mata daɗi fatan ta dai zaton ta kar ya zama gaskiya. Ta san ta aika an binciko mata cewa akwai wata MARYAMA da take ƴar tsintuwa kuma mariƙin

ta ya mutu, mai binciken ya dawo mata da amsar cewa tabbas akwai ta, amma dai matar mariƙin ta kore ta daga gidan don haka yarinyar bata garin ma. Wannan ne ya sa ta yarda da gaskiyar MARYAMA amma bayan wannan babu abin da aka binciko mata dangane da ita ashe dai akwai sauran rina a kaba. MARYAMA tsaye ta tashi ai kuwa Kaka da ita ma ta miƙe tsaye ganin abin ba na yi ba ne ta saka hannu ta gwale idon MARYAMA gabanta ne ya buga da mugun ƙarfi. Da sauri ta saka hannu ta ɗan ɗama rigar MARYAMA ai kuwa ta ga marar ta ta yi tudu kana gani kuma ka san ba timbi bane tun da a mara ne ba a ciki ba. MARYAMA gabanta ne ta doka da ƙarfi jikin ta ya shiga karkarwa da za a tsaga jikin ta ba za a samu jini ba ko kaɗan, saboda ruɗewa da kuma fargaba.

"Ciki ne da ke ko?" Kaka ta tambaya muryar ta tana karkarwa. MARYAMA wacce hawaye ya fara ambaliya a dakalin fuskar ta, cikin sanyin jiki ta shiga gyaɗa kai tamkar ƙadangaruwa don ta san aikin gama ya gama tun da babu wani abu da za ta ɓoye, tunanin ta ɗaya ma da bata sanar da Ya HAFEEZ ba tun a ranar da ya buƙaci jin labarin ta, yanzu za su ga ta munafurce su.

Kaka ganin MARYAMA tana kuka kuma ta gyaɗa kai alamar eh ce amsar tambayar da ta mata, sai hankalin ta ya ƙara tashi tana ta ambaton innalillahi wa inna ilaihir raji'un a zuciyar ta don a ganin ta tun da har MARYAMA ta san da cikin to tabbas shi ma wanda ya kawo ta wato HAFEEZ ya san da hakan nan take zuciyar ta ta shiga saƙa da warwara a kan cewa HAFEEZ ya yi wa yarinyar ciki ne shi ne ya kawo ta gidan duk da ta yarda da shi a kan tarbiya da tsoron Allahn sa amma dai ta san shaiɗan shi ne mugun mai yin jagoranci wajen aikata alfasha.

Ko ta kan MARYAMA bata bi ba, don yanzu gabaɗaya ta fi ganin laifin HAFEEZ da ya ɗakko yarinya ɗauke da cikin shege ya kawo mata gida tun da dai a kaf tarihin yarinya babu inda aka ce an mata aure. Waya ta ɗauka ta doka masa kira, yana kishingiɗe yana ɗan danna laptop kiran Kaka ya shigo zaune ta tashi yana sakin murmushi don ko ba komai idan sun yi waya zai tambayai lafiyar MARYAMAR shi wacce a yanzu yake jin koɓai yake da tunanin ta yake ya san kuwa babu makawa da son ta zuciyar sa ta kamu.

"Assalamu alaikum Kakata ta kain...

"HAFEEZU ni za ka rainawa wayo ka manta ni na haifi ubanka? Tunanin ka na yi tsufan da za ka yaudare ni, ka ɗakko yarinyar da ka ɗirkawa ciki kuka raina mini hankali ka kawo mini ita gida.... Kalaman da ta masa suka daki ƙwaƙwalwar sa, gabansa ya buga da ƙarfi mamaki al'ajabi suka taru suka cushe masa zuciya, shi kansa bai san lokacin da ya tashi tsaye ba daga zaunen da yake, tambayoyi barkatai suna cika masa kwanya...

*HEEDAYA*

Da idanun ta ta kafe shi tana jiran amsar sa. Ya ABDUL da bakin sa ya masa nauyi ga wani irin azababban ciwo da kan nasa yake masa, so yake ya musa wannan maganar sa take tambayar sa sai dai ji yake ya kasa, ji yake tamkar zuciyar sa za ta kama da wuta idan ya yi musu saboda wani zafi da yake ji zuciyar tana masa da alama ba zai samu salama ba har sai ya yi na'am da abin da ta zo masa da shi. Kai ya shiga gyaɗa mata yana kallon ta da rinannun idanun sa da har yanzu basu washe ba na kukan rashin Aunty RABEEYA da ya yi wanda ya zame masa jiki. Wani shu'umin murmushin cin nasara HEEDAYA ta yi kafin ta ƙara jefa masa wata tambayar.

"Kana so na? Za ka aure ni?" Ta tambaya tambaya tana wani haɗe rai don yanzu gyaɗa kan da ya yi hakan yana mata nuni da ta kama shi a hannu don haka dole ma ta fara yin yadda ta ga dama.

Kan dai ya ƙara gyaɗa mata a karo na biyu.

"Ba na son auren nan ya ɗauki wani lokaci ina so ka sanar da Abba za ka aure ni domin in maye maka gurbin Aunty RABEEYA, sunan Aunty RABEEYA kaɗai da ya ji ta ambata sai da ya ji zuciyar sa ta motsa, sai dai tantamar kalaɓanta yake sai dai ya kasa mata musu, wai aure shi ABDULHAKEEM ne zai yi aure kuma auren ma HEEDAY?. Waɗannan tambayoyin ne suke masa kai kawo a birnin zuciyar sa, sai dai babu yadda zai yi ya yi musu.

"To zan samu Abban " Ya faɗa tamkar wani sakarai har lokacin kansa tamkar ana buga masa guduma. Hannu ta ɗora a haɓar sa ta ce

"I luv you Ya ABDUL na daɗe ina ƙaunar ka, ni na sani na fi kowa son ka tabbas idan ka aure ni zan saka ka manta da kowace ƴa mace" Tamkar majigi haka yake kallon ta. Ƙofar ta buɗe ta fita shi kuma ya kifa kansa ya ma rasa wane kalar tunani zai yi.

A guje ta shigo falon Ihsan da Mubashshar da suke zaune Mubashshar yana assignment ita kuma tana kallo sai gani suka yi ta shigo kamar an jefo ta, ɗakin Umma ta shige ta danna mukulli Umma ta rungume tana ta tsallen murna, su duka dariya suke tamkar an musu albishir da kujerar hajji.

"Kar ki kayar da ni" Umma ta faɗa tana dariya.

"Umma wallahi ya amince ko musu bai yi ba kuma ya yarda zai sanar da Abba" Ta faɗa duk ta wani ruɗe ta zauce.

"Haba yarinya boka fa aka ce kuma kar ki manta laya fa kika haɗiya ai aiki dole ya ci"

"Tabbas Umma ai wallahi ban taɓa zaton zai amince cikin ruwan sanyi ba sai wani dafe kai yake"

"Ƙyale shi aikin ne ya ci shi ya sa kan yake sara masa ai ko nawa ne sai mun kashe, don sai kowa ya san ke kike auren sa musamman Hajiya Fati sai na nuna mata gaba da gabanta"

Shiru-shiru suna jiran su ji magana ta kai kunne Abba amma babu amo ba labari sai dai sun yi ɗif suna jiran tsammani. Tsawon sati uku shiru. A ɓangaren Ya ABDUL kuwa sai ya yi kamar zai je ya sanar da Abba kawai sai tunanin Aunty RABEEYA ya hana shi sakat sai yake ganin bai mata adalci ba daga mutuwar ta ya yi aure shi ba ya ma son ya auri HEEDAYA sai dai babu yadda zai yi don zuciyar sa azalzalar sa take yi. A wani yammacin Litinin ne bayan ya dawo daga wajen aiki ya yi wanka da yake yanzu gidan su yake ya ƙi zaman gidan sa saboda babu Aunty RABEEYA a ciki. Da sallama ya shiga falon Abba.

Bayan ya amsa masa ya zauna a ƙasan capet ya gaishe da shi.

"ABDULHAKEEM ka ƙi ka kwantar da hankalin ka ko? Duk ka yi baƙi ka rame kar ka manta fa Allahn da ya bamu RABEEYA ya fi mu son ta kuma shi ya karɓi abarsa ya kamata ka sawa ranka dangana kake mata addu'a" Shiru ya yi yana mai sunkuyar da kai sai yake ji tamkar wanda zai faɗi wani saƙo don a ganin sa tamkar abin kunya ne kuma cin amana sai dai ya kasa dakatar da kansa shi ma bai san dalili ba.

"Ina mata addu'a Abba"

"To Allah ya ƙara maka haƙuri haƙiƙa da wuya samun irinka a wannan zamanin mai son matar sa haka saɓanin wasu daga matan sun mutu shikennan sun manta da su"

"Abba dama magana na zo mu yi"

"Ina sauraron ka"

"Am, dama, dama"

"Dama mai?"

"Ina son na auri HEEDAYA" Idanu Abba ya ƙanƙance yana mamakin furucin nasa har sai da ya ce ya maimaita don shi Abba a iya sanin sa bai taɓa zaton a kwana kusa ABDULHAKEEM zai nemi yin wani aure, tunanin sa ma sai sun zaɓa masa matar za a masa auren dole don shi da

yake faɗin ya gama aure bare kuma wai HEEDAYA zai aura.

Mamakin sa ya ɓoye ya nuna masa jin daɗin sa amma a zuciyar sa tabbas ya yi mamakin hakan.

"Ai ta kwana gidan sauƙi HEEDAYA ai ƙanwarka ce sai dai kuma ka same ta ka ji daga bakin ta ni ma za mu yi magana da Daddyn ka da kuma Hajja"

"Ai mun yi magana da ita ta amince"

"Ikon Allah to, ba damuwa za mu zauna da Daddyn ka sai mu ji yadda za mu ɓullowa lamarin" Daga haka ya yi wa Abba godiya ya fito sai yake jin tamkar ya sauke wani nauyi don tun da HEEDAYA ta masa furucin nan bai samu nutsuwa ba sai da ya furzarwa Abba kalaman nan. Abba kuwa da mamaki ya cika shi sai dai hakan ma abin so ne ko ba komai Ya ABDUL ɗin zai samu nutsuwa.

Sosai aka sha faɗi tashi da maganar auren aka iyo wa Ya ABDUL caaa musamman Ammie don a ganin ta yaushe ma matar sa ta mutu har zai nemi ƙara aure auren ma da HEEDAYA. Sai dai ta san ita bata isa ta hana ba domin sai da Daddyn ABDUL ɗin ya gargaɗe ta don ya san basa ga miciji da Umma. Hatta Momma sai da ta shiga ta fita ta hanyar kissa da kisisina a kan ganin ta hana auren amma abin ya ci tura. Saboda Umma da Hajiya Aisha su tashi haiƙan a kan lamarin auren kullum suna hanyar zuwa wajen bokan su don ganin an yi wa bakin kowa dabaibayi musamman wanda zai yi yunƙurin hana auren.

Hajja kuwa daɗi ta ji na wannan haɗin don a ganin ta gida bai ƙoshi ba ba a kai daji ba. Aunty Hafsa kuwa ta san tabbas abin nan ba Ya ABDUL yana hayyacin sa ba ne tun da dama ta san ƙudurin su Umma tun ba yau ba bare kuma yanzu da suka samu sarari ita dama an daina saka ta a sabgar an kuma daina shawara da ita tun da sun gane bata tare da su.

Yau ya kama wata uku cif da mutuwar Aunty RABEEYA wanda ya yi daidai da saura kwana sati ɗaya ɗaurin auren HEEDAYA da Ya ABDUL. Zaune ƴan gidan suke su duka a falon Abba da ya kira taro, sai dai bai ce komai ba, bayan mintina kaɗan Ya ABDUL da Abba ya kira ya shigo da sallama gaishe da Abba ya yi sannan ya shiga gaishe da Momma wacce ta amsa babu yabo babu fallasa don ita yanzu mugun haushin ABDULHAKEEM ɗin take ji, na auren da zai yi wai ya rasa ma wa zai aura sai HEEDAYA , sosai take jin takaicin hakan don har maganganu Umma take yada mata, shi ya sa yanzu ko ganin Little RABEEYA ya zo sai ta ga dama take barin sa ya ganta wataran ma sai ta ce maaa bacci take ta hana shi ganin ta haka zai gaji ya tafi.

Ko da ya gaishe da Umma faram-faram ta amsa daɗi duk ya cika mata zuciya ganin Momma tana ta muzurai. Yaran ne suka shiga gaishe da shi ya amsa ya samu waje ya zauna.

Gyaran murya Abba ya yi ya fara magana.

"Abin da ya sa na tara ku a nan ba komai ba ne sai magana a kan RABEEYA ƙarama, wato ABDULHAKEEM ya same ni a kan cewa idan ya yi aure za ta koma hannun sa da zama" Ƙirajen mutum uku ne suka buga da sautin diririmdimmmmm. Ƙirjin Momma wacce ta ci alwashin azabtar da Ya ABDUL ta dalilin yarinyar don yanzu ta saka a ranta sai ta ringa zuwar masa da buƙatun kuɗi don take tatiƙe shi sannan take azabtar da shi ta hanyar hana shi ganin yarinyar don ta ɗaga mas hankali ta hana shi kwanciyar hankali don kishi take taya ƴarta duk da bata raye. Sai kuma ƙirjin Umma uwar amarya jin wai za a ɗauki yarinya a kai gidan ƴarta kenan waye zai reni yarinyar da ko zama bata yi? HEEDAYA za a kaiwa wahalar ko wa?. Sai kuma ƙirjin mai gayya mai aiki HEEDAYA da ta ji tamkar ana dakan sakwara a ƙirjin nata jin wai za a mayar da ita ƴar raino ita da ta ci burin zuwa ta miƙe ƙafa ta huta amma ake wani batu.

"Haba Alhaji yarinyar da bata gama warewa ba, a barta mana a nan in ma zuwa gidan uban nata ne sai take zuwa bayan ta girma take zuwa da yawo" Momma ta faɗa.

"Kin san dai in na yi magana babu mai warware mini, ko ƴarki ce? To mai ƴar ne ya buƙaci haka kuma babu sauyi duk ranar da ya buƙaci karɓar ƴarsa bayan ya yi auren zai iya zuwa ya ɗauke ta ni dai na sanar da ku na fita haƙƙi shi ya sa na kirawo shi don ku ji daga bakin sa" Abba ya faɗa cikin faɗa.

"ABDULHAKEEM idan ka yi aure duk ranar da ka ji ta raya maka ka zo ka ɗauki ƴarka ka tafi da ita" Abba ya ce yana masa umarnin ya tashi ya tafi. Fita ya yi ya tafi.

"Bayan shekara biyar amma?" Umma ma da ta kasa haƙuri ta tambaya.

"In ma bayan shekara ɗaya ne ruwan sa ne wannan, ni dai na sanar ne don ku kwana da sanin hakan watarana ku tashi na sallami kowa" Da wannan aka watse ran kowa yana suya.

"Umma kin ji wani sabon tashin hankalin kuma ko? Wai mai ya sa komai idan za a yi sai an samu gargada ne ?" HEEDAYA ta tambaya ranta a ɓace don bata taɓa kawowa haka za ta faru

ba.

"Kayya HEEDAYA ni ma abin ya ɗaure mini kai amma ai tun da bayan shekaru ne ba ma nuna zalamar mu a fili ba kin ga sannan ma yarinyar ra zama ta dara moruwa ba sai ta zama ƴar aike da aikin ki ba" Umma ta ce tana dafa ta. Shiru ta yi sai kuma ta murmusa amma dai duk da haka ba hakan aka so ba ƙanin miji ya fi miji kyau!.

Duk da haka sai da su Umma suka ziyarci boka amma ya tabbatar musu da cewa babu ruwan su game da ƴarsa don son ƴar a cikin jini da tsokarsa yake ba za a iya raba shi da son ba haka ma matarsa da ta mutu ba za a iya hana shi tunanin ta ba tun da dai auren ne muradin su kuma an yi to su yi haƙuri da wannan. Haka dai suka dawo jiki babu ƙwari sai dai sun lallashi HEEDAYA a kan cewa ta haƙuran tun da kafin ma yarinyar ta koma wataƙila ita ma ta haifi nata yaran tun da ba sanin ranar komawar aka yi ba, tun da sai an ɗauki shekaru an dai sanar ne don su sani ko ba daɗe riƙo ƴa zai koma gidan ubanta.

Hanzari ba gudu ba Abba ya taka birkin duk wani shirye-shirye na auren domin kuwa ya ce ko walima ba za a yi ba aure za a ɗaura a samu mutum biyu zuwa uku su rakara ɗakin ta!. Abin nan ya ƙonawa HEEDAYA da Umma rai sun so su raƙashe amma babu hali.

Hanya HEEDAYA ta sata ta tafi ƙunshi na gani na faɗa, aka mata saloon tare da ƙananan kitso aka yaryara mata. Maganin mata tamkar zai yi magana haka aa dirka mata ban da maganin matsi duk da tana budurwa amma wai gwara ya jita zam-zam ya san da bambanci da tsakanin ta da matar sa marigayiya, don Umma ta faɗa mata cewa matsawar namiji ya taɓa aure to sai mace ta zage dantse wajen gyara don kar ya ji matarsa ta fi ta komai.

A yau aka ɗaura aure tsakanin HEEDAYA Bashir da ABDULHAKEEM Mukhtar, Umma an ci leshi wanda suka yi anko  ita da Hajiya Aisha da Ihsan da kuma amarya amma ban da Aunty Hafsa don basu ma faɗa mata ba bare ta saya. Da daddare amarya ta ci gayun ta bayan ta yi wanka, ranta fari ƙal yau za su angwance da ango. Momma, da wasu mata biyu su ne masu rakiyar amarya, su Abba da Daddy suka umarta a ka ɗauki mota biyu suka tafi kai amarya Hajja tana ta sanya albarka. Ran Ammie da Momma baƙiƙƙirin don komai an kwashe na Aunty RABEEYA an jera sabo na HEEDAYA.

Zaune take a tsakiyar gadon ta, tana ta murmusawa ita kaɗai ta daɗe a rayuwar ta bata shiga farin ciki makamancin wannan ba, ji take tamkar an mara albishir da aljanna. Tabbas ta ci alwashin yau za ta mantar da Ya ABDUL tunanin tsohuwar matarsa da ta daɗe a kushewa!.

Wacce ya kasa daina tunanin ta, yau za ta nuna masa tsantsar so da wayewa a yau take so ta tanadi filin da za ta fara ginin tubalin soyayyar ta a zuciyar sa.

Lullube take da mayafin ta da yake ta fitar da sassanyan ƙamshin turaruka masu tsada da daɗin ƙamshi. Karan buɗewar get ta ji wanda ya sa ta ji wani sanyi a ruhinta don ta tabbatar masoyin ta ya ƙaraso. Jim kaɗan ta ji ƙaran buɗe ƙofar babban falon, sai kuma ta ji an turo ƙofar ɗakin da take ciki, bakinsa ɗauke da sallama cikin muryar sa da take mata daɗin sauraro, idanu ta lumshe tare da saisaita muryar ta ta mata lanƙwasa ta amsa sallamar tana jin wata ƙaunarsa na fisgarta. Babu zato babu tsammani ta ji wani abu da ya so hargitsa ƙwaƙwalwar ta, wato kukan yarinya ƙarama. Da sauri ta yaye mayafin da ya mata shamaki da ganin komai duk da bashi da wani kauri amma ta fi so ta ga wannan abin mamakin da yake shirin faruwa.

Zaton da ta yi ne ya zama gaskiya domin kuwa tabbas Little RABEEYA ce shimfiɗe a kafaɗar Ya ABDUL yana jijjigata.

"Yi shiru kin ji my Little RABEE " Ya ce yana ajiye wata ƙaramar akwati wacce ba sai an tambaya ba kayan yarinyar ne a ciki don da ɗaya hannun yake jijjigata ɗaya kuma yana riƙe da akwatin. Haushi, baƙin ciki haɗe da mummunan takaici ne lokaci guda suka daki zuciyar HEEDAYA.

Ranar da ta ci buri iya rayuwar ta? Rana ɗaya tamkar da dubu a wajen ta? Ranar amarcin ta? Ranar da ta so shayar da mijin ta ruwan ƙauna? Ranar da take so ta bayyana masa irin nisa da nutson da ta yi a bege da ƙaunar sa. Amma ya taho mata da yarinya, dama dawowar yarinyar ba sai bayan shekaru ba ne? Dama a ranar yau ne ranar tariyar ta za su tare tare da yarinyar, yarinyar nan mai shegen kukan dare zai ɗakko ya kawo mata mai za ta yi a yau ɗin raino ko amarci?

Ango kuwa ko a kwalar rigar sa bai ma lura da yanayin firgicin da amarya HEEDAYA take ciki ba, gadon ya ƙarasa ya kwanta tare da ɗora Little ɗin a saman ƙirjinsa yana jijjigata yana lallashin ta. Baki sake HEEDAYA take kallon sa wato bai ma san abin da ya mata ba bai gane ya ci mutuncin ranar amarcin ta ba shi ta ƴarsa ma yake wato tana ganin Aunty RABEEYA ta mutu ashe dai ga wata RABEEYAR za ta hana ta rawar hantsi tana ganin ta kashe miciji ashe dai bata sare kansa ba lallai akwai badaƙala!!!.

*SAURAN SHAFUKA KAƊAN NA GAMA FREE PAGES DUK MAI SON KARANTA BONONO

HAR ƘARSHE ZAI BIYA 500 DON IN SAKA SHI A GROUP IDAN KUMA NA GAMA CMPLT DOCMENT 700 ne.  WANDA YAKE BUƘATA ZAI IYA BIYA TUN YANZU KO SAI AN KAMMALA FREE NE MA TO GA DAI ACC ƊIN DA ZA A TURA FAIZA ABUBAKAR 9030283375 OPAY SAI A TURA MINI SHAIDAR BIYA TA 09013181851*

MAMAN AFRAH
09013181851
[2/19, 5:22 PM] MOM MASHKUR & AFRAH:
https://chat.whatsapp.com/BxScHoTf7PzDHEWZgZCnnf

BONONO

(RUFIN ƘOFA DA ƁARAWO)

NA

MAMAN AFRAH

First Class Writer's Asso.📝

*SADAUKARWA*

Daga farko har ƙarshe sadaukarwa ne ga MARYAM SANI HAFIZ (Merry tah) Alkairin Allah ya kai gare ki Allah lulluɓe rayuwar ki da tarin ni,imomi da albarkatu Allah raya mana Abdallah fatan alkairi.

Daga marubuciyar:

Ruɓaɓɓiyar igiya
Ƴan adaidaita sahu
Ungozoma
Ƴar zaman wanka
Ƙara'in inna delu
Beelal
Jalli joga
Da sauran su.
*09013181851*

PAGE 13

*HEEDAYA*

"Ya ABDUL ya na ganka da Little RABEEYA?" HEEDAYA da ta sha yaƙi da zuciyar ta ganin ta danne zugin da zuciyar ta take mata da azalzalar ta ta faɗa tamkar ta sake kuka don a halin yanzu marar ta ma ciwo take mata saboda ɗimbin magungunan da ta bankama tsabar son ta burge shi kowanne magani over dose ta yi.

"Na kasa haƙuri in taho in bar ta ne, kin san a cikin gidan nan da Hayatiy na fara rayuwa sannan daga lokacin da ta bar duniya ban ƙara sha'awar zaman gidan ba shi ya sa yanzu ma da zan dawo na taho da Little hakan zai rage mini kewar mahaifiyar ta, kin san komai nake yi a rayuwata da tunanin Hayatiy nake yi  haƙiƙa a zahiri ta mutu amma a baɗini ina jin ta tamkar bata mutu ba don ni da so da ƙaunar ta nake rayuwa kuma da shi zan mutu" Ya kai ƙarshen maganar hannunsa biyu suna dafe da bayan Little idanun sa kuma suna kafe da silin. Sororo ta yi tana kallon sa tare da mamakin kalaman sa sai da ya yi maganar nan ne ta gane kenan ita bosho ce kenan bata ma da wani amfani tun da da son marigayiyar mayar sa yake rayuwa sai dai ya maje bata bari ya gane ba don dole sai ta fara koyawa kanta kissa wajen zaman gidan nan don ta lura abin na Ya ABDUL ba na ƙare ba ne.

"Allah jiƙan Aunty RABEEYA ya sa ta huta" Ta ce cikin sanyin murya don ta san vata da mafita sai faɗar hakan tun da hatta boka ma ya ce ba za a iya cirr masa so da tunanin su ba kuma dama bokan ne ƙarfin dum wani sheɗanci nasu.

Har ƙarfe sha biyu idanun su biyu ana fama da Little ta ƙi kwanciya daga ya tarki ajiye ta sai ta tsanyara kuka. HEEDAYA kamar ta kwaɗawa yarinyar mari haka take ji amma ta ba kanta haƙuri.

"Buɗe jakar ta akwai madarar ta ki je kicin ki ɗora ruwan ɗumi ki haɗa mata" Ya faɗa ba tare da ya kalli inda take ba abin takaicin a matsayin ta na sabuwar amarya ko kallon soyayya bata samu daga ango ba kai idan ba ƙarya idanun ta suka mata ba sai ta ga tun da ya shigo ma bai kalle ta ba. Jin aikin da ya saka ta, tamkar ta rusa ihu ita da take amarya za a lallaɓa ta a buɗe mata mayafi ya lallashe ta ta yi shagwaɓar ta son ranta amma ta ƙare a shiga kicin ango ya ƙare a reno? Da to ta amsa ta ɗauki madarar har da fida a ciki ta fita bayan ta ɗauki wayar ta da yake gidan ba baƙon ta ba ne haka ta nufi kicin ɗin cike da takaici.

"Umma" Ta ce tare da rushewa da kuka bayan Umma ta ɗaga wayar.

"Haba HEEDAYA na kira ki ya fi sau goma amma baki ɗauka ba" Umma ta faɗa tana sauraron ta.

"Wayar ce a silent kin san ina zaune kan gado a lulluɓe ina jiran dawowar sa ya buɗe ni irin na amare masu gata amma shi ne...

"Wai gidan uban wa ya kai wannnan marainiyar ƴar tasa?" Umma ta katse ta don ba ita ce maganar da take son ji ba.

"Gidan nan mana Umma  har yanzu ko yarda bata yi ya ajiye ta ba, yanzu ma kin ganni a kicin wai in dafa ruwan zafi in haɗa mata madara"

"Sha biyun daren ne kike a kicin? Ni ma ina nan na fara jiyo hayaniya ashe wai ɗaukan ƴar ya zo ita kuma Hajiya Baturiya ta hana shi ita wai sai ta girma shi ne fa Alhaji ya ce ko ta haɗo kayan da yarinyar ta ba ABDULHAKEEM ɗin ko kuma ta fuskanci tsatstsauran hukunci daga gare sh, babu shiri ta ɗauko ta bashi tana kukan rabuwa danyarinyar, ai wallahi ABDULHAKEEM ɗin na an yi shegen yaro ni na fi tunanin ma uwar sa ce ta zuga shi don a kai miki reno a hana ki sakat'

"Cewa ya yi wai saboda ba zai iya zama a gidan da babi Aunty RABEEYA ba shi ne ya taho da it...

"Rabu fa shege gulmamme in ma uwar tasa ce ta saka shi ai ba zai faɗi gaskiya ba raba kan ki da na miji wani munafuki ne ya fi wasu matan ma munfurci"

"HEEDAYA, HEEDAYA" Ta jiyo yana rafka mata kira, ga daga kicin ɗin ma tana jiyo kukan yarinyar haushin kiran sunan ta da ya yi ya tokare mata zuciya wato ita ɗan sunan soyayyar ma ba za ta samu a kira ta ba.

"Umma sai da safe yana kira na"

"To HEEDAYA Allah ɗora ki a kan yarinyar nan ta yarda ya ajiye ta in ba haka ba ɗan amarcin nan ma na daren farko sai dai kike jin labari wajen ƙawaye" Umma ta ce tana yanke kiran dama takaicin ɗaukan yarinyar da ABDUL ɗin ya yi shi ya hana ta bacci take zaune tana tunani.

Jin abin da Umma ta ce ya ƙara ɓatawa HEEDAYA rai don ta faɗawa su MEEMA ita yau sai kwanan amarci ita da yake MEEMA ta yi auren ita da RAUDA sai suke ta mata dariya suna cewa za ta sha amarci ashe dai ita raino za ta sha don babu alamar za ta adar da wani abin arziƙi, wannan shi ne karin maganar da bahaushe yake cewa babu niyya ango ya kwana da wando.

Madarar ta kai masa ta tarar shi tsaye yana zagaya ɗakin tana kafaɗar sa sai lallashin ta yake har da ƴat waƙa yake mata, shi da alama ma cikin nishaɗi yake wannan ya ƙara ƙona mata rai.

"Yawwa my Little RABEE za ki sha madara ai ko uhm yarinyar kirki mai kama da maman ta" Ya ce yana zaunawa bakin gado ya ɗora ta cinya tare da karɓar fidar sai da ya kara a gefen fuskarsa don ya ji ko da zafi sai ya ji za ta iya sha, wannan ya ƙara ɓatawa HEEDAYA rai wato yana ganin ma za ta iya kawo mai zafin da zai ƙonawa yarinyar baki.

"Za ta sha mana yarinyar kirki ce ai" HEEDAYA ta ce tana ƴar dariyar yaƙe a fakaice kuma tana aika musu harara. Yarinya ta zuƙe madara tas ta saki gyatsa amma ta daina kuka sai wasa da take tana ta ɓangalawa uban dariya shi kuma sai farin ciki yake yana dariya tamkar yana magana da sa'an sa haka yake mata magana ita HEEDAYA rabon ma ta ga yana dariya haka tun kan Aunty RABEEYA ta rasu.

Haka nan suke zaune HEEDAYA tun tana doguwar hamma har ta gyanyaɗi ya fara ɗiban ta bata san ta ɓingire bacci ba sai wajen ƙarfe huɗu saura ta tashi ta gan shi rungume da ƴarsa suna bacci. Takaici duk ya ishe ta wato ƴar ta yi bacci maimakon ya tashe ta matsayin ta na amarya shi ya kwanta bacci abin sa ita sai yanzu ma ta tuna cewa ana kawowa amarya kaza da kayan maƙulashe amma shi daga jakar ƴarsa sai ƴar tasa ya shigo ƙwafa ta yi ta juya musu baya ta koma bacci.

Ko da asuba da ya tashi ya tashe ta ya tafi masallaci. Ganin yarinyar tana ta bacci tamkar dai wata matacciya wato ta hana su bacci ita yanzu tana ramako. Sai da ta je har gaban ƴar ta saka hannu ya dungure mata goshi.

"Shegiyar yarinya tun kina zanen goyo kin iya kissa da kisisina da taya uwarki kishi, wato kika ƙi bacci kika hana mu cin amarci sai da kika ga gari ya kusa wayewa kika kwanta kamar kasa kike bacci. Little kuwa da yake bacci ya ci ƙarfin ta ko dingurin da aka mata bata ji ba bare ta falka

Tana idar da sallar ta kwanta baccj tana jiyo muryar Ya ABDUL a falo da ya dawo daga masallacin maimakon ya shigo ya zauna yana karatun qur:ani ita dai har bacci ya ƙara surar ta bata ji ya daina karatun ba.

Wajen ƙarfe takwas ya ta ji yana kiran ta idanu ta murtsuka ta tashi zaune.

Ki mata wanka ki haɗa mata madara ta sha" Ya ce tana miƙa mata yarinyar sai wasa take tana dariya abin ta tamkar dai ba ita ce ta rufe ido take kuka da dare ba. Dakyar ta lallashi kanta ta karɓi ƴar zani ta ɗauka a jakar kayan ta ta goya ta ta nufi kaicin ta ɗuma ruwan wankan, fidar ta zo ta ɗauka ta wanke ta ƙara haɗa mata madarar sai ta ajiye ta je za ta mata wankan, ta cika famfas ɗin da kashi takaici HEEDAYA har da ƙwallar ta. Haka ta wanke mata ta mata wankan ta saka famfas ɗin a shara. Shirya ta yi ta zauna ta bata madarar yana zaune yana danna waya da yake yau lahdi ma babu inda zai je.

"Akwai turarukan ta cikin jakar ki shafa mata" Da to ta amsa ta ɗakko ta shafa mata, ita ma wankan ta yi ta je ta haɗa break fast ta kawo suka ci. Kwantar da Little ɗin ya yi ya haura sama ya yi wankan ya shirya ya fito ya buɗaɗa ƙamshi. Ta lura ma dawowar yarinyar kusa da shi kamar ma damuwar sa ta ragu don sai wani ɗan walwala take gani a fuskar sa.

"Bari mu je mu gaishe da Ammie" Ya ce yana ɗora Little ɗin a kafaɗar sa. Da a dawo lafiya ta raka shi tare da cewa ya gaishe da Ammien. Ita mamaki take yi ma da yakr iya tuƙi da yarinyar a hannun sa ko kuma a kujera yake kwantar da ita shi ya sani. Tabbas sai ta yi maganin wannan tatsitaiyar yarinyar don ta ga yanzu ita ce kishiyar ta wato ma maimakon ita amarya ya fita da ita sai wata yarinya hmmm!.

Yana fita ta ɗau waya ta kira Umma suka gaisa ta kwashe komai ta faɗa mata Umma tana ta faman faɗin dole a samo mafita. Suna gama wayar ta kira MEEMA.

"Inyee amarya mau maganar sugar har an tashi kenan na ɗauka ku manya manya sai sha biyun rana ko ƙarfe uku saboda amarci" Ta ce tana dariyar wasa.

"Hmmm!. Bari ke dai MEEMA" Ta ce tana kwashe komai ta faɗa mata.

"Kan uba!. Kuma kika yarda?"

"To ya zan yi?"

"Sai ka ce ba mace ba kika zauna ranar farin cikin ku ta tafi a banza da ya baki madarar bakya samun maganin bacci ki haɗa mata a cikin madarar shegiya ta ɗaɗɗaka ta ringa bacci kamar matacciya ku kuma ku raƙashe amarci abin ku" Shiru HEEDAYA ta yi tana sauraron MEEMA jin ta zo mata da abin da ita da Umma basu hasaso ba.

"Wallahi kwanyata toshewa ta yi jiya ko kaɗan ban yi wannan tunanin ba kuma bana jin akwai maganin mura a gidan nan amma zan ba me gadi ya siyo mini yau in ɗirka mata haba ina dalili"

"Ko ke fa ai in ya san wata bai san wata ba, namiji ai ya kasance a tafin hannun ki shi ne amma ba wai ki zauna yana mulkar ki ba, duk wannan jiji da kan nasa sai kin cire masa su"

"Kin san waye Ya ABDUL kuwa?"

"Shi ba namiji ba ne? Ai boka ya gama miki aiki tun da har kika zama matar sa yanzu kuma sai ki tashi da kan ki ki ƙarasa aiki, ki murza kambunki yadda kowace mace take murzawa kar ki zama bora a cikin mata"

"Sai luluƙani daji kike ni ban fahimci kurman baƙin nan da kike faman karanta mini ba ki mini dalla-dalla"

"Magungunan mata za ki nema na mallaka da duk wanda kika ji ana gara kan namiji daga nan salon wasan zai sauya, akwai wani group na MANYAN MATA da nake ciki zan saka a sanya ki ki shiga ki ga yadda ake bajin ta ki ga yadda mata suka zama sarakuna kuma gimbiyoyi a gidan mazajen su babu ruwan su da ɓacin rai da wulaƙancin  namiji rayuwar turawa suke namiji yana nan-nan da su yana buɗe musu bakin aljihun sa, sannan tarairaya sai kin ce bakya so"

"Don Allah MEEMA?"

"Wallahi kuwa yanzu bari zan ba direbana magani ya kawo miki yanzun nan tun da ba ya nan ya fita, ƙulaƙulai ne guda uku sunan sa uku bala'i a ƙasan ki za ki saka su narke maganin mallaka ne namiji ko kan dutse gare shi kan tauri sai ya ladabtu sai ya zama raƙumi da akala"

"Dan Allah turo mini MEEMA wallahi wannan in ban tashi tsaye ba na ga alama ko ƴar soyayyar nan ta amare da ake nuna wa mata sai dai in ga ana yi kuma don Allah ki saka a saka ni a group ɗin don ni har na matsu na je na fara ganin me ake yi a ciki"

"Yanzu zai kawo miki ai mazan ne sai da tashi tsaye ana haɗa musu tarko amma in ka tsaya kallon ruwa tuni kwaɗo yake maka ƙafa, ai hatta ƴar nan tashi sai dai ki ɗakko mai reno take kula da ita amma matsayin ki ya wuce a ce kin zama ƴar wankin kashi, amarci ne ya fi dacewa da ke"

"Shi sa nake son ki MEEMA ta in na mallaki Ya ABDUL na gama warkewa a duniyata na samu komai ai ni wallahi in dai zai nuna mini ƙauna da kulawa to wallahi ko haihuwa ba zan yarda in yi a kwana kusa ba bare har na yi saurin tsufa, sai na gama cin duniyata da tsinken tsire"

"Yo ai dama haihuwa mayar da soyayya baya take yanzu ba ƴarsa ce ta hana ku morewa jiya ba to in ɗanku ne ma haka zai hana ku soyayya daga kun fara soyayya cikin dare ɗa ya tashi ya yi ta tsallara ihu sai dai ki haƙura ki bashi shiga shayar da yaro shi kuma miji ya ƙullace ki don ya shirya yin uzuri sa ɗa ya hana shi, in kin ga kin sake sai kin yaye yaro wataƙila kina yin yayen wani cikin ya kawo kai shukenan fa ke sai haihuwa da reno shi ya sa namiji in ya ga ba ya samun mai yake so sai ya ɗirko miki kishiya...

"Bari faɗin haka ni kin san na tsani kishiya"

"To ai kowace mace ma bata son kishiya sai dai dole don haka yanzu shawara ta ragewa mai shiga rijiya" Haka ta ringa mata kuɗuba ita kuma ta hau ka ta zauna. Suna gama wayar jim kaɗan ta mai gadin gidan ya zo ya mata nocking ya ce mata an aiko wani direba. Saƙon ya karɓo mata cike da murna ta dawo ciki tana ta tsara yadda komai zai wakana. Bayan ta yi wa maganin maɓoya ta dawo falo ta kwanta ta hau whatsapp ai kuwa ta ci karo da sunan MANYAN MATA group sai sannan ma ta tuna da shi ne group ɗin da MEEMA ta ce za a saka ta cike da murmushi da kuma son ganin mai ake yi a ciki ta shiga. Saƙonni ne suke ta shigowa.

Ai sai yanzu na matsa masa ya fita.

Wata kuma ta ce
Ai wallahi mu dai babu ruwan mu da matsalolin gidan aure ai in namiji yana nuna maka soyayya ji kake babu ya kai sannan baka da wata damuwa. Yadda kowacce take fitowa tana faɗar yadda alaƙar ra take da mijin ta abin ya birge HEEDAYA irin rayuwar da take mafarkin samu.

MEEMA ce tana hawa online ta shiga group ɗin ta gabatar da HEEDAYA matsayin ƙawarta. HEEDAYAR ma magana ta yi tana yi wa MEEMA godiyar gabatar da ita tare da cewa Allah sa su ƙaru da juna.

"Barka da zuwa sister" HUSNA ta yi tagging na maganar HEEDAYA ta mata barka da zuwa amsawa ta yi tana godiya daga nan duk aka shiga mata sannu da zuwa. Ta ji daɗin yadda aka tarɓe ta sannan kuma ta ƙara mamakin yadda kowa yake faɗar sirrin sa na zamantakewar auren cikin group ɗin tabbas idan ta cigaba da zama a yadda ta fara a gidan Ya ABDUL lallai za take shaƙar baƙon ciki yadda matan MANYAN MATA group suke faɗar zamantakewar su da mazajen su ya tafi da ita sannan hakan ya sa ta ɗaura ɗamarar ƙwato nata ƴancin a gidan miji!.

Wayar ta ajiye ta ajiye bayan sun yi magana da MEEMA a private tana ta faɗawa MEEMA mamakin dama ana samun haka irin wannan kulawar da matan group ɗin suke bada labari nan ta tabbatar mata da kaɗan ta gani ta cigaba da zama a group ɗin za ta ga zahiri ma. Da wannan ta shiga kicin ta yi girki, basu shigo gidan ba sai la'asar ya ce ya ci abinci a gidan Hajiya da yake ma bacci Little RABEEYA take sai ta karɓe ta ta kwantar da ita don ya ce ta sha madarar ta a can.

Da dare ko da ta tashi haɗa mata madara a kicin dama ta akiye maganin tarin da ta ba mai gadi ya siyo mata na yara a cikin madarar ta zuga ta gauraya sannan ta saka a fidan ta ba yarinya ta sha sai kuwa bacci ya ɗauke ta ta kwantar da ita. A bayi ta saka uku bala'in wajen MEEMA. Yana ta danne danne a waya har sai da ya kammala ya kwanta ta ɗauki ƙaramar kafifa ta shimfiɗa a ƙasa ta ɗauki Little za ta mayar da ita can.

"Dama ba ke za ki kwanta a katifar da kika shimfiɗa ɗin ba?" Ta ji ya jefo mata tambaya mai kama da ta rainin hankali ta ji haushi sosai amma kuma sai ta danne ta ce

"Ka san yara da juyi to ba na so ne ta faɗo cikin dare wani abu ya samar mini ita" Jim ya yi sai kuma ya ji ya gamsu da maganar tata kwantar da ita ta yi a ranta tana cewa

'Ashe dai da ake cewa namiji yaro ne za ka iya masa wayo ashe dai gaske ne kin ga har na masa wayo, hmmm!. Sai ma ka ji uku bala'i ' Da dibara har sai da ta sanya burin ta ya cika!. Ba ƙaramin ƙara son sa ta yi ba kuma sai yanzu ne ta ji tana mahaukacin kishin da bata so kowace mace ta raɓar mata shi, ji take ina ma bai taɓa sanin wata mace ba sai ita amma ƙaddara ta

riga fata tun da ya auri Aunty RABEEYA ta aure shi sai dai za ta yi iya yin ta na ganin har duniya ta naɗe bai sake sanin wata ƴa mace ba don ita ce matar sa a duniya a ƙiyama ma ita take so ta zauna da shi.

Ya ABDUL tun da ya kusance ta sai ya ji wata zazzafar ƙaunar ta tana fisgar sa ya ji ya aminta da ita sai ya ji gabaɗaya damuwar da take danƙare a zuciyar sa ta washe yanzu son HEEDAYA yake yi. Zaune suke a falo suna hira irin ta masoya ya fara mata zancen Aunty RABEEYA da yadda yake jin ciwon rashin ta har yau. Amma ta ƙeƙashe ƙasa ta ce ita bata son maganar kowace ƴa mace wai kishi take ji. Yanzu kam sai yadda ta yi da shi don a yanzu wata mata ta samu wacce ta ɗan manyanta haka take rainon Little ita take mata komai kuma ba ya iya yi mata musu domin yanzu tsoron ɓacin ranta yake.

Yau ta kama juma'a don haka bayan ya shirya cikin shadda sky blue ya saka hula sai tashin ƙamshi yake.

"Baby nah zo mu yi hoto" Ta ce tana kashe masa ido ɗaya. Babu musu ya zo tana rungume da shi ya sunbace ta a kumatu ta ɗauki hoton. Sun matuƙar yin kyau don ita ma material ne sky blue ɗin mai jar fulawa a jikin ta. Har bakin ƙofa ta raka shi tana masa a dawo lafiya. Yana fita ta dawo falo ta kwanta a kan doguwar kujera ta hau whatsapp group naau na MANYAN MATA ta shiga kamar yadda ra zata haka ce ta faru domin kowacce tana turo hotunan ta da suka ɗauka da mijin ta haka suke duk ranar juma'a. Sai dai idan za su tura hoton ba a buɗe fuskar miji sai a samu ɗan emoji a rufe saitin fuskar sai dai a bar jikin sa ita kuma matar ana ganin ta tangararai. Alfanun hakan don kowacce ta nuna majinta da irin soyayyar da suke ita da mijin ta haka za a ringa yabawa kowacce ana fasa mata kai shi ya sa ma ba sa barin ƴan mata ko zawarawa su shigar musu group.

"WOW! Amma HEEDAYA kina hutawa kalli wata kulawa da ya nuna miki ji yadda ya sumbace ki" Wata ta yi magana da ta ga hoton HEEDAYA da Ya ABDUL duk da ta rufe masa iya fuskar sa amma ana iya ganin yadda suka yi hoton tana jifan sa da wani shu'umin kallon soyayya.

"Ai na faɗa miki tana shimfiɗa soyayya a gidan ta tana taka bazarta" Wata ma ta faɗa tana saka emojis na dariya. Kan HEEDAYA ne ya fashe ta tuno wancan satin video ne ta ɗauka tana bayan Ya ABDUL yana mata doki irin wanda yara suke yi wato ya sunkuya ta hau bayan sa yake zaga falon da ita, dama kuma ta saita wayar ta tana ɗaukan bidiyon, shi ta tura wancan satin a matsayin goron juma'a.

Husna wacce zuwanta yanzu kenan ta turo hoton ta ita kaɗai twna zaune a kan kujera a falo tana murmushi. Gabaɗaya aka iyo mata caaaa ana cewa ai bata more ba ita kullum sai dai ta turo hoton ta babu miji.

"Na sha faɗa musu mijina matafiyi ne ba ya zama sai ya yi wata biyu ma ban saka shi a idona ba, kuma ko ya zo ma wallahi ba shi da lokacina bare har ya kulani mu yi wani hoto ba ya girmama buƙatata ma" Kowa jajanta mata ya yi suna cewa bata dace ba wata mai shegen

surutu ta ce

"Wai shi kuwa wane irin bussines ne wannan yake tafiya har wata biyu kuma idan ya dawo na ya ƙi baki lokacin sa?, Fisabilillahi ina Kano ina Lagos?"

"Eh mana aikin kamfani, kamfani ne da shi na yin robobi"

"To ai ba kamfanin robobi ba ko kamfanin silbobi yake da akwai wata biyu ya yi yawa sai ka ce wani soja, to mai ya sa ma ba zai tafi da ke ba"

"Wallahi ya ƙi"

"Wannan da sake ni ba zan ma iya wannan rayuwar ba" Wata ma ta faɗa.

"Gaskiya kina cikin jarabawa" MEEMA ta ce tana jimantawa.

"Allah kyauta!" Cewar HEEDAYA.

HUSNA kuwa maganganun da suka yi sai ta ji zuciyar ta ta karaya don ita sai take ji ma tamkar bata da maraba da wacce bata da aure bambancin kawai ita akwai igiya a kanta kuma dai mijin yana ɗaukan ɗawainiyar ta amma da sai ta ce babu.

Tana fitowa daga group ɗin ta samu saƙon wata baƙuwar no tana buɗewa ta ga haka.

"Slm suna na HEEDAYA ni ƴar garin Dutse ce da yake jihar jigawa, ina da aure na ɗauki no ki ne a MANYAN MATA group" Amsa mata HUSNA ta yi tana mata godiya da jin daɗin ta na kulawar ta gare ta.

"Ni suna na HUSNA ni ƴar garin Kano ce sannan ina aure a Kano" Nan suka shiga taɓa hira HEEDAYA tana mai kwashe komai ta faɗa mata game da yadda za ta jawo hankalin mijin ta don har ta ce za ta saya mata uku bala'i ta aika mata Kano godiya ta ata sosai don ita ce ta uku da HEEDAYA ta ɗauki no ta bi pc tana son samun ƙawaye matan aure don yanzu duk ta watsar da ƙawayen ta ƴan mata ko Ifteehal da ta zo gidan ta warning ta kora mata a kan kar ta ƙara zuwar mata gida idan kuwa har ta ga sun cigaba da ƙawance to ta tabbbatar aure ta yi don ba za ta yi ƙawance da marar aure su ƙwace mata miji.

Yau kwana biyu kenan sa boka ya musu aiki a kan Ammie don farraƙa tsakanin ta da ɗanta kamar yadda suka yi alƙawarin yin haka. Tun da dai sun kasa raba shi da Little ɗin duk da yana son HEEDAYA amma yana nuna wa ƴarsa kulawa. Tsawon kwanaki biyun nan YA ABDUL bai je gaishe da Ammie  ba. Abin ya bata mamaki don haka ta shirya da magriba direba ya kai ta gidan nasa don ta gani ko lafiya don ko kiran sa ta yi a waya ba ya ɗauka

Da sallama ta shigo falon bayan ta yi nocking an mata izini. HEEDAYA ce zaune a kan kujera ƙafa ɗaya kan ɗaya. Chatting ɗin da ya zame musu jiki suke yi a group nasu na MANYAN MATA har Ammie ta yi wa kanta masauki a kujera amma HEEDAYA bata ce mata ko ƙala ba.

"HEEDAYA ina wuni ni in gaishe ki" Ta faɗa cikin gatse.

"Lafiya ƙalau mai ziyarar bazata babu neman izini" Baki sake take kallon HEEDAYA. Ya ABDUL ne ya fito daga kicin ɗauke da plate mai jalof na taliya da ta sha bushashshen kifi da ruwa-ruwan ta sai turiri take. Falon ya ƙaraso hankalin sa a kan HEEDAYA Ammie kuma baki sake take kallon sa ganin tamkar bai ganta ba.

"Baby HEEDA na gama dafawa baki ji yadda ta yi daɗi ba" Wani yatsina ta yi don ta ƙara ƙular da Ammie ta ce

"Sai ka ƙarasa aikin ka wato ka bani a baki"

"Abu mai sauƙi fitar da wando ta ka" Ya ce yana zaunawa kusa da ita.

"ABDULHAKEEM"

"Na'am " Ya amsawa Ammie hankalin sa a kan HEEDAYA.

"Mai ya hana ka zuwa kwwna biyu?"

"Yana tare da iyalansa " HEEDAYA ta ara ta yafa.

"Eh haka ne" Ya faɗa shi ma.

"Ko gaishe ni ba za ka yi ba ina RABEEYA ƙarama?"

"Tana wajen mai renon ta" Ya ce ba tare danya mata maganar gaisuwar ba.

"Ina so ka gaishe da ni" Cewar HEEDAYA zamewa ya yi daga kan kujerar ya durƙusa a kan gwiwoyin sa ya ce

"Habibty ina wuni" Tsabar mamaki bakin Ammie ya ƙi rufuwa.

*HAFEEZ*

"Wallahi Kaka ban san da wannan maganar ba ki yarda da ni" Ya faɗa cikin ruɗu.

"Waye zai yarda da kai ai tantsuwar ka ba za ta samu shiga a waje na ba, kuma wallahi na baka mintina ƙalilan ka zo in ba haka ba zan mata korar kare don ni babu mai ɓata mini sunan zuri'a" Tana gama faɗar haka ta yanke kiran. Gabaɗaya ya haɗa zufa, ga tarin mamakin da ya dabaibaye masa zuciya, tambayoyi barkatai da ba shi da amsar su, su ne suka taru suka masa yawa.

"Innalillahi wa inna ilaihi raji'un" Ya faɗa yana dafe kai da hannu ɗaya, tare da saka hannun cikin gashin kansa ya hautsina.

"MARAYAMA ta ciki? Kai impossible" Ya ce a fili tare da jefa wayar aljihun sa, tare da ɗakko mukullin motar ya fito daga ɗakin ko laptop ɗin bai rufe ba. Ƙofar gidan ya kulle ya shiga motar ya fige ta a guje. Gudu yake shararawa a kan titin tamkar zai tashi sama fatan sa da burin sa bai wuce ya isa cikin garin Dutse ya sauka a gida kafin Kaka ta cika abin da ta faɗa na ƙudurta in bai iso da wuri ba za ta yi wa MARYAMA korar kare.

Ya sani idan ta kore ta babu tabbas ɗin ya sake sanyata a idaniyar ta tun da bai san ina za ta nufa ba, kazalika ya san Kaka ba za ta yi shaci faɗi ba bata magana a kan abin da bata tabbatar ba sai dai yana shakku a kan cewa MARYAMA tana ɗauke da ciki. To wa ya mata? Ya aka yi bata faɗa ba ta yaya ma hakan ta faru wace irin ƙaddara ce wannan da take son shiga tsakanin sa da ƙaunar MARYAMA bayan ya gama mutuwa a kan son ta, yana tsara ranar da zai sanar da ita tare da bayyanawa Kaka ƙudurin sa na auren sa ashe dai akwai ƙurar da bai sani ba.

"Shin mai ya sa kika ƙara yi wa kan ki baƙin fanti bayan wanda kike ɗauke da shi?" Ya tambayi kansa a fili yana dukan Sitiyarin duk gudun da yake shararawa kan titi sai ya ga kamar ma ko sauri ba ya yi bare a yi zancen gudu.

MARAYAMA tun daga lokacin da ta ji Kaka ta kira shi a waya tana faɗa masa tana da ciki kuma za ta mata korar kare. A take ta zube a kan gwiwoyin ta tana faɗin

"Don Allah Kaka ki yi haƙuri kar ki kore ni ban san inda zan je ba, bani da kowa bani da komai sai ku sai Allah" Ta ce tana miƙa hannu za ta kama ƙafar Kaka. A zuciye Kaka ta saka hannu ta doke mata hannu, tana nuna ta da yatsa ta ce

"Ai ko ke ce kaf duniya babu wanda ya rage sao mu da ke to na cire ki a kan ma'amala da mu, ina miki kallon salaha ashe dai lumbu-lumbu ce ke wutar ƙaiƙayi?"

"Mero, mero, mero" Kaka ta shiga ƙwala mata kira amsawa ta yi tare da shigowa da sallama ganin Kaka tsaye ƙiƙam rai ɓace sai huci take ga MARYAMA zaune tana kuka da magiya sai ta ji ranta babu daɗi.

"Don Allah ki saka baki kar ta kore ni wallahi ban san inda zan je ba kuma wallahi ni ma ban san wanda ya mini ciki ba da shi na ganni wallahi ban san ya aka yi ba" Ta faɗa tana kuka tana kallon Meron da mamaki ya kashe.

"Ciki!!? Wane irin ciki?" Ta tambaya da mamaki.

"Ciki dai na haihuwa ta tashi ki duba ta har idanun ta ki duba ki duba marar ta ma"

"Innalillahi wa inna ilaihi raji'un" Ta ce ganin zahirin abin da Kaka ta ce

"Ko a garin mahaukata babu wanda zai ce ya tsinci ciki a jikin sa kuma shi ma munafukin zai zo ya same ni, da ya ɗauka zai yi wasa da hankali da tunanina a yau sai kun bayyna gaskiya wai baki san ya aka yi kika samu ba sai ka ce a garin mahaukata in shi ya kitsa miki yadda za ki faɗa ma asirin ku zai tonu" Kaka ta faɗa rai ɓace Mero tana ta bata baki amma bata sauraron ta.

HAFEEZ ko da ya shigo garin Dutsen bai rage gudu ba, ana buɗe masa get ko parking bai gama ba ya fito ba tare da ya rufe ƙofar ba ya shige gidan, mai gadi yana masa sanu da zuwa ko ta kansa bai bi ba. Yana shigowa ya tsinkayi muryar MARYAMA tana kuka tana faɗin ita ma bata san wanda ya mata ciki ba. Jingina ya yi da bango yana dafe kai da hannu biyu ya shiga jero sunayen Allah a zuciyar sa.

'Ko mai zai faru dole na kare MARYAMA dole ni na ɗauki lafin ba zan juri ganin ta a damuwa ba, ba zan yarda a raba ni da ita ba wato a kore ta don muddin Kaka ta ji ni ma ban san da cikin ba to tabbas!. Sai ta kori MARYAMA' Ya ce w zuciyar sa, tare da yin ƙundunbala ya shige falon Kaka murya na rawa ya ce

"Cikina ne Kaka!. Ni na mata cikib kuma ba a son ranta ba fyaɗe na mata" Ya faɗa hawaye yana cika masa idanu, don shi ciwo yake ji a ransa in ya tuna wani namijin ya san MARYAMA a mace kuma har da ciki alhalin babu aure. MARYAMA da ta tsinkayi muryar sa jin abin da ya ce ta shiga tashin hankali jin zai yi wata sadaukarwa saboda ita bayan ta san ba shi ya yi cikin ba kuma ita kanta bata san cikin na waye ba.

Kaka da Mero daskarewa suka yi a wajen jin furucin sa.

Ban yi editing ba a yi hƙr da typin errors 😒

*MUNA DAF DA GAMA FREE PAGES MAI BUƘATAR SHIGA GROUP DON KARANTAWA HAR ƘARSHE YA BIYA 500 TA ASUSUN FAIZA ABUBAKAR 9030282375 OPAY*
[2/19, 5:22 PM] MOM MASHKUR & AFRAH: BONONO

(RUFIN ƘOFA DA ƁARAWO)

NA

MAMAN AFRAH

First Class Writer's Asso.📝

*SADAUKARWA*

Daga farko har ƙarshe sadaukarwa ne ga MARYAM SANI HAFIZ (Merry tah) Alkairin Allah ya kai gare ki Allah lulluɓe rayuwar ki da tarin ni,imomi da albarkatu Allah raya mana Abdallah fatan alkairi.

Daga marubuciyar:

Ruɓaɓɓiyar igiya
Ƴan adaidaita sahu
Ungozoma
Ƴar zaman wanka
Ƙara'in inna delu
Beelal
Jalli joga
Da sauran su.
*09013181851*

PAGE 14

*AMMIE*

Da mamakin HEEDAYA da ABDULHAKEEM ta bar gidan don ko Little RABEE ɗin babu wanda ya kawo mata ita sai dai ta san cewa tabbas!. Wannan ba ABDULHAKEEM ɗinta ba ne domin shi wancan mai tsananin biyayya ne da girmama ta, amma ta san yanzu an sauya mata shi wannan ta guda shi ya sa bata so auren sa da HEEDAYA ba don ta san babu mutunci a lamarin HEEDAYA da uwar ta. Sai dai babu wanda ta sanar ta je ta kama addu'a a kan Allah ya dawo mata da hankalun ɗanta jikinsa kuma ta san Allah maji roƙo ne sai dai a samu jinkiri.

HEEDAYA da Ummar ta duniya ta musu daɗi suna cin kare su babu babbaka, musamman HEEDAYA da ta kasa ta tsare a gidan mijin ta kambunta kawai take murzawa shi kuwa ABDULHAKEEM ya gama mutuwa a kan son da aka sanya masa na ƙarfi da yaji wato ta bin bokaye da malamai da kuma mallake -mallake na magungunan mata waɗanda basu da alƙibla. Domin yanzu HEEDAYA ta yi ƙaurin suna a wajen zuwa malamai daman an ce barewa ba za ta yi gudu ɗanta ya yi rarrafe ba

Alaƙa ta yi ƙarfi tsakanin ta da HUSNA yanzu kaf online bata da aminiya kamar HUSNA kuma nan ne wajen baje kolin gabaɗaya katafanin sirrin gidan auren ta. Duk da suna baje hajar sirrikan gidan auren su a group a nasu ganin ai ba sanin juna suka yi ba don haka don wani ya san sirrin wani ba wani abu bane duk da cewa gabaɗaya sirrin da suke faɗa a group ɗin abu ne na daɗin da suke fuskanta a gidan aure. Kaf group ɗin MANYAN MATA yanzu sun yarda cewa HEEDAYA ta fi kowa yin yadda take so a gidan mijin ta kowa tana bashi sha,awa don nata samun ya zarta hankali gabaɗaya ta mayar sa mijin ta sauna ko kuma shashasha bashi da burin da ya wuce faranta mata don ita kaɗai yake kallo, ya manta da mahaifiyar sa da sauran duk wasu abubuwa komai nasa HEEDAYA sai dai duk abin nan da ake abin bai yi tasirin rabuwa da ƴarsa ba yana bata kulawa duk da hakan ma HEEDAYA ta saka a ranta sai ta saka Little RABEE ta zama tarihi a zuciyar sa don da ita take kishi a yanzu ita kuma ta fi so ya zamana daga ita sai ƴaƴan da za ta haifa nan gaba ne take so su kasance a zuciyar sa, tun da a halin da ake ciki yanzu babu haihuwa a tsarin ta a cewar ta sai ta gama cin duniyar ta da tsinken tsire don haka ma take yin tsarin haihuwa wato planning.

Umma yanzu babu abin da take sai turawa Momma haushi saboda ta san Momma ta ɗauki son duniya ta ɗora a kan Little RABEE amma kuma an ƙwace ta a hannun ta yanzu tana hannun su tun da HEEDAYA ce a gidan ita kuma wannan abun yana ci mata tuwo a ƙwarya.

"Aminiyata Husna wallahi shaƙuwata da ke na ɗauke ki tamkar ƴar uwata shi ya sa nake kwashe duk wani abu da ya shafe ni nake faɗa miki, yanzu ina so ma in saka rana in zo har garin kano domin in ganki a zahiri ba kamar yadda muka san juna a hoto ba" HEEDAYA ta tura mata saƙon lokacin suna chatting.

"Allah sarki ai ni ma na matsu mu haɗu yadda muke ɗin nan babu abin da bamu sani ba da ya shafi rayuwar mu ya kamata wani ya ziyarci wani"

"Kar ki damu tun da shi HAMEED ba zai kawo ki ba tun da ba shi da lokacin ki ni zan saka ABDULHAKEEM ya kawo ni"

"Ka ji matar so wallahi aminiyata soyayyar ku tana birge ni kin tsinci dami a kale a yanzu ba duka maza ba ne suke ba mace kulawa da soyayya ta zama tana cikin jin daɗin rayuwa kamar

yadda kike ji, kina gani dai hatta uku bala'in da kika aiko mini na yi amfani da shi a banza duk da dai an samu sauyi amma dai ke kam ta dabance ina fatan Allah ya ƙara ɗora ki a kan mijin ki har ƙarshen rayuwar ku"

"To amin amma dai ni kin san ba zan taɓa yarda na zauna namiji ya ci abinci a kaina ba duk wani cin kashi ya mini ba"

"To ai ba daga macen ba ne kowace mace za ta so ta samu komai na rayuwar aure da kwanciyar hankali da kulawa da soyayya sai dai idan bata samu ba ya za ta yi?" HUSNA ta jefa mata tambayar.

"Ni ai kin san bana zama kullum kuɗina suna wajen malamai da bokaye ai kuwa ina ganin biyan buƙata don ga shi da ƙorafin gidan aure sai dai in ji ana yi"

"Haka ne amma ni ba zan iya bin malamai da bokaye ba a kan namiji in ɓata lahirar ta don hakan shirka ne"

"Yo ai sai ka nemi gafara ni kam gwara in gwara kan namiji yanzu fa Ya ABDUL ko uwar da ta haife shi sai na ga dama nake barin sa ya je gaishe ta in ma ya je sai dai in ni na masa umarni in bam bashi ba kuwa wallahi ko za a ɗauki watanni ko gidan su ba zai je ba ke ko kallon gidan ba zai yi ba ga shi dai zai je gidan mu gaishe da uwata amma ba zai shiga gidan su ba sai in ni na ce kin ga kuwa ai kwalliya tana biyan kuɗin sabulu don in ba haka ba da yanzu na zama sorry a gidan nan"

"Kina yadda kike so aminiyata"

"To ke ya kika gani, ai shi ya sa daga ni babu ƙari ke ni fa na saka a raina dama a duniya dai babu wata mace da Ya ABDUL zai mata kallo na so ke har jaddada masa nake cewa ko fita ya yi kar ya yi wa kowace ƴa mace kallo sau biyu, ya kan ce mini ai in ma daina tunanin zai ga wata mace da sunan so don daga ni ya rufe ƙofa har gaban abadah"

"Kin ciri tuta ai nake faɗa miki matsalar mata kishiya ce don baka ƙara sanin mene ne zaman aure sai kana da abokiyar zama"

"Hahaha! Ai ni dama don ma na san babu ita a tsarina ba zan taɓa ma yarda ba Ya ABDUL nawa ne na ni kaɗai!. Don ni aka halicce shi, wallahi duk ranar da na buɗi ido na ga an mini kashiya ko ta ɗiyar kara ce na tabbata mutuwa zan yi"

"Ai shi ma ba zai ma fara ba kawai ki cigaba da gashi kuma ki saka a ranki baki da kaishiya a gidan auren ki don kin kasa kin tsare aminiyata"

Waɗannan kalaman ne suke sanya HEEDAYA ta ji kanta ya fashe a duk lokacin da HUSNA ta mata su ƙawa ɗaya tamkar da miliyan a cewar ta kenan yanzu yadda take baje sirrin ta na

gidan aure hatta magungunan mata da yadda suke mu'amalar aure da mijin ta babu wanda take ragewa sai ta faɗawa HUSNA ko MEEMA bata sanin wasu abubuwan kamar yadda take kwashewa take faɗa mata, hatta magani in ta yi amfani da shi da yadda mijin ta ya yaba a kan yadda ya same ta sai ta faɗawa HUSNA. Ita kuma HUSNA baiwar Allah babu wani abu da take ɗauka a gidan HAMEED sai takaici kamar dai yadda aka saba don shi har yanzu bai damu danita ba ita kuma da a ce zai nuna mata kulawa ko yaya ne da sai ta ji babu ya ita a duniya kai ita ko dai zai auro mata uku ne babu ruwan ta amma dai ga shi ita bata samu komai ba daga gare shi na haƙƙin auratayyar shi ya sa ko a group ɗin idan ana hirar mazaje take jan bakin ta ta yi shiru saboda ita ko gutsuren abin da suke samu ba samu za ta yi ba haƙurin man dai shi take yi tana neman zaɓi da mafita daga ubangiji.

*BAYAN WATA BIYU*

Yau ne HEEDAYA ta shirya domin zuwa garin Kano ta kaiwa HUSNA aminiyar ta ta online ziyara kowa cike yake da ɗoki da murnar haɗuwar sa da wacce ya saba. HEEDAYA tana ta Alla-alla su isa Kano kawai so take ta ga HUSNA. HUSNA ma a nata ɓangaren haka ne ta shirya musu tarɓa ta musamman suna waya da HEEDAYA har suka iso ƙofar tangameman get ɗin gidan in da mai gadi ya wangale musu get ɗin Ya ABDUL ya kutsa hancin motar ciki.

HUSNA da ta kasa zaune ta kasa tsaye saboda farin ciki tana tsaye a harabar get ɗin, motar tana tsayawa ta taho wajen da sauri, Ya ABDUL ne ya fito ya zagaya ya buɗewa HEEDAYA ƙofa hannu ta miƙo masa ya kamo ta ta fito da sauri suka rungume juna ita da HUSNA cike da tsananin murnar haɗuwa. Shi kuwa yana ta musu dariya a haka suka saki juna HEEDAYA da HUSNA suna riƙe da hannun juna suka shige cikin gidan Ya ABDULA yana biye da su tana faɗin an nuna masa wariya. Bayan an gaisa ta gabatar musu da abinci suka ci sai Ya ABDUL ɗin ya ce zai je wajen wani abokin sa ya dawo nan HEEDAYA ta ringa faɗa masa ya kiyaye ban da kallon mace sau biyu don hakan ganganci ne da wasa da ranta sumbatar ta ya dawo ya yi a gaban HUSNA yana faɗin ai shi nata ne babu wata mace da zai iya kalla da sunan so don sauran mata ma kallon muciya da zani yake musu ita kaɗai yake wa kallon mace.

HUSNA dariya take ra musu bayan fitar sa ta ringa cewa gaskiya sun dace da juna mijin ta rana ƙaunar ta. Hira suka cigaba da yi har sai da ta dawo kafin ya fito da tsarabar da suka kawo mata tana ta godiya bayan kayan matan da HEEDAYA ta jibgo mata. Tata tsarabar ta bayar wanda kayan yara ne masu kyau ta tsada ta ce su kai wa Little RABEE da kewar juna suka rabu HEEDAYA da HUSNA suna ta ɗagawa juna hannu.

Haɗuwar da suka yi a zahiri ya ƙara danƙon zumuncin su tare da shaƙuwar su. HEEDAYA da take ɗaga kai da hanci a group tana nuna ta fi kowa shawo kan mijin ta musamman da wasu daga cikin matan group ɗin suke fasa mata kai. Yanzu tsabar jijji da kai ma har ta fara share MEEMA idan ta mata magana sai ta ga dama za ta amsa.

"Wai HEEDAYA mai na miki ne kwana biyun nan na ga ko a group na MANYAN MATA in kika yi magana na yi magana sai ki wa kowa replay ki share magana ta anya hakan daidai ne kuwa amma in wani abu na miki ki yi hakuri" Haka MEEMA ta rubuta ta tura mata amma sai bayan kwana biyu ta mata replay da cewa

"Babu abin da kika mini ra'ayi ne kawai kin san kuma hausawa sun ce ra'ayi kukan jaki"

"Ban gane ba, ai na ce ki yi haƙuri ko na miki wani laifin cikin rashin sani"

"Ni fa babu abin da kika mini"

"Wai yanzu don a kan HUSNA na ne kike share ni kar ki manta ni fa ƙawar ki ce ta kusa tare muka yi karatu kuma duk wani mataki da kika taka a gidan ABDULHAKEEM ni ce sila ko kin manta a daren ki na farko ma ko inda kike bai kalla ba? In kin manta in tuna miki hatta malamai ni na kai ki kika san wajen su suje miki aiki amma ya dace ki watsa mini ƙasa a ido, saboda wata ita fa online kuka haɗu ni kuwa tun bamu san kanmu ba muje tare...

"Dakata! MEEMA baki da hurumin da za ki faɗa mini mai zan yi a rayuwtaa, kuma HUSNA ta fiki sau miliyan a wajena an faɗa miki shi zumuncin online ɗin ba ya fin na zahiri? Sannan da kike wani yanyanyayan ɗin kin zama silar zamana wani abu a gidan miji mene ne yanzu kuma ina ne ban sani ba ni kawai ji na yi na daina ra'ayin ƙawancen da ke " Tana gama faɗar hakan ta daina buɗe saƙon na MEEMA ma. Wannan abin ya yi wa MEEMA ciwo sai dai duba da butulci irin na ɗan adam sai ta janye jikin ta daga wajen HEEDAYA ita kuwa HEEDAYA ko a kwalar rigar ta, yanzu wasu ƙawayen ma ta sake a wasu groups ɗin amma dai babu kamar HUSNA.

*BAYAN SHEKARA ƊAYA*

Yanzu Little RABEE tana tafiya ga kuma tana cin abinci sanna yarinyar sai kyawun ta haɗe da kamamnin ta da mahaifiyar ta suka ƙara bayyana in da yarinta ba sai ka ce Aunty RABEEYA ce idan ka ganta. Sai dai wani abu da ya fara ci wa HEEDAYA tuwo a ƙwarya yadda Ya ABDUL ya damu da yarinyar sosai yanzu ko gidan ya shigo sai ya ce mai renon ta ta kawo masa ita haka zai zauna ya yi ta mata wasa ko ma ya ɗauke ta su fita. Sawun ta wajen manyan malaman ta da take ji da su uku a kan a yi farraƙu tsakanin Ya ABDUL da Little RABEE amma abin ya ci tura!. Kowa sai ya ce ba zai iyu a farraƙa su ba don a nata rashin imanin so take a saka masa tsanar yarinyar a ransa yake mantawa ma da ita amma sai take ganin tamkar wutar soyayyar ake rurawa a tsakanin su ba ta ƙiyayya ba. Ta kashe kuɗi don cim ma wannan burin amma abin ya ƙi ci ya ƙi cinyewa hakan ya sa ita ta ɗauki tsana da kishin yarinyar ta saka a ranta tamkar dai ta manta da karamci da halaccin mahaifiyar ta lokacin tana raye ita kawai sai ita da ƴaƴanta ƴaƴa da babu rana bare watan haihuwar su don babu haihuwa ma a ranta yanzu.

Wani abu da ya fara kutso kai cikin lamarin zamanta da Ya ABDUL shi ne ƙaurace mata, ya fi son kasancewa shi kaɗai bayan ra san koyaushe muradin sa bai wuce ya gan shi tare da ita ba. Amma yanzu sai ya haura sama ya kulle ƙofa ta rasa mai yake idan ta tambaye shi sai ya ce hanyaniya ce ba ya so. Ta faɗawa HUSNA wannan ƙorafin amma sun kasa samo bakin zaren. Don haka sai ta ɗauki aniyar bin ƙwaƙƙwafin sa ko za ta gano dalilin sa don bata yarda da hujjar da ya bata ba ta cewa hayaniya ce ba ya so.

Da dare misalin ƙarfe sha ɗaya na dare ta gaji da zama ita kaɗai a ɗakin ta tana ta juyi so take bacci ya ɗauke ta amma ta kasa sai tunane-tunane take tana saƙa da warwara. Ƙafafun ta ta sako daga kan gadon tana hamma, sanye take da riga da wando na bacci kanta da hula mai net. Saman ta haura cikin sanɗa ta je ƙofar ɗakin nasa ta tsaya. Kunnen ta ta kara sai ta ji dirin magana. Mamaki ya kamata ta rasa da wa yake magana . Kunne ta kasa a nan ta gane waya yake.

"Ina son ki mana, ai ko duniya zan iya ɗaga babbar murya na faɗawa ina ƙaunar ki" Wani irin bugu ƙirjin HEEDAYA ya yi lokaci guda zufa ta jiƙata jikinnta ya ɗauki karkarwa ji da ganin ta ya ɗauke na sakanni. Ta kasa gaskata kunnuwan ta abin da suka jiye mata.

'Mace?' Ta jefawa kanta tambayar zuciyar ta tamkar ta huda ƙirjin ta ta fito.

"Yaushe na yi wannan sakacin Ya ABDUL yake wayar soyayya da mace na shiga uku ni kam" Ta faɗa a fili tana kama handle ɗin ƙofar ta murɗa amma sai ta ji a rufe. Ya ABDUL da yake waya da masoyiyar sa jin an taɓa ƙofa alamar za a shigo sai ya ce mata yana zuwa zai kira. Tasowa ya yi ya buɗe ƙofar maimakon ya girmama ta ko dai ya matsa ta shiga ɗakin sai ya kasa ya tsare. Mamaki al'ajabi suka cika mata zuciya.

"Kina buƙatar wani abu ne?" Ya tambaya a dake. Kallon sa take da idanun ta da suka kawo ruwa ta danne abin da take ji ta ce

"Na ji shiru ne kuma na kasa bacci shi ne na ce bari na taho nan"

"Ina buƙatar kasancewa ni kaɗai ba na buƙatar takura" Yana gama faɗar hakan ya rufe ƙofar. Idanun ta kamar za su faɗo a take ta ji komai ya sare mata lokaci guda ta tuna cewa Umma shekaran jiya ta ce mata ta ga ya shiga gidan su bayan ta san sai ta masa umarni yake zuwa gidan nasu to mai hakan ke nufi.

Ba wannan ne damuwar ta, soyayya yake da wata a waya? Da bibiyu take taka matakalar ƙasa ta dawo ta nufi ɗakin ta tana zuwa ta ɗauki wayar ta hannun ta har rawa yake ta kira HUSNA don ta san ita kaɗai za ta tattauna da matsalolin ta. Sau uku tana kira amma babu

amsa.

'Haba HUSNA ki ɗauka mana ki ji danuwar da ta kutso kai cikin gidana' Ta faɗa a zuciyar ta tana jin wani tashin hankalin yana baibaye zuciyar ta.

A karo na huɗu HUSNA ta ɗauka muryar ta cike da bacci ta ce

"HEEDAYA lafiya" Kuka HEEDAYA ta fashe da shi don ta kaaa furta komai.

"Haba aminiyata ya da kuka kuma ko mutuwa aka miki?"

"Yo ba gwara a mini mutuwa ba da bala'in da yake tunkaro ni"

"Subhanallahi mene ne damuwar"

"HUSNA Ya ABDUL ne na kama shi yana waya da mace, kin san ai na fala miki sauyin da ya fata shigo minj da shi cikin rayuwar auren mu to wallahi ɗazu cikin kunnuwana na ji yana furta kalmar so ga wata mace

"Innalillahi wa inna ilaihir raji'un wannan wace irin baƙar rana ce?" Ta faɗa hankali tashe tana tashi zaune daga kwanciyar da take.

"Shi ne da ya buɗe ƙofar ma wai ni HEEDAYA yake tambaya ina da buƙatar wani abu, sannan na taho ke ma na zo ina kiran ki kika ƙi ɗauka"

"Ayya!. Ki yi haƙuri bacci nake kin san gwauruwa da bata da miji a kusa da na yi isha'i sai na kwanta bacci baki ga yau ko chatting ba mu yi sosai ba tun wuri na sauk...

"Bar wannan labarin ƙanzon kuregen mene ne mafita wallahi kaina ya kulle na kasa kowane tunani ban taɓa tunanin ko hasashen akwai irin wannan ranar za ta riske ni ba"

"Ki bar wannan tada hankalin ƙaryar sa ya ce zai aure ta ai"

"Yo ko ba auren ta zai yi ba ni yin kalmar sa ta so ga wata mace ai bala'i ne me lasisi a wajena vana ƙaunar komai ya haɗa shi da kowace mace ki hatta ƴarsa ta cikin sa Little ɗin nan na tsane ta kishin ta nake wallahi dama ɓarin ta aka yi ko kuma a take da aka haife ta ta bi uwar ta...

"Ya isa haka HEEDAYA ƴar zumun naki, yarinyar da mahaifiyar ta ta so ki kamar mai to ko ba don mahaifiyar ta ba albarkacin uban ta bai kama ta kike faɗar wannan ba ai ba a kishi da ƴaƴa"

"Ke kike ganin haka ke ni kishina hatta uwar sa bai tsallake ba sai da na musu farraƙu ko yanzu ma ina da niyyar ƙara farraƙa su don na ji ƙishin-ƙishin yana zuwa gaishe ta" Kai HUSNA ta

gyara tana mamakin irin baƙin kishin HEEDAYA bayan maza kuma ba tabbas gare su a kan mace ba tun da har ta ji yana furucin so ga wata to tabbas sai dai addu'a dama da wuya namiji ya ƙaunaci mace ita kaɗai.

Sosai HEEDAYA take kukan baƙin ciki a cewar ta yau ba za ta iya bacci ba ita dai HUSNA ta bata baki daga ƙarshe suka yi sallama ranta yana suya idan ta tuna furucin da ta ji Ya ABDUL ya yi wa wata sai ta ji tamkar ta yi ƙaramar hauka.

Washe gari da safe da ta tashi ko kicin bata kalla ba dama duk saboda baƙin kishin ta ko masu taya ta aiki babu ta gwammace ta yi girkin ta da sauran ayyuka sai dai sauran na harabar gidan da ba fulawoyi ruwa maza su yi, sai sai renon Little RABEE ita kuwa ta haife ta ma ko yin jika da ita.

Ko da ya fito ko kallon arziƙi bai samu ba, shi ma kuma sai ya ɗaure fuska ko sallama bai mata ba tana jin lokacin da ya tafi ganin Little RABBE. Tana jin fitar motar sa ta fito ta saka direba ya ɗauke ta sai suka keta hazon shiga daji suna karo da ciyayi. Wurin bokan da MEEMA ta haɗa ta da shi ta je bayan ta kora masa jawabin abin da yake tafe da ita sai ya ce ta kwantar da hankalin ta ko da ya yi soyayya ba zai taɓa auren macen ba ai sun gama kama mata shi a hannu babu shi babu sha'awar wata ƴa mace sai ita!. Kalaman sun mata daɗi inda ya bata wani garin magani ya ce ta saka masa a miya. Kuɗi ta biya shi ta shiga mota direban ya ɗakko ta don har ya saba kawo ta wajen.

Daga nan gidan su ta wuce ta je ta korawa Umma jawabi. Zare idanu Umma ta yi tana ta ambaton bai isa ya buɗaɗa musu ƙasa a ido ba don HEEDAYA bata da kishiya a duniya!. Ita ma wurin nata bokan ta ce za ta nufa ya juyarwa da ABDULHAKEEM ɗin hankali a kan mace don ba za ta iya ganin wannan abin kunyar ba a jawo mata gori a wajen kishiya don har yau takun saƙa suke ita da Momma har ma Ammien don suna ganin sun mallake ABDULHAKEEM.

Kaf sai da HEEDAYA ta faɗawa HUSNA labarin zuwa wajen boka da kuma yadda ya faɗa mata, sannan ta ƙara faɗa mata maganin da ya bata da inda ya ce ta sakawa mijin nata a miyar abinci. Kwana biyu dai ta ga daidaituwar al'amura har ma wurin su Ammien ya daina zuwa wanna lamari ya mata daɗi hankalin ra ya kwanta tana ganin amfanin zuwa wajen bokaye da malamai.

Kwanci tashi asarar mai rai wata uku da yin haka a lokacin da duniya ta yi wa HEEDAYA da Umma daɗi suna ganin sun samu kan ABDULHAKEEM ashe dai basu sani ba lumbu-lumbu ya musu babu zato babu tsammani wani labarin mai kama da ya fi faɗar mutuwa ya riski Umma da HEEDAYA lamarin da ya sanya suka shiga mummunan tashin hankalin da suka kusa zaucewa musamman HEEDAYA da jin labarin ya sa ta zama kamar mahaukaciya. A ranar wata labara ne tana kwance tana danna waya ga yankaken apple mai sanyi a plate tana ɗauka tana ci Shigowar Ya ABDUL da sallama da wasu samari guda biyu suna biye da shi ɗauke da set guda

na akwati. Zaune ta tashi tana murmusawa tana jin daɗin yau kuma kyautar da za a mata kenan kasancewar ta saba da kyaututtukan da yake mata don ita ko lefen aure ma ba wani damuwa ta yi da shi ba amma wannan ya faranta ranta. Suna ajiyewa suka gaishe ta tare da fita fuskar ta cike da murmushi take musu sannu har da ɗaukan 5k ta basu wai sa sha lemo. Bayan sun mata godiya sun fita ta tashi tana wani fari da ido ta ƙarasa wajen sa gani ya zauna dafa kafaɗar sa ta yi tana aika masa wani sihirtaccen kallo mai cike da ma'anoni da dama na so da ƙauna.

"Yanzu wannan duk ni kaɗai?. Ina godiya a gare ka ba zan gushe ba ina ambaton na yi dacen miji ba har sai numfashina ya bar gangar jikina, ina ƙaunar ka Ya ABDUL ina faran har abada mu zauna mu kaɗai don ba na fatan ko a mafarki wata mace ta raɓar mini ko da takalmin sawarka ne bare kuma kai ɗin da kan ka...

"Wannan kayan faɗar kishiya ne, yau saura sati guda za a ɗaura mini aure" Kalaman sa suka yi gaggawar katse wa nata kalaman hanzari. Duhu ne dimm ya wulgawa ganin ta, cikin sakanni ganin nata ya dawo sai kuma falon ya shiga juyawa mata tamkar famka, kunnuwan ta suka yi dummm basa jin kowane sauti. Sororo take kallon sa da idanun ta da suka ƙanƙance saboda mamaki. Lokaci guda komai ya kwance a zabure ta tashi tsaye tana kallon akwatinan masu kalar ruwan goro da suke ta faman sheƙin sabunta, sannan ta waiwaya ta kalli Ya ABDUL da ya koma ya jingina bayan sa da jikin kujera yana kallon ta hankalin sa kwance kamar tsumma a randa!.
[2/19, 5:22 PM] MOM MASHKUR & AFRAH: BONONO

(RUFIN ƘOFA DA ƁARAWO)

NA

MAMAN AFRAH

First Class Writer's Asso.📝

*SADAUKARWA*

Daga farko har ƙarshe sadaukarwa ne ga MARYAM SANI HAFIZ (Merry tah) Alkairin Allah ya kai gare ki Allah lulluɓe rayuwar ki da tarin ni,imomi da albarkatu Allah raya mana Abdallah fatan alkairi.

Daga marubuciyar:

Ruɓaɓɓiyar igiya

Ƴan adaidaita sahu
Ungozoma
Ƴar zaman wanka
Ƙara'in inna delu
Beelal
Jalli joga
Da sauran su.
*09013181851*

PAGE 15

*MARYAMA*

Ta shiga tashin hankali sosai na jin furucin Ya HAFEEZ zai ɗauki abin da bai san nashi ba ne ya ce cikin sa bayan ko ita da cikin yake jikin ta bata san mai shi ba. Kaka sosai ta sha masa faɗa tana cewa ya bata mamaki ya yi abin da bata taɓa zato ba duk da dai tana kokwanton hakan amma ba a shedar ɗan yau. Tun daga ranar ta kafa musu karan tsana da shi da MARYAMA ta daina ba MARYAMA abinci sai dai shi ya dafa ya ba MARYAMAR. Idan zai tafi wajen aiki sai dai ya siyo mata komai na buƙata ta ajiye a ɗakin nata har da ƙaramin gas take girkin ta.

Duk da bata ji daɗi hakan ba kuma tana jin nauyin sa duk da ta yi yinƙurin sanar da Kaka cewa ba cikin sa ba ne amma ya ƙi ya bari. Ko da ya zaunar da ita ya tambaye ta amsa ɗaya ce dai ita ma bata san cikin waye ba amsa mai cike da ruɗani haka ya haƙura ya fawwalawa Allah komai. Tana so ta gudu amma babu hali don bata da wajen zuwa.

*BAYAN WATA BIYAR*

Haka ake rayuwar babu daɗi kuma babu yabo babu fallasa tsakanin ta da su Kaka har gwara Mero ma wani lokacin tana mata magana in ta ga Kaka bata wajen. Cikin ya tsufa sosai ga shi duk ta kumbura dakyar take tafiya ksancewar haihuwa ko yau ko gobe. Hankalin Ya HAFEEZ gabaɗaya a tashe yake bai san ya zai yi da abin da za ta haifa ba ga shi Kaka ta kafa sharaɗin tana haihuwa za a ɗaura musu aure su bar mata gida, duk da ita ma tana cike da tausayin su a ranta tana kuma shiga damuwa ganin HAFEEZUN ta ne yake da cikin ɗan shege wannan abu yana ɗaga mata hankali.

Yau ya kama alhamis da misalin ƙarfe goma na safe tana ɗaki zaune tana ta kuka abin

tausayi ita kanta bata san ya za ta yi da lan da za ta haifa ba ga shi ta zo ta raba mutumin da ya tainake ta da soyayyar Kakar sa sun dawo kamar aboka gaba. Kamar an ce ta ɗago ta gan shi tsaye a cikin ɗaki idanun sa sun tara ƙwalla. Tabbas ya san MARYAMA iya gaskiyar ta take faɗa sannan yana tausayin maraicin ta sannan ga soyayyar ta da take neman nakasta masa rayuwa. Kai ta sunkuyar ga wannan cikin nata da ya mata gingirigim. Daga ta ci abu sai ta ji babu sai ta sake cin wani abu wuni take tana ciye-ciye ga shi ɗan yake ta motsi.

"Ki saka hijabin ki zan kai ki asibiti a miki scanning domin sanin saura sati nawa ki haihu tun da Kaka basa nan dama shi ya sa na kasa fita da ke" Ya faɗa cikin sanyin muryar tausayin ta yana tsarga masa. Da to ta amsa dakyar ta dafa ƙasa ta miƙe tsaye ƙafafun ta duk a kumbure. Hijabin ta saka ta bi bayan sa a mota ta same shi, buɗe mata ya yi ta shiga mai gadi ya buɗe musu suka fita tare da haura wa saman titi.

A wani wajen scanning ya yi parking, ya buɗe mata tare da kamo hannun ta ya taimaka mata ta fito yana riƙe da hannun ta tana takawa dakyar suka shiga.

"Ma sha Allah ina taya ka murna madam ta kusa sauka ko?" Mai scanning ya ce yana murmusawa, murmushin yaƙe Ya HAFEEZ ya masa. Wurin suka shiga ta kwanta a kan gadon, shi kuma yana zaune a kujera ya kifa tagumi. Fara mata scanning ɗin ke da wuya abin cikin cikin nata ya bayyana a cikin computer daga mai scanning ɗin har Ya HAFEEZ a kiɗime suka tashi tsaye ganin abin da ya kusa tarwatsa musu kwanya wanda tun da suje a rayuwar su baay taɓa gani ba. Ita ma ganin sun tashi a kiɗimen ta ɗago idanun ta ta sauke a kan computer Idanu ta zaro cike da ruɗani wani irin tsoro tana baibaye mata zuciya sai kuwa ta fara karkarwa tare da haɗa haruffa ta ce

"Ya, Ya, Ya HAFEEEZZZZZZZZ"

*HEEDAYA*

"Mai kake faɗa ne wai Ya ABDUL ka san dai ko ana mini wasa a duniya ba na son wasan kishiya amma mai ya sa ka zaɓi mini shi a yau baka san za ka iya tarwatsa ƙwaƙwalwata ba?" Ta ce lokacin da ta ƙarasa gabansa don ta san tabbas! Sai dai in wasan yake mata amma ta san wannan ba iyayyiyar magana ba ce ko a mafarkin ta bare a zahiri. Kalaman sun yj tsauri da yawa.

"Ni sa'an wasan ki ne da zan miki wasa?" Ya jefa mata maganar cikin dakewar muryar sa babu ko alamar wasa ko sassauci a furucin sa sai ya koma mata Ya ABDUL ɗin na asali wanda ya canja mata bayan auren sa da Aunty RABEEYA. A hankali ta sulale ta durƙushe a kan gwiwoyin ta ta ɗora hannuwan ta a kan gwiwar ƙafar sa hawayen nan shaɓe-shaɓe kamar an ce mata Ummar ta ta mutu  cikin rawar murya ta ce

"Aure Ya ABDUL? Ni za ka yi wa kishiya?"

"Aure mana ba a auren ke aka aure ki? Ina so ki sani aure babu fashi, sannan ki sani haƙar ki bata cim ma ruwa ba domin kuwa ABDULHAKEEM ya daɗe da hango tubalin ginin da kika yi wa rayuwar sa shi ya sa ya nemar wa kansa mafita ni na fi ƙarfin juyawa a wajen ki HEEDAYA kar ki manta zaɓina RABEEYA ce wacce Allah ya karɓi abin sa amma ni kaina ba zan ce ga yadda aka yi na aure ki ba na san dai ni na yi furucin kuma ina tuna komai amma babu takamaiman dalilin. A yadda RABEEYA ta tafi ta barni tafiya ta bazata a shekaru ƙalilan ban tama kawo zan kalli wata mace da sunan so ba sai ga shi a watanni ƙalilan na yi aure auren na wai ke HEEDAYA?Abu bai tsaya a nan ba har kike rabani da uwata da ta yi silar wanzuwata a duniya ta sha wahala ta ta raine ni shin adalci ne wannan ke za ki so a raba ki da taki uwar? Ko so ne wannan ki kai ni hanyar shiga wuta tun da wofintar da iyaye ai hanyar wuta ce to ki sani ko don Abba ba zan saki ki ba amma kuma ni ma zan auro muradina sai ku zauna zaman kishi tare da ita wataƙila ita ta ƙaunaci jinina Little RABEE ta bata kulawar uwa wacce ta rasa a wajen ki kuma matsayin kina ƙanwar mahaifiyar ta ki ji tsoron Allah kuma ki sani shi ramin ƙarya ƙurarre ne" Yana gama faɗar hakan bai jira cewar ta ba ya tashi tare da janye hannuwan nata da take riƙowa tana roƙon sa don ta kasa furta komai sai zancen bebaye take hawayen nan kamar an buɗe famfo.

Bai saurare ta ba ya haura sama abin sa yana riƙe da mukullin motar sa. Bizigir ta yi a tsakiyar falon ta kwanta reran tana kuka tare da ambaton ta mutu ta lalace. Gabaɗaya duniyar take ji tana juyawa mata ta rasa makama da tunanin abin yi ta kwashe sama da minti ashirin tana kukan kafin ta tashi zaune ta fara jidar akwatinan tana jefa su kan benen. Ya ABDUL da ya watsa ruwa fitowar sa kenan bayan ya shirya ya ga kiran wayar masoyiyar sa yana shirin ɗauka ya fara jiyo ƙara abu hakan ya ankarar da shi wani abu yana faruwa da alama HEEDAYA ce take masa hauka shi kuma ba zai jura ba kuma ba zai ɗauka ba.

A fusace ya fito tamkar kumurcin zaki lokacin HEEDAYA ta ɗaga ƙaramin kit ɗin za ta yi jifa.

"Ba na son hauka HEEDAYA ki sani nan gidan ABDULHAKEEM ne ba turun mahauka ta, ki sani ba zan lallaɓa ki ba idan kin ga ba za ki iya ba hanya a buɗe take dama kara na miki saboda su Abba wallahi da a ce wata bare ce a yau sai na yanke igiyar aurena duka uku a kanta don ba matar zama ba ce za ta yi abin da kika yi" Yana faɗar hakan ya juya ya koma. Da ido ta bi shi har ta ɓacewa ganin ta jin maganar sakin da kuma cewa ƙofa a buɗe take sun razana ta. Tana ta mamakin yaushe Ya ABDUL ya zama haka ko dai aikin ta ne ta karye da wannan tunanin ta ajiye kit ɗin hannun ta ta tafi ɗaki tana zuwa ta ɗaga waya ta kira Umma ta zayya ne mata wannan ne abin da ya ruɗa su gabaɗaya.

Tun da ta kira HUSNA take rusa kuka gabaɗaya aun shiga tashin hankali suna jimantawa ita ma HUSNA kukan take taya ta tana mamakin ashe dai duk kanwar ja ce duk mazan haka suke.

"Ya zan yi HUSNA Ya ABDUL ya shammace ni, a lokacin da nake tsaka da sakin jikin ni kaɗai zai rayu da ni ashe dai ba haka ba ne ashe dai akwai wani ɓoyayyan shiri da yake a bayan fage, ashe dai da ya nuna mini ya daina kula kowace mace sannan boka ya tabbatar mini da cewa ba zai taɓa sha'awar aure ba an fitar masa shi a ransa ashe dai ƙarya bokan yake yi na shiga uku hankalina ya kai ƙololuwar tashi mafita kawai nake neman ko ta wane hali"

"To mai zai hana ki dage da addu'a ni ma in taya ki tun da aikin bokayen da malaman ba su ci ba?"

"Haba HUSNA kin san dai ana jinkirta karɓar addu'a ni kuma wuri ya ƙure mini tun da yau saura sati guda fa ya ce wannan wace iriyar baƙar ƙadsara ce da raba tsaka ta kunno kai" HEEDAYA ta faɗa cikin kukan da ya ƙi tsaya mata.

"To yanzu ya kike ganin za a yi ni ma wallahi kaina ya kulle na rasa mafita da a ce ina da iko ina da yadda zan yi da sai na dakatar da auren nan haba wace ce wanna mai rawar kan za ta shigo cikin gidan ki, da a ce ma za mu san wace ce da sai na zo mun je har gida mun tsoratar da ita don ta janye ƙudurin ta na auren sa" HUSNA ta kai maganar ranta yana ƙuna.

"Ai ni ban san ma wace ce ba da alama abin an yi shi ne a munafurce don Umma ma da na kira ta yanzu hankalin ta ya tashi don bata sani ba, ni na fi zaton wataƙila wannan ƙeƙashshshiyar uwar tasa ce za ta saka shi yin auren wataƙila ma ita ta sama masa matar ko ma ƴar gidan ƙawarta ce wa ya sani"

"Amma na yi mamaki bayan bokan ya ce miki ya makantar da ido da zuciyar ABDUL ɗin daga ganin duk wata ƴa  mace" HUSNA ta ce cike da jimantawa.

"Bari ke dai ina zuwa zan kira ki wallahi zuciyata zafi take ji nake tamkar na haɗiyi zuciya ba mutu ko na kashe kaina"

"Haba aminiyata musulma kike fa duk komai ya yi tsananj maganin sa Allah" Tsabar ma kuka ya ci ƙarfin ta kashe wayar ta yi.

Tana kwance tamkar matacciya ta rasa abin yi kamar an tsikare ta ta ɗauki waya ta kira MEEMA dakyar ta ɗauka bayan ta tsinke.

"Ya aka yi ne?" Ta jefawa HEEDAYA tambayar HEEDAYAR tana jiyo ƙaran taunar wani abu da alama wani abu take ci. Kunya ce ma ya kama HEEDAYA don sai ta rasa ma bakin magana gani ta daina kula MEEMA sai yau da komai ya caɓe.

"MEEME wai Ya ABDUL ne zai yi aure nan da sati ɗaya" Ta faɗa cikin muryar kuka.

"Ayyiriri" MEEMA ta saki guɗa sannan cikin nuna jin daɗi da bayyana farin ciki a muryar ta ta ce

"Ya mini daidai Allah sa nan gaba ya rufe ƙofa wato ya auri mata huɗu kin ga kishiyoyin ki uku"

"Haba MEEMA don Allah ki manta da komai ki tausaya mini zan zo gidan ki ki daure ki raka nj wani wajen bokan mai aiki sha yanzu magani yanzu ya mini aiki ko nawa zan biya don a janye maganar auren nan in ya tabbata mutuwa zan yi"

"Allah suturi buƙwai in ji kishiyar mai doro, ai ba mutuwa ba wallahi ko mushe za ki sai dai ki yi amma ni babu ni babu ke marar mutunci da bata san halacci ba. Da kin manta da halaccin da na miki har yau baku bani amsar saƙon da na tura miki ba saboda kin sake ƙawaye shi group ɗin MANYAN MATAN ma na ga ni na kai ki to ki ƙare ƙalau da sabbin ƙawayen naki" Tana gama faɗa ta kashe waya jifa ta yi da wayar a kan gadon ta kwanta ta rushe da kuka jim kaɗan ta ɗakko mayafi da jaka ko ta kan Ya ABDUL ɗin bata bi ba ta fita ta hau napep sai gida. Falon Abba ta nufa tana share hawaye Abba kuwa ganin ta ya san mai ya kawo ta amma sai ya nuna bai san mai yake tafe da ita ba. Kwashe komai ta yi ta faɗa masa a ganin ta zai dakatar da Ya ABDUL daga auren amma abin mamaki sai ta ji ya fara mata nasiha a kan ta rungumi ƙaddara ta zauna a ɗakin ta dama namiji mijin mace huɗu ne.

Ko cikin gidan bata shiga ba ganin haƙar ta bata cim ma ruwa ba a wajen Abba ta nufi gidan su Ya ABDUL ɗin ra kwashe komai ta faɗawa Daddy nan ya lallashe ta a kan ta yj haƙuri Abba ne a cikin maganar kuma Abba ne gaba da shi. Gidan Hajja ta wuce tana zuwa ta fashe da kuka ta shiga faɗa mata.

"HEEDAYA auren ne sunnar ma'aiki bakya so a raya? Ita uwar ki ita kaɗai take zaune a gidan ta ko kuwa tana da abokiyar zama? To ni ba na ciki da faɗan rashin gaskiya, babu wanda zan faɗawa a fasa aure ke da aka ce ƴar marainiyar nan ma baki bari ba HEEDAYA ko kin ɗauka duk ba mu san abin da yake faruwa ba? To ki sani yanzu kiwon mutum ake kiwo ba dabba ba" Kamar ta shaƙe Hajja haka ta ji nan ta baro gidan ta rasa ya za ta yi. Sannan babu ma wanda ya faɗa mata wace ce amaryar bare ta je ta ɗauki mataki.

Daga ita har Umma sun bi boka da Malam har sun gaji, sai kashe kuɗi suke amma babu biyan buƙata. Hajiya Aisha sai da ta raka ta wajen wasu manyan bokayen amma jiya i yau babu sauyi. Yanzu har ɗaurin aure ya rage kwana uku.

Part ɗin Ya ABDUL wanda ba a ƙarasa ba aka ƙarasa sai kuma ɗaya part ɗin da yake a rufe dama an gama shi. Shirye-shirye ake ta yi don Umma har gida ta je ta yi wa Ya ABDUL wankin babban bargo ta je ta yi wa Ammie da ko kallo ma bata ishi Ammien ba ta mayar da ita mahaukaciya.

Duk ta zabgr ta yi baƙi ta sa baƙin kishi a zuciyar ta, HUSNA ce kaɗai abokiyar shawarar ta duk wani shiri da take da shi a kan kishiyar take kwashe komai tana faɗa mata. Tun da dai sun yj jimami sun yi iya ƙoƙari ganin batun auren ya ruguje amma abin ya ci tura!.

"Wallahi HUSNA na ji babu daɗi ga shi yanzu ko kula ni ba ya yi, a tawa wautar so na yi gobara ta ƙone mu ni da shi ƙurmus mu mutu kin ga ban barshi a duniyar ba ma bare ya auri wata ko kuma mu yi hatsari mu...

"Haba HEEDAYA ki daina wannan tunanin, tun da dai har ta kusa shigowa ki mayar da hankali a kan zaman kishin da za ku yi kar ki bari ta zo ta ƙwace miki fada"

"Yo ƙwacewa ta nawa kuma, ni yanzu gaba ma nake masa ba na masa magana, sannan ma ni duk magungunan matan da nake sha waɗan da nake baki labarin yana santin su idan na yi amfani da su duk na tattara na ajiye kin san dai kaf sirrina ai na sanar da ke hatta magungunan mata da nake amfani da yadda nake amfani da wajen da nake siya da kuma yadda Ya ABDUL yake in ya kusance ni ai duk ina baki labari to mene ne ya yi saura wanda bana yi da zai mini kishiya"

"Ki ɗauki ƙaddara kawai kuma kin san dai wanda ya riga ka da kwana ya riga ka da tashi don haka ki  maida komai ba k" Katse HUSNA ta yi don in ana maganar kishiyar ma ƙunci take ji.

A yau ne aka ɗaura auren Ya ABDUL da amaryar sa, ranar da ta zama baƙar rana a wajen HEEDAYA babu wanda ta tara kuma babu abin da ta yi matsayin ta na uwar gida. HUSNA ce take kwantar mata da hankali tun ana gobe ɗaurin aure. Kuma yau da ake ɗaurin auren tun da safe HUSNA ta tafi wata ƴar uwar su HUSNA ta rasu suka tafi gidan makoki  ba su sake waya ba. Da la'asar lis HEEDAYA tana zaune bayan  RAUDA ta zo suna zaune kamar kurame abin duniya ya haɗe musu goma da ashirin don a ganin HEEDAYA abin kunya ne su yi gayyata ƙawaye za su rainata ita kuwa dama MEEMA bata zo ba. Sai Umma da take kiran ta a kai-a kai tana tambayar an kawo amaryar. Aunty Hafsa da ta zo da safe HEEDAYA ta mara rashin kunya wai ai da ita Ya ABDUL yake shawara amma saboda ta tsane ta bata bashi shawarar kar ya mata kishiya ba ita kuwa ta ɗauki ƴar ta Ikram da Little RABEE suka koma gida.

Zuwan Ihsan da Mubashshar tare da Na'eema ya yi daidai da shigowar motocin kawo amarya. Guɗa ce take tashi haɗe da bugun ƙirjin HEEDAYA. An wuce da amarta part ɗin ta da take a lulluɓe.

"Aunty HEEDAYA wallahi duk ƴan gayu ne baki gan su ba farare da su, amaryar tana lulluɓe da mayafi baki ga yadda aka mata ƙunshi mai bala'in k...

"Ya ishe ki Ihsan in zuzuta kyan kishiyata ne ya kawo ki ki ɗauki ƙafafun ki ki tafi" HEEDAYA ta faɗa a harzuƙe don kuwa ta cika fam. Sai wajen takwas da wani abu RAUDA ta tafj su kuma su Ihsan sai da tara ma ta gota.

Zaune take dirshan a ƙasan ɗakin tarasa mai yake mata daɗi. Ƙofar aka turo jikin ta ya bata shi ne. A fusace ta ɗago jin ƙamshin turaren sa ya gama haɗe ɗakin. Farar shadda ce a jikin sa an mata aikin baƙi sai farar hula mai ratsin baƙi. Fuskar sa a washe kamar gonar auduga.

"Uwar gida ran gida, uwar gida sarautar mata" Ya faɗa cike da daɗin baki bata tamka masa ba don tana buɗe bakin ta wataƙila zagi ne zai fito.

"Ni zan tafi sai da safe" Ya ce yana ajiye mata leda ɗaya da yake ledoji biyu ne a hannun nasa. Yana fita ta yi cilli da ledar kaza da lemukan, takaici yana cika ta ganin ita a nata ranar amarcin ko tattabara bai kawo ba amma yau za ta ci albarkacin kishiya!?.

Yadda ta ga safiya haka ta ga dare kuka kuwa har ta yi ta ƙoshi sai dai tana ta ƙudurtar sabon shiri don kuwa sai amaryar nan ta fita da ƙafafun ta don Ya ABDUL nata ne ita kaɗai.

Amarya da ango an yi kwanan farin ciki cike da farantawa juna, sun yi matuƙar murnar kasancewa da juna. Misalin ƙarfe tara suka sakko daga saman benen hannun su sarƙe da juna sanye suke da shadda baƙa sun yi anko kasancewar su farare sai ta mugun karɓi kikin su. Amarya kyakkyawa mai zubi da tsari na halitta ta sha ɗaurin ɗankwali gashin kanta da ta tufke jelar har har gadon bayan ta. Riƙe yake da ƙungunta bayan hannun nasa ɗaya yana sarƙe cikin nasa ji suke ba ya su a fagen masoya. HEEDAYA wacce baƙin kishi ya hana ta sakat ta baro part ɗin ta ta nufi part ɗin Ya ABDUL tun da yanzu ya koma nasa ya bar saman da yake a part ɗin ta. Zuciya da take ta mata saƙe saƙe ce a kan wai har tare bai fito ba sun raina mata hankali. Babu zato suka ga an banko ƙofar wacce Ya ABDUL da ya dawo daga masallacin asuba bai kulle ba. Da yake sun bata baya da ta shigo sai ta yi mutuwar rsaye ganin su sarƙe da hannu sannan yana maƙale da ƙugunta sai wani ƙamshin turarukan su mai sanyin ƙamshi da ya cika falon.

Wayar ta da take hannun ta wacce take ta faman kiran HUSNA tun jiya bata shiga, tana dab da shiga falon ta danna kiran HUSNA ashe dai kiran ya tafi kuma wayar tana ringin. Hakan ya yi daidai da fara ƙaran wata waya da take kan kujera can wajen da suke tsaye. Ya ABDUL ɗin ne kaɗai ya juyo fuskar sa ɗauke da murmushi. Ita kuma amarya bata juyo ba sai ta ƙarasa gaban kujera ta ɗauko wayar da take ƙara, lokacin kiran ya katse sannan da ta juyo ta taho bayan angon ya mata shamaki da ganin uwar gidan nata wacce bata taɓa gani ido da ido a sai a yau take sa ran ganin ta. Tana dab da ƙarasowa Ya ABDUL ya ɗan kauce sai kuwa amarya da idanun ta suke kan fuskar HEEDAYA da ta yi mutuwar tsaye riƙe da waya idanun ta suna kallon ƙasa da alama dai ganin su ya daki zuciyar ta kishi ya motsa. Taku ɗaya biyu amarya ta yi ta ɗaga hannunta ta ɗora a kafaɗar HEEDAYA da sauri HEEDAYA ta ɗago tana son ganin shin Ya ABDUL dafa ta ɗin da ya yi mai zai ce mata har yana da bakin magana? Amma sai ta samu saɓanin tunanin ta a kan fuskar da idanun ta ya sauka ta kusa samun taɓin hankali tsabar ruɗun da ya ziyarci ƙwƙwalwar ta. Sai dai tunanin ta ya ƙi tsayuwa wuri ɗaya saboda ta lura akwai

bambanci da fuskar da take zato sai dai kama ɗaya tamkar an tsaga kara wannan ta fi waccan haske kuma waccan tana da faɗin fuska sannan wannan fuskar ta doguwa ce.

"HEEDAYA!!!. Ki daina wahalar da kan ki wajen kirana a waya domin kuwa ga ni na dawo kusa da ke, kin ga wayar da kike kira a hannuna suna na HUSNA aminiyar ki ta online, ina so ki sani mu biyu iyayen mu suka haifa wato ƴan biyu kuma, ni ce Hassana ake kirana da HUSNA ita kuma Husaina. Da ni kike chatting da ni kike waya da ni kike komai amma ba ni kika gani ba ranar da kika ziyarce ni gidan ƙanwata Husaina kika je kuma da ita kuka haɗu ba da ni ba" Bakin HEEDAYA tamkar ƙofar gari haka yake a buɗe saboda mamakin da aka kashe ta da shi wanda tana tunanin tun da ta zo duniya ba a taɓa bata mamaki irin na yau ba.

Amarya taku ɗaya biyu ta yi ta ce

"Na kamu da son mijin ki ne tun lokacin da kike baje sirrin ki a faranti, kike kwashe komai kina faɗa mini, kin san zuciya bata da ƙashi sai na ji ina ma ni ce Allah ya ba ni'imar nan kullum cikin faɗa mini sirrin ki kike wanda ya dace da wanda bai kamata a ce kina faɗa ba har son da nake yi wa mijin ki ya linku bila adadin sai dai kash auren wani a kaina ya hana ni aiwatar da komai. Kwatsam wata rana na kama HAMEED ya kawo mini mace gida lokacin na tafi Kano ganin gida da yake mu ƴan asalin Kano ne to Husaina ta a Kano take aure ni kuma a Abuja. Ban sanar da shi dawowata ba da yake sai bayan na tafi ya zo Abujar sai a ranar na gane ashe manemin mata ne buƙatar sa yake biya a waje da matan banza shi ya sa yake hana ni nawa haƙƙin. A ranar na nemi saki da yake ba damuwa ya yi da ni ba a take ya sawwaƙe mini. A haka har na gama idda ke kuma kina nan kina baje mini sirrin ki wanda yake ƙara mini kwaɗayin son auren miji mai nagarta kamar ABDULHAKEEM. Kwasam kika ga na ɗora tallar wasu takalma na wata ƙawata a status kika ce kina so kika yi oder lambar da za ta karɓi kayan naki sai kika turo mini lambar mijin ki a nan na samu tsuntsu daga sama gasasshe.

Husaina ta da ita muke shirya komai don ganin na cika burina. Ashe dai faɗuwa ce ta zo daidai da zama shi ma kina bashi labarina ta haka ya kamu da sona ba tare da ya sanar miki ba. Ko da na kira shi na sanar da shi wace ce ni da ƙudurina na sanar da shi labarina sai ya amince da ni tare da nuna mini dama yana jin labarina a wajen ki daga nan muka ƙulla soyayya wacce ta kai mu ga aure kin ga yanzu sai mu ƙara ɗamarar zama aminan juna tun da gamu a ƙarƙashin inuwa ɗaya " Ta kai ƙarshen maganar tana kallon HEEDAYA da ta yi mutuwar tsaye hawayen nadama da da na sani suna zirya a kumatun ta.

'HUSNA, HUSNA, HUSNA kenan shuka nake a idon makwarwa? Ina kiwon ɗan damisa a matsayin mage? Ina ta famkamar kishi ina hangen kar wasu su shigo ashe dai na yi BONONO RUFIN KOFA DA ƁARAWO? ' HEEDAYA ta faɗi hakan a zuciyar ta ta ma kasa haɗa kalmomin da za ta yi magana da su wajen wannan gagarumar cin amanar da mijin ta da kuma wacce ta ɗauka aminiya suka mata!!!.

*LAST FREE PAGES MAI SON JIN YADDA ZA TA KAYA ZAI BIYA 500 A SAKA SHI A GROUP DON YA KARANTA HAR KARSHE IDAN NA KAMMALA CMPLT DOCMENT 700. ZA A BIYA TA ASUSUN FAIZA ABUBAKAR 9030283375 Opay ko FAIZA ABUBAKAR 9013181851 Palmpay shaidar biya ta 09013181851* K *ULLUM PAGE 2 IN SHA ALLAH KAFIN AZUMI ZA MU KAMMALA*

*SHIN MENE NE A CIKIN MARYAMA? SANNAN KUMA YA ZAMA ZAI KASANCE TSAKANIN UWAR GIDA HEEDAYA DA AMARYA HUSNA? KI BIYA KI KARANTA HANKALI KWANCE*

MAMAN AFRAH
09013181851